*💖💖👩🏻‍🦱ZEE BABY👩🏻‍🦱💖💖* *HATSABIBIYA* *RAMLAT RETURN*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

*Story & Written*
*By*
*Real Ladingo😉*

*Bismillahir Rahamanir* *Rahim*

*idan kina bukatar book dinan Akan nera dari ukku yake ki tuntubeni saman number nen zamu kashe magana +22796515805*

*Free Page 1&2*

Saudi ARabia cikin garin mekkah Misalin karfe ukku na dare ihu najiyo kida na tashi da gudu na nufi inda naji kidan ina cike da mamaki ah irin lokacinna lokacin da kowa ke bacci wasu kuma suna ibada domin nema kusanci da Allah sabahanu wata'alah to su awannan lokacin lokacin iya shegentane ko nace ita shegensu Dan duk mafi akasarin su Saudia yaran su da manyansu ba bacci sukeba sai anyi sallahr asubahi to Zee baby

haka take bata bacci cikin hadaddan parlon na shigo Wanda ya gaji da haduwa har na zarce zan nufi d'akin da kidan ke tashi naga wata kyakyawar balarabiya yar kmanin shekaru 35 year azaune da cazbi ahannuta tanaja ta hada kai da gwiwa tana magana muryata na Rawa tsayawa nayi domin naji me take cewa naji da harshen larabci tana cewa" Ya Rabbi ka dubeni ka yayemun damuwata Allah ka shiryamun Zaeenaba da wanne zanji da rashin mijina ko da rashin iyayena ko da rashin 'ya'yana maza har biyu mahaifina ya nuna musu yada zasu tsaneni an rabani dasu nazabi Zaeenaba akan komai munbar musu komai namu munbaru Jeddah mun dawo mekkah amma babu sauyi bakin mahaifina ya bini nima yata ta bijiremun Ashe haka bijirewa iyaye yake Dole zan dauki mata karya saka akasheta dole zatab bar
```

Saudiya tunda ta kamala secondary school gashi yau tacika gida da raye raye bata fice yawo ba har aje akasheta idanu na zaro nabar gurin na nufi d'akin da kida ke tashi ikon Allah nace yarinya na gani yar kimanin 17 year sai tikar rawa take tana juyi tamkar tarwada wani shegen wando mitsitsi bakinsa mazauninta rigar kuwa bata da maraba da breziya yaran duk bakar fatane su biyune kade larabawa duk da itama farinta bai kai na Jannat ba sai tafawa suke RAF RAF RAF suna zugata " Sai Zee,baby aikuwa ta Kara da gewa ta kwasar shoki idan ka kalleta balarabiya sak saide ta

dan sa dishi kadan Dole ma zakasan ruwa biyu ce saboda tsantsar kyauwon da Allah ya mata gashinta har gadon bayanta ta saka masa kalolin colour har kashi uku da ja da ruwan furfura da kuma bleu kunnenta dauko take da tila har biyar ajere tasa musa kananun barima na zinariya sun jeru Cas sunyi mata masifar kyawu hancinta ma atille yake tasaka yar karamar barima ta zinare kasan lebenta lebanta ma a tile yake shima yar barimar zinarece amanne agun Wanda hakan ya Kara kawata kyawon fuskarta duguwace masha Allahu kirjinta cike yake dam da albarkatun fulani akwaita cikar halitta duk da batada jiki ko kadan amma akwai mazauna kirata sak Coca-Cola sak

idanuta manya manya ne saide alumshe suke kana kallonta sai kazaci kaga kamar da gan take lumshesu amma ba haka abun yake ba halitta tace hakan kwayar idanunta tamkar iron ta turawa haka yake abinda ya Kara mata kyau kenan gashin idanunta gazar gazar ne tana da gashin gira mai kyau mutika tanada dogon hanci dan bakinta madedeci dan bai cika karamtaba ya dan bude kadan pink ne tamkar ta shafa Jan baki kalar pink zaka gani itako halitta tace haka wlh ajikinta babu makosa saide halayarta batajin magana ga rashin kunya da mugunta kamar me batada tsoro kuma bata barin ta kwana mutikar zaka Nuna mata rainin wayo to fah zata nuna maka ita tafika inko ka Nuna mata so to fah zata Nuna tafi kowa sonka kai ita duk da yada kazowa Zaeenaba to zata iya dakai wayarta da take hannu Jannat kawarta ta dauki ringing gunta ta zo ta janyeta tana mata magana da harshen larabci " habibty zee

majeed na kira fah daket ta cirota daga rawar da takeyi ta bata wayar tayi picking ta fito parlo Umminta na zaune jikinta ta kwanto tana wayar" hello Qalbi me ya hanaka zauwa haka mukayi da kai shiru yayi tsaki taja zata kashe kiran taji daga can yace " Zee babyna yau inama su Abbu magana tunda kin kammala karatunki suzo ayi magana Dan wlh inajin tsoron yada 'ya'yan hausawa ke kawo miki hari karki bijiremun tunda kince sunfi burgeki Akan mu kiss ta sakar masa ta wayar tana wani shegen murmishi " Qalbi na kasan ina Sonka fah to ya kukayi. Da su fashe mata yayi da kuka idanu ta zaro gabanta na faduwa badai shima an Hana ya aure taba" Qalbi garkameman kato da kai kake kuka Ify ta fada dariya nason kufce mata Dan rashin jarumtarsa tasa Sam baishiga zuciyartaba Dan ita tanason jarumin namiji mai cikar zati jajir tacce Wanda abinda za saka sa kuka to fah ba karami bane ba amma shi wai ko fada sukayi ta kirta masa rashin mutumci ya fara mata kuka kenan tsoki taja ranta ya bacci sosai cikin zafi zafi tace Qalbi wlh zan kashe wayar baki daya ayi

namiji ba juriya da jarumta haba ina Dan dalili haka kakeso muyi aure ina juyaka sai yada nayi

da kai ga shegen kukanka tsiya to ni idan namaka na shagwaba wa zai lallasheni tirr" Afuwan zee zeena Abbu ya hana yace kasheni zaiyi idan nasake maganarki wai ke yar macace wata uwar tsawa ta daka masa mai firgitarwa idanuta sun kada sunyi jajur kallo daya Raiyan ta mata ta dauke kai tanajin tsoron kar abunta ya motsa Dan bataji bata gani cikin bala'i tace masa " so wait Dan sunki aikin banza aikin wofi kaine abun tausayi ba niba lusarin Namiji kawai Dan kai kake fama da dafin so kai majeed ba Zaeenaba ba kuma ba nibace yar mace Abbunka ne Dan mace Dan uwarshi da Sauri ummi ta rufe mata baki kashe wayar. tayi tana turo baki ta rungume Raiyan wato mahaifiyarta idanuta wasu irin ruwan hawaye ke fitowa jajaye tamkar jini uwar tagani amma Dan karta lallabata abun yafi karfi sai cewa tayi " Zaeenaba abinda kikeyi ganinki yanada kyau Kenan duba kiga shigarki kuma dama nace kibar kula maza duk nawa

kikene gashi kinaja anawa mutane cin mutumci ? " ummi me nayi Dan buro ubansan zaicemun yar mace asali suka fimune ko mai za'a cemun haka mutuwa kan waye bata zuwa shi majeed din ba yaga yan uwan mahaifina ba duka duka watansa nawa da komawarsa kasarsu da ya kammala karatunsa waya baiga tsantsar kamarmu da wannan banzan gayan ba baki ta buge mata" kiyimun shiru ina rabaki da kaya kina shirin lada ganmo ko " to ummi majeed da kansa yake cewa ko makaho ya shafa yasan muna kama to mai nayi zaki dokeni? " ni dai ina son ki nutsu ki kama kanki kibar yawo don Allah da raye raye da rashin kunya ni kam Allah yana gani na baki tarbiyya yada uwa tagari takeba d'anta amma ke Al'amarinki sai gyaran Allah fatana ya shiryaki kalli kanki wacce yar mutumci zata maida gashin kanta haka?

" ummina dadin murnar gama makaranta ne fah kuma Dan uwarsu karsu bari ya aureni shegu yan iska ni shiyasa duk cikinsu babu Dan buro uban da na taba so har can cikin raina ta fada tana goge hawayen fuskarta da ya fara rikidewa ya zama jini jini " ummina kinsan Allah?

Baki ta rufo Mata "imun shiru Allah ya shiryeki Dole zan hadaki da mai gyara miki zama mik'ewa tayi tana zunbura baki tabar wajan duk da ranta abace bai hanaba ta koma gun su manal sukaci gaba da casu saida aka kira sallah asubahi suka kashe kidan Ana wasu suka zube Dan sunyi taune taunesu ko sallah

basuyiba sai bacci amma zee da Jannat saida sukayi sallah suka kwanta don duk iskancin to fah bata wasa da sallah tanajin majeed na kiranta taja tsaki tana harara wayar takin dauka har bacci ya kwashe da kudirin idan suntafi gidansu Jannat baza dawo gidaba sai tayi sati Raiyan tana gama sallah ta kwanta da kudirinta aranta na fitar da zee daga kasar baki daya ko Allah yasa ta shiryu acan Dan tasan anan Dole mahaifinta na farautar ran zee gwara tayi nesa da kasar tasan tabbas za'abata kulawa a can

*Nigeria* da misalin karfe goma na safe azaune na hango wani hadadan gaye Dan kimanin 28 year cikin wani makeken Office Wanda ya gaji da haduwa waya ce manne

akunnesa yana magana cikin nutsuwa sai lumshe mayatattun idanuwansa yake lumshewa ya tura hannusa cikin kwantacciyar sumar kansa yana shafawa sai sheki take tamkar ta larabawa kana kallonsa kasan soyayya yake zubawa farine dogo ingarma namiji jajirtace yanada faffadan

kirji fuskarshi ta kawatu da saje Wanda yayi masa masifar kyau yanada manyan idanu lumsassu tamkar yanajin bacci haka suke yanada dogon hanci dimple dinsa har har biyu sun loba sosai Wanda hakan ya Kara masa kyawu na musamman dugone mai sufar karfafa kai da ganin yanayinsa baya daukar wargi ko raini,

nocking kofar akayi ga wayoyi har biyu na ruri yaki ko kallonsu kiran ya tsinke ya bada izinin ashigowa kofar ta murda ta shigo da sallama fuskarsa babu wal wal ya

amsa ta risina cikin bashi girmansa Nurse din tace" Doctor an gama shirya komai kai ake jira ka Shiga tiyata? cikin dadadar muryasa tamkar baya son magana yace "OK ganinan ficewa tayi yai picking din wayar da an kira yafi so goma ya Kara akunnesa shiru ba ayi magana ba gani lokaci na kuremasa ya tsinke kiran ya kashe wayoyinsa ya ajiyesu ya core wani tsadadan agogo ya ajiye ya Mike cikin wani taku na isa da kasaita ya ke takunsa yana bude akofa yaci Karo da yayansa Mahabeer fuskarsa dauke da murmushi yace" haba Dr Sardauna tun yaushe ummi Raiyan ke kiranka baka dagawa wlh itace ta tasuni da kira ina aikina nazo Hospital naga ko Ify baka daukan kiranta kansa, ya dafe " oh my God wlh my brother abubuwa sun Mun yawa yanzuma tiyata zan shiga ai mun kashe magana da ita ni ba nida dama kaine zaka tafi Dan ta gama shirya komai yada za'a fito da fitsararar yarinyar nan Dan wlh bazan jeba inada abun yi wannan aikin sai kai bantashi kamuwa da ciwon zuciyaba shine daddy yayi fushi wai ai nafi ka sanin garin nade

lallabashi nace ga babba murmushi mahabeer yayi Dan dama yafiso yaje ayi abin karamci" ai nasani tace wai akwai maganar da zakuyi " OK kace zan kirata idan na fito  da Sauri ya wuce cikin kuzarinsa yayi d'akin tiyatar mahabeer ya juya fuskarsa dauke da murmushi Dan yasan halin rikitattan kanan Nasa tunda yace bazai jeba to fah bazai jeba Dan baya ra'ayin zauwar yarinyar Sam yana fita ya shiga motar yaja ya nufi can gidansu yaji ya za'ayi don yasan Tabbas Dr Sardauna bazai jeba kai ya girgiza yana driving dinsa cikin nutsuwa kida na tashi kadan kadan cikin motar ya dauki hanyar gidansu yaji abinda Daddy da  zai yanke gama da tafiyarsa saudiyar, kamar yada Dr Sardauna yace din...

Sai kunji next page insha Allah

*Karku manta kudin* *wannan book nera dari* *ukku ne kacal zakusha* *karatu maicike da* *abubuwa daban daban*
*na rayuwar duniya ga me bukata ya tuntubeni awannan number my kashe magana Yanda* *zaki sambadi karatunki* *akan dari ukku kacal*🤸🏻‍♀️
👇🏻
*+22796515805*

Rahma ce ummu Fareesa🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️

*💖💖👩🏻‍🦱ZEE BABY👩🏻‍🦱💖💖* *HATSABIBIYA* *RAMLAT RETURN*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

*Story & Written*
*By*
*Real Ladingo😉*

*DEDICATED TO*
My momy Aisha Alto😘

*Bismillahir Rahamanir* *Rahim*

*idan kina bukatar book dinan Akan nera dari ukku yake ki tuntubeni saman number nen zamu kashe magana +22796515805*

*Free Page 2*

....unguwar *kofar marusa lowcos* naga ya nufa wani makeken get naga Mahabeer yatsaya yana honr aka wamgame masa get din ya shige Ana harabar gidan yayi parking saboda gagawa yake ya koma gun aiki ya fito yana nufi cikin gidin taku yake cikin nutsuwa da kamala sai lokacin naga haduwarsa yanada tsayi amma ba sosai ba Dr Sardauna yafishi tsayi da murdadan jiki shi Mahabeer bashida jiki amma ba shida Rama sosai yanada hanci da idanu ma dedeta amma ba fari bane kuma ba baki bane tsaka tsakiyane farinsa yana da yalwar gashi kai da ta idanuwa agaskiya Mahabeer kyakyawane duk bai kai Dr Sardauna amma idan Dr baya kusansa zaka zaci shidin samun na biyunsa zai wuya cikin maza sai de fah idan Dr Sardauna na kusansa to fah sosai zakaga makusasa shi mutum ne mai sanyin hali da saukin kai yanada yawan fara'a da son jama'a bai fiye daukan zafiba sabani
```

Dr Sardauna uban bakar zuciya da tsama Sam bai fiye shiga abinda ba shafesaba amma fah yanada karamci baya raina na sama dashi kuma shima na kasa dashi yayi kadan ya kawo masa wargi shiyasa gidansu yara ke tsoransa dan baya musu ta dadi shiyasa kowa yafi maida hankalinsa wajan Mahabeer saboda faram faram d'insa da mutane
Kofar parlon ya murda ya shigo da sallama ghaisha na zaune tana waya wata kyakyawar budurwace yar kimanin 22 year tana kwance kan cinyarta sai dariya hira da ghaisha takeyi take sallamar khalisat ta amsa cikin sanyinta cike da kunya kusanta ya zauna " my bro sannu? " yauwa yace khalisat ykk? " Alhmdllh my bro bai sake magana ba har

"ghaisha ta gama ta kalleshi tana murmushi" ghaisha mu ina daddy? dukansa tayi" ba kasan da tafiyasa daura ba to ai suntafi basu wuce awa dayaba da tafiya amma meye na nemansa kuna gida daya?" ghaisha kinga fah ummi Raiyan ta matsa kan tafiyar nan? murmushi tayi ta dafa kafadarshi" to ai daddynku ya gama magana kaine zaka tafi jibi ya war haka kana saudiya bari ya dawo zuwa yamma uban yan rigima tunda yace baya zuwa ai Daddynku ya barshi murmushi yayi ya Mike " to Nina koma sai na dawo Aunty amaryace ta fito tana rike da hannu Nanah sai rigima take mata " ah Mahabeer daga ina warhaka? murmushi yayi yaje ya dauki Nanah "baby rigima yi shiru mom wlh kan tafiyar ne bari na dawo dai zamuyi hira murmushi tayi" to sai ka. dawo saida ya lallaba Nanah tayi shiru ya ajiyeta ya dukowa yai ma ghaisha kiss " ghaishamu sai yamma dariya suka masa har khalisat ficewa yayi yana girgiza kai Aunty Amarya ta iso ta zauna ta kalli khalisat ta doketa abaya " wlh ke baki rabo da da son jiki sai kace mage murmushi tai ta Kara shigewa jikin ghaisha " ah to ina ruwanki kujini da Mariya babyn daddy kukan me kikeyi " hmmm kibarta kawai wai sai mun fita dariya ghaisha tayi suna hira cike da kaunar juna,

Misalin karfe ukku na yamma zaune yake cikin Office dinsa sai juye yake sama wata lumtsumemiyar kujera yana waya da harshan larabci cikin nutsuwa da girmamawa yake mata magana" ummi babu damuwa zan saka mata idanu sosai insha Allah rashin jinta acan zata baroshi saboda akwai maganinta anan kin san gyarata Dole zan jajirce naga ta dawo saiti insha Allah kuma kirika hakuri karki saka damuwa aranki har ciwo ya kamaki ko me tace masa oho naga yayi murmushi yana Sosa sumar kansa " ummi mashakurah ta kusa zuwa nan da kwana ukku take isowa daga London Amin ummina eh jibi zai taso ta kasance cikin shiri OK idan na koma gida zan kiraku bye tisnke kiran yayi yana ciza jajayan lips d'insa yana juyi kan kujera sigari ya kunna yana bata hayaki baki da hanci idanusa sun kada sunyi jajir tamkar an masa wani Abun Bacin Rai dan sam ya tsani zancen zuwan yar Agullar yarinyanan kasarsu dan babu yada zaiyine ya hana wlh da ya hana shi ganinsa tarbiyya zata batawa yaran gidansu tsaki yaja knocking din kofar akayi

Ya bada izinin shigowa da sallama ya shigo sallama ya amsa yana zabga masa harara " Dr Sardauna nawa nida Mashakurah menayi haba Abokin kwarai tsaki yaja " wlh Ahmed kafiya rainin hankali kewayowa yayi ya rungumesa yana dariya" to Afuwan Dr bazan sakeba" dallah malama sakeni duk ka shekeni sakinsa yayi ya zauna kujera da take fuskantarsa" ya babymu ta taso hararasa yayi yana busa sigarinsa hanci ya toshe " to ka fita mana har na gama sha dan bazan fasaba? " to nace ya akayi mashakurah bata zoba dama karya kakeyi" harara ya zabga masa " akan me zanyi karya wlh sweet baby ta sami yar matsala ciwon cikin ya tisamun ita sai

nan da 3,days zata taho ni nace ta bari har ta warke itama sai kuka take mun tin safe ina lallaba abata har ta hakura dariya Ahmed yayi zaiyi magana na'uran manne a bango ta dau ruri agigice Dr Sardauna ya Mike yana cillar da sigarin hannusa ya fito da gudu cikin kuzarinsa  Ahmed ya dauki sigarin ya kasheta yayi zaune dan bazai bar masa Office ba kowa ba  yana fita yaci karo da nurse zasu kiransa da azama suka karasa, d'akin Dr haladu ne tsaye kan matar Dr Sardauna na shigowa ya matsa ya shiga aikinsa, cikin 30 minute ya samu numfashinta ya fara aiki dede Hamdala yayi yau akalla kwanata ukku bata motsi fitowa yayi 'ya'yanta na tsaye suka taresu yayi musu bayanin komai sosai sukayi farin cikin suna samasa, Albarka tare da godiyar Allah wata yar matashiyar budurwa dan dadi batasan lokacin da ta fada, jikinsa Dr Sardauna ta rumgumeshi tana kukan farin cikin ba cikin jin haushin da bakar zuciyarsa ya hankada ta yana jan tsaki ya nufi Offiice d'insa yana harara yarinyar yayunta  sunji dadin yada Dr ya mata suka hau mata fada haushi ya cika ta bar musu gurin yana zuwa Office toilet ya shiga yana wanke hannuwansa yana jan tsaki dan ya tsani rashin tarbiyya sam ya tsani mace marar kamun kai ko da ya fito dariya Ahmed yake masa ganin yada yake cicin magani yana cizon lips d'insa banza yamasa ya zauna ya kunna sigari ya fuskacin Ahmed yana masa magana amma banji me yake ce masa ba amma da alama mai mahimmanci ce...

✨🌟✨🌟✨🌟✨🌟✨🌟✨🌟

*Saudi Arabia*  karfe biyu na dare ummi Raiyan ce zaune saman Dadduma tana tana gayama Allah kukanta hankalinta atashe Zee baby yau kwana ukku Kenan taki dawowo gida tunda taji labarin an gama mata shirin zuwa Nigeria bata gidansu Jannat bata gidansu manal gashi Mahabeer ya ISO yana Jeddah sai gobe zai shigo motar kasuwa ya shigo mekkah yanzu ya zatayi idan bataga Zaeenaba ba bata rumtsaba sai bayan sallah Asubah tana tayiwa yarta Addu'ar shiriya tana tunanin hakkin iyayanta ne da ta bijire musu abaya shine yarta ke bata wahala amma ita bazata iya yiwa yarta mafi soyuwa aranta bakiba sai de Adu'a itace mafita tasan Tabbas ta koma Nigeria dangin mahafinta bazasu barta taci gaba da wannan rayuwa ba babu abinda ya ke damunta sai kananun shaye shayen da takeyi da ta tuno waye Sardauna tabbas zataci ubanta idan ta musu iya shege zai saitata sai taji dan dadi a ranta har bacci ya saceta,  da misalin karfe daya na rana

kwance take saman wani makeken gado tana sharara bacci hankalinta kwance daga ita sai wata guntuwar Riga gabaki daya halitar jikinta mai cike da kyakyawar surah da Jan hankalin duk wani lafiyayan namiji ta baiyana rabin manya manyan breast d'inta duk awaje tsaye suke kam jajir dasu harta kan nipple din ana gani duk awaje shigowa yayi da niyar tashinta tayi sallah Azuhur lokaci ya wuce amma ganin yanayin da take komai bata abaiyane dan bata taba zaton zai shigo d'akinba dan ta murza key gaba daya jikinsa ya dauki rawa idanusa ya rufe burinsa kawai ya rungumeta ya tsotseta ya manta wacece Zee baby saman bed d'in ya fado ya rumgumota ya fara murza kirjinta yana koqarin had'e bakinsu ta bude idanu bakinta dauke da kallamar shahada, ta ingijeshi amma ina karfinsu ba dayaba idanu maharaz ya rufe yada yakeji bazai iya barintaba sai ya cinma burinsa duk da zee batada tsoro yau ta Sare da Al'amarin

maharaz cizon sa take tana yagonsa amma idanuta akekashe babu Alamar zatayi kuka duk da ta gama tsorata mutika idan ka tsaga jikinta babu jini gata babu abinda tafi shawa irin a tsotsi nonota ko irika murzasu duk da babu

Wanda ya taba mata hakan amma tana mutikar kaunar hakan to yanzu hakane maharaz yake mata jin ta fara shiga yanayin da tabbas idan bata dauki mataki ba to fah zaiyi galaba akanta jin yana neman tura hannusa, kasanta taji idanuta yacika da kwalla, jikinta ya dauki kerrrma babu bata lokaci tayi kamar zata tayasa, iskancin da yake shirin mata hannuta ta tura cikin wandonsa ihu ya saki azatonsa banana zata murzamasa har kara ware mata kafa yakeyi😆😝 amma sai kawai ta saka masa wata jibgegiyar kunama bakikirin da ita aikuwa babu bata lokaci ta harbeshi a 'ya'yan marena😅 habawa sai kawai ya saketa tanagani ya saketa yana ihu fitsari na zubowa ta diro daga saman bed d'in batabi ba ta kansa ba ta warci Abbayar ta ta saka ta saka nikaf ta saka takalmi ta dauki wayarta da Jakarta tai maza ta fice daga d'akin parlo ta isko abokansa biyu amma basu gane ko wacece saboda ba'a ganin kominta sai idanuta ihun da sukajine yasa sukayi d'akin itako ta zuba aguje tayi waje sauri sauri take tafiya har ta fito bakin titi cikin sa'a ta sami limozyn ta shiga cikin sa'a khaleedia d'in zata, cikin motar sai surutu akeyi haushi ya cika kamar taci ubansu sai dura musu zagi take k'asa k'asa kuma wasu sunji amma babu Wanda ya kulata itakuwa taso wata ta tanka mata ta huce haushinta amma babu wacce ta kulata ganin balarabiyace karta jamusu shairri

ana zuwa dede inda zata sauka tayi magana taciro miah daya ta basu ko canjin bata tsaya amsaba ta fice ta tsalaka titi ta nufi gidansu Wanda ba haka tasoba dan tasan duk inda taje idan ba gidan maharaz bane to fah sai ummi Raiyan tasa an samota to gashi Wanda ta yada dashi fiye da kowa cikin 'ya'yan hausawa yau yana shirin karya mata haki a idanu sai tsine masa Albarka take cikin ranta amma da ta tuna ta'asar da tamasa sai taji dadi tasan gaba sai yaji tsoron yima kowace mace hakan dan bai taba nuna mata hakan ba shiyasa ta yarda dashi ta tsani mazinaci tana isowa kofar gidansu majeed na isowa kofar gidansu awata maiyar mota da sauri ya fito yana kiranta ko kallonsa batayi ba key ta ciro cikin jaka ta bude gidan wuff ta shiga da sauri ta rufo kofar da karfi key ya shiga da kansa mai aiki taga tana wankin gida tana gaisheta hannu ta daga mata ta shiga da taso tace mata karta tube kayanta akwai baki to gani taki mata magana kuma sanin halinta yasa

ta bari tin da ta ga bata cireba tun kan ta Iso cikin parlon ta cire Abbayar ta ISO daga ita sai wannan shegiyar rigar dan tasan babu Wanda zai shigo musu parlo da sallama ta shigo Mahabeer ne zaune an cika masa gabansa da kayan ciye ciye suna magana da ummi Raiyan ya juyo yana amsa sallamar miyau din bakinsa ne ya kame ganin Zee baby a haka gabaki daya ya rasa nutsuwarsa saboda shi mutumne mai karfin shawa itako ko ajikinta da gudu ta nufo gunsa, ta danne bacin ranta dan ita mutum ce wacce duk bakin cikin da take cikin idan bataso nunawaba to fah karyar mutum ya ganota tana dariya tayi kansa idanu ummi Raiyan tazaro ta dora hannu akai sai cewa takeyi "Ya Rabbi Ya Rabbi Ya Rabbi su manal idanuwa suka zaro suma sun cika da kunya itako ko a jikinta tayo kansa tana fadin" marhababuka Ya Ahukhuya ganin zata kunne masa wutar da bazai iya kashewa ba jikinsa na rawa ya Mike tsaye ya nemi gurin tsira har wata irin zufa yake agoshinsa amma kafin yasan abunyi tuni ta fada saman

kirjinsa ta bire samansa kamar biranya ta rumgumesa tana dariya... Ba mahabeer uban gayya ba Jamal kansa da yayo jagora ya rakoshi tun daga Jeddah zuface ke keto masa dan jiyake tamkar shi aka rumguma wandonsa sai motsi yakeyi😆 ummi Raiyan idanu ta rufe tana Kiran Sunayen Allah, da mamakin dawowarta gida kai tsaye da tsakiyar rana don saninta duk inda zata tofah bata fita da rana kuma haka zalika bata dawowa gida da rana  Mahabeer kuwa suman tsaye yai yada kirjinta ya tokareshi ga shafar wuyasa da take tana masa kiss tana dariya ta tsareshi da shanyanyen idanunta tanaso yayi mata magana shiko sai Kiran Sunayen Allah yake ya bashi juriya jarumtarsa ya tattaro......✍🏻

🤸🏻‍♀️Sai kunji next page insha Allah

*Karku manta kudin* *wannan book nera dari* *ukku ne kacal zakusha* *karatu maicike da* *abubuwa daban daban*
*na rayuwar duniya da wata irin rikitacciyar soyayya mai zafin gaske ga me bukata ya tuntubeni awannan number mu kashe magana Yanda* *zaki sambadi karatunki* *akan dari ukku kacal*🤸🏻‍♀️
👇🏻
*+22796515805*

Rahma ce ummu Fareesa🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️

*💖💖👩🏻‍🦱ZEE BABY👩🏻‍🦱💖💖* *HATSABIBIYA* *RAMLAT RETURN*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

*Story & Written*
*By*
*Real Ladingo😉*

*Bismillahir Rahamanir* *Rahim*
```

*idan kina bukatar book dinan Akan nera dari ukku yake ki tuntubeni saman number nen zamu kashe magana😉 +22796515805*

*Free Page 3*

....nutsuwa ya sakama kansa ya qaqaro murmushi yana kallonta ya janyeta daga jikinsa ya kama hannuta suka nufi inda ta yasar da Abbayar ya sunkuya ya dauka haka kawai yakejin ciwon kallon da Jamal yake mata saka mata Abbayar yai suka dawo saman kujere. kusansa ta zauna tana murmushi zata kwanta jikinsa ya kiya ya kalleta da harshan turanci yace" kanwata ykk ina kika shiga har tsawon kwana biyu? hannusa ta rike ta fara magana da Hausarta babu wani kwarewa " Ahukhuya banason Nigeria na gudu gidan abokina Maharaz ya boyeni kwana biyu yana bani kulawa yanzu ina cikin bacci Dan buro ubansa yazo yana matsani niko na saka masa kunama adiyan kaya na gudo gida ta fada tana wata irin dariya idanuwanta sun kade sunyi jajir alamar bata huceba kunyace ta kamasu ya kalli hannusa da ta rike tana murzawa tana dariya kamar zarara aransa yace ya Allah ka rabanin da wannan shawa Dan naga wannan

Ko munje ba daina tabani zatayi ba naga tabi'artace taba jikin mutum batare da ta kawo komai araiba sakinsa tayi ta Mike ta nufin gun Raiyan ta fada jikinta tana mata magana da larabci tana sakar mata kiss"ummina nayi missing dinki? ta rumgumeta gam tana kukan shagwaba ajiyar zuciya ta sabke tana buga bayanta Alamar lallashi fada ta Shiga mata da nasiya ta lallabata har tayi shiru dagowa tayi ta kalli manal ta harareta" ke Dan uwarki shine zaki wani zo gidanmu ai kinsan bananan salon ku tadawa ummina hankali? dariya manal tayi tana kallon jannat" habibty ummi taje ta dauko mu fah kallin jannat tayi ta mata magana da idanu ta mayar mata mik'ewa tayi daga jikinta " kuzo muje ciki banyi sallah Azuhur ba tashi sukayi suka bita Mahabeer sosai yakejin sonta cikin ransa kai tsaye tin lokacin da ta rumgumeshi kallon ummi yai

ya fuskan ceta suna magana Jamal ko har yanzu wandonsa baibar motsiba ummi Raiyan tace" Mahabeer ba fah lako lako zakuyi mataba Dole sai kun zage kun zazare mata to bare kai da take ra'ayinka Akan Al'mahadee wato Dr Sardauna don haka ka sa mata idanu sosai don Allah kusa ta dawo cikakiyar mutum ina so naga zaeenaba ta nutsu tazama kamilar mace tayi nisa dani ko hankalina ya kwanta ko iyayena zasu yafemun tunda sun nuna itace basu kauna sunfi son abokan haihuwarta mazan biyu sun rabani dasu sunsaka 'ya'yan cikina sun gujeni sun tsaneni ni da Zaeenaba saboda ta nuna kauna gareni wlh ina sonta bana son rabuwa da ita amma Dole zan hakura saboda hankalina zai fi kwanciya inaji tsoron ya saka akasheta ta fadi tana goge hawaye Dan tasan tabbas Zee taga kukanta akwai bala'i ajiyar zuciya ya sabke cike da tausayinta " ummi Raiyan kiyi hakuri

Insha Allahu zata nutsu kuma zaku shirya da mahaifanki wlh Dole yaranki zasu nemeki koba bajima yanzu ma hankaline bai gama ratsasu ba shekara sha bakwai ne fah suke ciki to cikin su Zaeenaba tafisu wayo ita da take mace ajiyar zuciya ta sabke " to da fatan zaka yimun koda wata daya kafin ku tafi? idanu ya zaro ummi wlh bakin kwana ukku zanyi mukoma aiki sunmun

yawa bakiga shi Al'mahadee da bashida dama Dole nine nazo murmushi tayi " to Allah ya kaiku Ify ya kuma hada fuskokinmu da Alkhairi? " Ameen ummi suna cikin hira akayi kiran sallah la'asar suka Mike sukaje sukayo Alwalla suka tafi masallacin da yake manne kusa da gidan ummi ta Mike ta shiga tayi sallah zuciyarta babu

Dadi batason rabuwa da yar tata amma da ta tuna rashin jinta gashi batasan me zai faru a gaba ba Dan rashin jin. Yar tata sai ahankali gashi tana Addu'a ba dare ba rana amma baby wani sauyi Zee baby ko suna shiga ta tube kayan jikinta tana rawa da juyi sai ihu takeyi tana dariya daga ita sai shegiyar rigar nan manal tace" my habibty wlh iskanciki gaba yakeyi fah fasa rawar tayi wata shegiyar tsayuwa akarkace tana kallonta shekeke tana murmushi " bari nayi bautar Allah na gama zanci durin uwarki la'ada waje yasin bathroom ta shige jannat ta kalli manal " wlh duk kece kika koya mata Hausa da zage zage gashinan akanki take sabkesu wlh dazu naji kunyar abun da ta fadi gaban baki? dariya manal tayi" naji amma shaye shaye wa ya koya mata Dan kaniyar mai da famiki shurba daga cikin toilet ta lailayo zagi ta dirka musu ta ciko Dan bokiti da ruwa ta bude kofar ta watso musu " sheguna ina jinku fah ta koma taci gaba da wankata ta dauro Alwalla ta fito tabude wardrobe dinta ta bude ta ciro Abbaya ta saka ta nade kanta da mayafin ta shimfida dadduma tayar da sallahr Azuhur, suko kayansu sukacire suka canza da nata suna mata Allah ya isa azuciya tana idarwa taji kiran la'asar ta tashi ta tayar suma Alwalla suka dauro sukayi sallah tana gamawa ta ci uwar kwalliya tasaka wata atamfa bakace mai ratsin  fari dinki Riga da siket manal ce me musu dinki tare su ukku kullum to jannat ba'a barinta tana sawa agidansu saide idan ta fito gashinta ta sarce  ta daureshi tayi masifar kyau kamar ka saceta sai dai dinkin ya fito da surata yan mazaunanta masu daukar hankali sai motsi suke tana kadasu gangan tana musu gwalo manal tace " dallah can figigiyar banza nacemiki ki faso gari kizama yar duma duma A dama dake kullum ke kamar kinashan ruwan zafi ta fesa turare

ta kallesu " wlh manal danayi jiki gwara daga haka nakara tsotsewa Dan uwarki ko ba jiki akwai kayan aiki ta juyo mata yan mazaunanta masu qira coca cola tana fito da harshe waje tana kadawa ihu suka saka " ku tashi muje parlo ku gaishe da Dan uwana kuma wlh sai kun duka har k'asa fitowa sukayi suna dariya gun mahabeer suka nufa ta zauna kusansa suko suka duka suna masa sannu da zuwa cikin fara'a ya amsa yace" ko zaku bimu Nigeria ne kai suka girgiza suna dariya Zee ta jinginu da jikin Mahabeer ashagwab'e tace" Ahukhuya nima bana zuwa fah ta Kara shigewa jikinsa tana turo baki aransa Adu'a yakeyi Allah yakawo masa dauki son yarinyar yamasa mugun kamu ga wata muguwar shawarta da yakeji janyeta yayi yana murmushin karfin hali " kanwata kiyi hakuri muje sati dayane zakiyi ki dawo ko ummi ya fada yana kallon ummi dariya tayi" eh sati daya zakiyi habibty ajiyar zuciya ta sabke" to naji amma da anyi sati zaka maidoni kuma ba gidansu wannan banzan gayan bane zan zauna ko ummi ta matso ta doketa abaya tun karfi take dukanta tana mata magana da larabci saida ta Saki Kara ta rukunkume Mahabeer tana kukan sangarta tare dukan yai yanaba ummi hakuri ransa babu dadi Dan yaji haushin bugun da take mata kamar yayi kuka yace" haba ummi Raiyan Zee yarinya ce fah lallabata zamuyi zata daina masa amma dukan yayi yawa sai ajimata ciwo ai idanu ummi Raiyan ta zuba masa cike da mamakinsa " haba Mahabeer yanzu ahakane zaku ku gyarata kana daure mata gindi wlh shiyasa naso yazo da kansa tun kafin su isa can taci gidansu la'ada waje  cikin shashekar kuka tace" Ahukhuya kagani kullum sai ummi ta dokeni

saboda wannan mungun mutumin wlh idan mukaje Nigeria mutikar na Ganshi akasar idona

idanusa kafin na dawo Allah na dauki Alkawarin sai na Rama abinda akamun akansa ta fada tana Kara rumgumesa tana kukan takaicin duk lokacin da zata zageshi sai ummi ta doketa kuma duka ba na wasaba shiyasa takejin duk duniya ta tsaneshi sama da komai Hasbinallahu Wani'imar Wakim kawai yake maimaitawa gashi bayason kukanta daurewa yayi yana bubbuga bayanta " yi hakuri kanwata nima bazan yardaba anaci miki mutumci yi shiru kinji ya leko fuskarta shiru tayi ta boye kanta kirjinsa samu yayi ya lallabata ya janyeta jikinsa Jamal da idanu yake binsu yanajin haushin yada idan tahau jikin Mahabeer yake janyeta baya bari ya rage zafi ba lallashinta ya shiga yi har ta Saki ranta suko su manal sunsha mamaki Dan sunsan Zee baby bata cika kuka ba a Al'amuranta kuka baya cikin tsarin rayuwarta ummi dai da idanu take binsu yau ta Mahabeer take ta Saki jikinta sai labari take bashi yako maida hankalinsa kanta sai dariya yakeyi Jannat na tayasu Dan Mahabeer ya burgeta bashida damuwa akwai fara'a
Saida akayi kiran sallah magrib suka Mike sukayi shirin zuwa masallaci suma su Zee baby suka tafi suyi sallah sai tsokanarta sukeyi wai taga Dan uwanta ta sheresu dariya tanusu batace dasu komaiba,

************
✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨
*Nigeria* karfe shida na yamma Wata jibgegiyar motace fara sal da ita saman  babban titin malali cikin nutsuwa yake driving waya manne akunnesa sai murmushi yakeyi cikin amon muryasa mai dadin gaske naji yace" sweet baby kiyi hakuri wlh kukanki na daga mun hankali kiyi shiru ganina fah saman hanya zanzo na ganki shikenen ko OK Oya fito gani na karaso ina Sauri kar lokacin sallah magrib yayi ya fada yana tsinke kiran saboda ya Iso kofar gidan honr yai mai gadi ya bude masa ya danno hancin motar gidan yana parking ta fitowa masha Allah wata kyakyawa na gani baka ce sosai amma tanada kyau amma ba doguwa bace ba kuma bata fiye gajarta ba tanada hanci dede misali da idanuwa dede gwargwado tanada gashi ba laifi bakinta Dan karamine saidai tanada yar kiba kadan agaskiya dai batada makosa tanada kyau yar 23 year tanda faram faram batada daurin kai saide ta fiye sanyin hali batada hayaniya duk da a turai tayi karatun Nurse har tsawon shakara ukku isowa tayi ta bude motar ta shiga da sallama

tana murmushi shima murmushin ya sakar mata " sweet baby uwar yan rigima ya gajiya bazaki bari ki hutaba kamar bamu hadu da safe ba ya cikin naki da fatan kinsha magungunan da na kawo miki kanta ta sada tana wasa da  hannuta " nifa kinga matsalata dake dagowa tayi Dan tasan halinsa yanzu zaiyi watsi da lamarinta ya tafiyasa Dan Sam bayason shariya " my Dr yi hakuri ta fada tana kallonsa cikin dauriya Dan kwayar idanusa fusgar mutum sukeyi my Dr na kayi kyau sosai kamar na saceka ta fada cike da kunya " OK Oya fadamun me kike so kika tisani da kuka sai nazo kuma gani kina wani sunne sunne ko cikinne ? kanta ta kwantar saman kafadarsa tana sabke ajiyar zuciya "sweet babyna menene bakida Ify ne ? " my Dr na wlh idan nayi awa biyu ban gankaba banajin dadine amma yanzu banajin komai na warke ta fada cikin sanyinta murmushin gefen baki yai ya dagota kanta daga kafadarsa ya kura mata mayatattun

idanunsa yanajin mugu mugun sonta da kaunarta na ratsashi Dan tarbiyyarta tayi masa tamkar ba aturai tayi karatu ba " my mashakurah wlh nima ina sonki nifa na ganki nace kinmun so sai me ki ajiye hankalinki Dr Sardauna nakine ke daya insha Allah kinji sweet babyna idanuta ta lumshe ta daga masa kai kiss ya mata agoshi " OK Oya shiga ciki kinji an fara kiran sallah kisha magani kinji? kai ta daga fitowa tayi tana daga masa hannu idanuta sun tara kwalla ya gani sairai idan yace ya lallasheta kuka zata saka masa shiyasa yaja motar ya fisgeta da karfi juyawa tayi ta tafi ta nufi cikin gida yana fitowa ya harba motar kan titi yana gudu sosai ya dauki hanyar kofar Marusa lowcos gudu yake shararawa sosai Dan ya samu sallah magarib, lokacin da yazo har an gama sallah honr yayi aka bude masa katoton get din gidan ya danna hancin motar gidan Ana harbar gidan yai parking ya fito gun mai gadi ya nufa agaguce yayi Alwalla ya nufi masallaci, bai fito daga masallaci ba saida akayi isha'i yana fitowa ya shiga bangaransu wow agaskiya ya hadu sosai d'akunane har biyar ukku daga farko biyu acikin wata yar kwana kwanar naga ya karya dakin karshene Nasa ya ciro key aljihunsa ya saka ya bude kofar wani ni'imataccen kamshi ya me fitowa tamkar yanzune akayi anfani da turarukan masha Allah nace saboda haduwar bedroom din wani royal bed makekensa d'akin ba tarkace amma zaka zata dakin amaryane ga wasu lumtsma lumtsuman kujeru na kayan jikinsa ya rage ya shiga toilet Yajima sosai ya fito daure da towel kirjinsa cike yake da gashi yana da fadin kirji sosai duk amunmurde yake tamkar yanacin karfe agaguce ya shirya ko mai bai shafaba yasa wando 3quater ya saka da Riga short ya fesa turare ya gyara sumar kansa tayi luf luf sai shegi take baka sudik wayoyinsa ya kwasa baki daya ya fito cikin kuzarinsa yake tafiya ko kofar bedroom dinsa bai rufeba ya nufi part dinsu ghaisha da sallama ya shigo parlon ghaisha na zaune Nawwara na jikinta yana shigowa ta Mike suna gaishesa yaran parlon hannu ya daga musu ghaisha tace" bokan turai baki ya turo kamar wani yaro zama kusanta ya kwantar da kansa saman cinyarta ashagwabe yace " ghgaisha nah wlh duk nagaji" sannu Dr Sardauna ai Dole tin safe sai yanzu tausa ta fara masa" yauwa mamana Allah kuwa ciwon jiki nakeyi dariyace ta kamasu Hafeeza ce dariya ta kufce mata khalisat ta zaro idanu ta Mike sadaf ta gudu tun kafin ya dago aikuwa ya zabura zai tashi ghaisha ta rikeshi suna ganin haka suka matso suna bashi hakuri banda hafeeza da khalisat da suka Ari ta kare ghaisha tace"maza ku tashi kusan nayi ai yasan wa tayi dariyar mik'ewa sukayi suka bar parlon baki ya ciza ya kalli ghaisha" yanzu Dan Allah mamana kina kallo khalisat mai zubin nunar rana itada yar iskan yarinyanan sukamin

dariya kawai Dan nama mahaifiyata shagwaba dariyar ta danne " haba Dr Sardauna khalisat baiwar Allah me take cewa acikin gidanan wlh banda ita akama dariya hafeeza ce ita zaka lakada amma banda khalisat baiwar Allah yarinyar da magana ma ba damunta tayi ba mareniyar Allah Aunty amarya ta fito daga kitchen tana dariya " Wlh Aunty daurin gindinki dai ta samu Dr mun kabarsu zanyi maganinsu baki ya ciza Dan ya tsara launin azabar da zai musu bayan sun mance da anyi abun danshi baya horo kai tsaye " Auntymu ki barsu zanyi maganinsu wayar sace ta dauki ringing screen d'in wayar ya kalla Ahmed ya gani mik'ewa yai yayi picking ya Kara a kunnesa ya fice daga parlon akofa suka ci Karo da Daddy murmushi ya masa "ah Dr kaida mutanan Saudia " Daddy bari na dawo akwai hira ya tafi yana magana Daddyn kansa ya girgiza Dan yasan tambayarce bata masaba ya samu ya sulube masa Dr Sardauna mota naga ya shiga yamata key honr yayi aka bude masa get ya fice daga gidan aguje,

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

*Saudi Arabia* bayan sunyi sallahr isha aka fito da abunci Wanda ragone jibgegensa aka gasheshi da dafe dafen abunci irin irin nasu na larabawa Jamal sai baki yake washewa zaune suke akasa saman carpet sun baje baki dayansu suka hadu sunacin abuncin ummi Raiyan sai farin ciki takeyi ta tuno da mijinta da yaranta yan mazan Zee baby na kusan Mahabeer ta tisasa da rigima Dole sai shine yake bata abaki itama nata bashi su manal sai dariya sukeyi ummi dai kai ta girgiza Jamal shifa haushin Mahabeer yakeyi. dan de ba yanda zai yine suna kammalawa mai aiki tazo ta kwashe komai ta gyara gun sukaje suka wanko hannusu aka dawo Ana hira su jannat sai karfe goma suka tafi gida sun rakasu suna dawowa su ukku ita da Mahabeer da Jamal suka tardo majeed kofar gidan ya fito amota yashi gaban Zee baby cikeda rashin kunya ta rike k'ugunta tana girgiza zatayi magana Mahabeer ya riketa ya janyota cikin gida aikuwa kafin kofar ta rufe ya biyosu yana magiya ta sauraresa hararasa Mahabeer  yake ransa abace cikin harshen turanci" kai malam kama gabanka tunda bata Sonka karabu mana da ita yau naga jaraba Dama haka kuke da kwawa ya dage sai masifa yake kirtama majeed shiko burinsa Zee baby ta kulasa dadi taji ta rungume Mahabeer tana dariya" yauwa Ahukuyah cimun durin uwarsa tunda ubansa yace baya kaunata na tsaneshi wollah bana sonsa yanzu dadi ya cika Mahabeer janyeta yai jikinsa ya kamo hannu majeed ya ingizashi waje jamal yace" wai kai ina ruwanka da shiga tsakanin masoya " dallah malam yimun shiru yaja hannuta su shigo parlo sai cika da batswa yakeyi itako dadi takeji sai sangarta take zuba masa jamal na biye dasu ummi Raiyan tace " Mahabeer wai dama tare kuke sakinsa tayi taje gun ummi ta rumgumeta " ummi bari kiji rada ta mata akunne " ah haba ikon Allah Mahabeer yanzu shirmenta zaka biyewa dariya yayi yana Sosa kansa hira sukaci gaba dayi sai karfe daya suka ma ummi sallama

Zasu kwanta Zee ta ririke Mahabeer bazai kwanta ya bari sai anyi sallahr asubah saida ummi ta riketa tace su tafi sukwanta kar yabiye mata ita ba bacci take ba dakinsu suka nufa ummi ta ja hannuta suka shiga bedroom d'in ummi tasa ta cire kayanta tayi wanka tasaka kayan bacci Riga da wando iya gwiwa ta lallbata suka kwanta tana rumgume da ita tana shafa mata gashinta kinyin barcin tayi tanaga ummi tayi bacci ta janye jikinta sadaf ta fito daga d'akin ta nufo parlo ja tayi ta tsaya ganin Mahabeer tsaya yana kai komo ya rasa me keyi masa dadi cikin farin cikin ganinsa ta nufi gunsa da gudu tana kiransa "Ahukhuya juyowa yayi suka hada idanu farin ciki ya ganin kan fuskarta amma ganin kayan jikinta ai bai bari ta karaso ba Dan yasan ba inda zata tsaya sai saman jikinsa ai kuwa ya zunduma da gudu ya nufi dakin da yafito yana shiga ya banko kofar ya murza key taji karan murza key din zubewa bakin kofar dakin tayi ta fashe masa da kuka tana kiransa Ahukhuya....✍🏻

Sai kunji next page insha Allah

*Karku manta kudin* *wannan book nera dari* *ukku ne kacal zakusha* *karatu maicike da* *abubuwa daban daban*

*na rayuwar duniya da wata irin rikitacciyar soyayya mai zafin gaske ga me bukata ya tuntubeni awannan number mu kashe magana Yanda* *zaki sambadi karatunki* *akan dari ukku kacal*🤸🏻‍♀️👇🏻
*+22796515805*

Rahma ce ummu Fareesa😘

*💖💖🙍🏻‍♀️ZEE BABY🙍🏻‍♀️💖💖* *HATSABIBIYA* *RAMLAT RETURN*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

---

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

---

*Story & Written*
*By*
*Real Ladingo😉*

*Bismillahir Rahamanir* *Rahim*

*idan kina bukatar book dinan Akan nera dari ukku yake ki tuntubeni saman number nen zamu kashe magana😉 +22796515805*

*Free Page*

page 4

.....sosai take kuka tana kiransa hankalinsa atashe yazo bakin kofar ya jingina yana sabke ajiyar zuciya yarasa ya zaiyi da zee baby gashi baya son kukanta hankalinsa tashi yake ahankali cikin sanyin murya ya kirayi sunanta " Zee babyna yi shiru banason kukanki kinji kara sautin kukan tayi tana buga kanta da kofar tana kiransa arikice ya bude kofar ya sunkuyo gabanta ya dagota yana bata hakuri tayi shiru bazai karaba tunda bataso jikinsa ta shige tana sabke ajiyar ziciya
```

bayanta yake bugawa alamar lallashi ransa duk babu dadi shi sam yanzu bayajin shawar kukanta yafi daga masa hankali hannuta yaja suka iso gun kujerun parlon suka zauna tana manne jikinsa har yanzu ajiyar zuciya take sabke dan taji haushin gudunta da yai ya rufo kofa fuskarta ya kamo yana goge mata hawaye " zee babyna kiyi hakuri ki yafemin bazan sakeba kinji kanwata idanuta ta zuba masa tana taro baki alamar bata hakura ba murmushi ya sakar mata

yana hura mata idkar bakinsa a idanunta lumshe idanu tayi ta saki murmushi ta boye kanta akirjinsa gashinta yake shafa mata yana mata hira mai dadi aikuwa ta fara dariya saida yaga kamar dariyar tayi yawa ya bari kuma cikin ikon Allah duk yada, take manne jikinsa baiji komaiba game da shawarta sai tsantsar kaunarta da take ratsa jininsa da tsokarsa har kusan karfe biyu da rabi ya ga fah batada niyar bacci har gyangyadi ya fara fur ta hanashi idanu ya bude ya kalleta" kanwata kiyi hakuri ki barni na kwanta kinji zee na? ganin yada idanusa sukayi ya bata tausayi duk batason rabuwa dashi ta dauré ta jinye jikinta anashi " Ahukhuya muje ka kwanta mik'ewa tayi ta kama hannuwansa suka nufi d'akin ashe duk zaman da suke a parlo Jamal na labe yana kallonsu ajinsa ko wani abun zasu oho yanaga sun nufo d'akin ya koma da sauri ya kwanta har dakin suka shigo tana rike da hannusa kiss ta masa " mu kwana lfy murmushi yayi ya daga mata kai ficewa tayi daga d'akin

ta rufo masa, kofar dakinta ta nufa naga ta daga hankadan pillow ta dauki wata yar kwallaba ta bude murfin ta kafa bakinta saida tasha rabi ta maida ta buye ta dauki wasu kwayoyi ta zuba bakinta tana taunawa ta kunna kida ta saki sauti wakar larabci ce sai tikar rawa take baji ba gani sai ihu take da tsalle da juyi kafin zuwa karfe biyar abubuwan da tasha sunyi mugun ratsata sai tangadi takeyi amma haka ta Mike taje tayi Alawlla tasaka Riga doguwa ta tayar da sallah amma ta kasa tsayuwa sai azaune tayi tana gamawa ta bungire saman daddumar sai bacci ya kwasheta,,

****************************************
Bayan kwana ukku zuwa wannan lokacin zee da Mahabeer sunyi muguwar shakuwa bata iya nisa ko nan da can tare sukaje sukayo sayaya tsaraba kaf yan gidansu yayo masu tsaraba tare sukaje  kabah yayi umarah wacce da kashigo garin ake rakaka kayi yayima zee baby Addu'ar shiriya da shaye shayen da takeyi dan ya kamata tasha kuma ajikinsa mayen ya fara kamata har kuka yayi ummi Raiyan tace ai shine babban abinda yake daga mata hankali shiyasa ta matsu tabar Nigeria dan tasan acan ina zataga kayan maye shiyasa ya kara Sata jikinsa dan yasan saida lallaba sun gama shirya kominsu na tafiya yau suke tashi karfe ukun dare zee baby har cikin ranta batason tafiyar amma da ta tuna sati dayane zatayi taji tanaso taje kasar hausa ta ga ya take ya tsarinsu da Al'adunsu yake tasha kunshi kafa da hannu kitsone dai ba'ayimata saboda tausahin gashin da santsinsa ko anyi tsefewa yakeyi ga zafi da ciwon kai da yake Adabarta shiyasa bataso

su manal da jannat da Radia tun safe suke gidan suka gaji da raye rayansu kuma suka koma kukan rabuwa saida ummi Raiyan da Mahabeer suka lallashesu sukace ai sati daya zatayi ta

dawo tukun hankalinsu ya kwanta suka saki jikinsu sukaci gaba da sabgar gabansu, sai bayan sallahr magrib sukayi shirin zuwa Jeddah gaba dayansu sukayi rakiya zuwa Jeddah,  karfe tara suna Jeddah  Airport zazaune sai lokacin ummi Raiyan takejin ciwon rabuwa da Zaeenaba amma ta dauré dan tasan idan zee din ta gani zatace bazata ba yawonsu su zee suka tafi da su jannat sai sayaya take duk ba sanin mutanen tayi taji tana son kaimusu abubuwan nan k'asar sai wajan sha biyu suka dawo Mahabeer yacewa ummi Raiyan su tafi dan bayaso sai lokacin tafiya yayi ta kafa kuka rungume juna kuwa suka suna kuka su dukansu sai daket ya lallabasu sukayi shiru Jamal ma sallama sukayi Mahabeer yayi masa godiya sosai da karamcinsa Jamal yace saboda zee gashinan zuwa Nigeria Mahabeer ya amsa dan yasan karyace Raiyan ta kara rumgume zee tanata sumbatarta itama sumbatarta takeyi sun jima ta jata gefe tayi ta mata fada ta nutsu tako amsa ta da to suka rabu kowa na hawaye abinda yasa zee bata damuba saboda ance sati dayane zatayi shiyasa su manal da kuka suka shiga mota suka tafi ji sukeyi kamar su bita, kuka ta fara daket yasamu tayi shiru

Sai karfe biyu da rabi suka shiga cikin jirgi saboda shirin da Mahabeer yayi bazaka taba cewa ba balarabe bane ba zee ko baka ganin komi nata sai kwayar idanuta to dama Al'adar garince haka jirgin cairo ne suka shiga sai karfe ukku da yan mintuna sukaji alamar jirgin zai tashi zee ta fara rawar sanyi dama jikin Mahabeer ta jingina kallonta yayi yaga tana karkarwa jikinsa ya janyota ya rumgume ya ciro mayafi ya lullubeta kara shigewa jikinsa tayi" zee,na menene? jinkita ya taba yaji zafi gum hankalinsa ya tashi dan yaji zazzabine ya zubo mata hannuta ta sakalo wuyansa tana hucin zazzabi ga rawar sanyin da takeyi kiransa tayi"Ahukhuya? " Na'am zeena yi hakuri kinji jirgin tashine zaiyi bari ya tashi na samo miki magani kara matseta yayi yana lallashinta yada ya shigar da ita jikinsa yasa ta rage jin sanyin cikin sa'a wani balarabe cikin ma'aikatan jirgin masu rabon abunci yazo wucewa Mahabeer ya tsayar dashi duk da yaga sauri yakeyi cikin sa'a ya tsaya ya tambayeshi da turanci maganin zazzabi yakeso matarsace babu lafiya yace" ok ya jira jirgin ya daga yanzu zai kawo masa, godiya yayi masa ya tafi yaji dadi sosai da za'a samu maganin tasha karfe uku da rabi dai dai jirginsu ya daga zee na manne da yayanta tana rawar sanyi hankalinsa ya kara tashi jirgin na tashi zee ta fara kwarara amai jikinsa ya rumgume tsam har ta gama yana bubbuga bayanta hankalinsa atashe " my zeena sannu kinji kai ta daga masa dagata yayi ya mike ya janyo jakarsa ya ciro wata jallabiya baka mai shegen kyau ya ciro karamar Jakarta itama ya ciro mata abaya shi ya fara zuwa ya gyara kansa cikin toilet ya canza kaya tsaf sai yafi d'azu kyau ya dawo ya kama hannuta suka tafi akofar toilet ya tsaya ya bata kayan ta shiga ta canza ta wanke fuskarta da bakinta

ta fito ya kamo hannuta suka dawo ya feshesu da turare ya zauna ta kwanta jikinsa ya lullubeta bai jima da zamaba mutumin ya kawo masa maganin harda ruwa da dan abin masarufi cimarsu ta larabawa ya lallabata ta danci ya bata magani tasha dan batada matsala da magani saboda ta saba cin kwayoyi Allura ce ko zata mutu babu uban da ya isa ya mata ita tanasha ya rungumeta yana lallabata ba jimawa tayi bacci ajiyar zuciya ya sabke ya duko ya mata kiss saman goshinta ya kara shigar da ita jikinsa ya rufeta ruf,  koda akazo rabon abunci bai amsaba dan shi bai fiye cin abunci ba idan yana tafiya kansa ya jingina da kujera ya lumshe idanusa dan bacci yakeji bai jimaba ko baccin ya daukeshi jirginsu na sharara gudu cikin hazo

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Karfe takwas na safe jirginsu ya sabka Egypt sabka da jirgiya yayine ya tashi Mahabeer da ya kananade zee suna shakar barci manne da junansu idanu ya bude cike da mamakin irin baccin da yayi tashinta yayi taki tashi dan sam bacci bai ishetaba bakinsa ya kai kunneta " my zee,na kitashi mun iso cairo juyan jirgi za'a mana zuwa Nigeria kinji my zeena? Shagwab'e masa tayi tanarke masa tana turo baki ashagwab'e tace" Ahukuhya? " na'am my zeena ya akayi" shiru tayi tana kallonsa murmushi yai mata " bacci ko kai ta daga masa, tana lumshe idanunta ganin mutane sun fara fita ya mikar da ita Dole ta tsaya mikewa yayo ya ciro karamar akwatunsu ya gyara mata mayafin abayar ya kama hannuta suma suka sabko dogayan motocinan sai kwasar yan k'asa k'asa takeyi suka shiga aka kaisu inda zasu zauna kafin jirgin da zashi Nigeria ya shirya suna zaune tana manne

Kusansa yayi ta lallabata taci wani Abu taki Dole ya hakura basu wani jimaba sosai ko awa daya basuba suka shiga jirgi yanzuma jirgin na shirin tashi yaga tanason yin amai rumgumota yayi yana bubbuga bayanta ya shiga mata rada akunne" my zeena please karkiyi amai ki daure wlh damuwa nake shiga yanda yake matan cikin ikon Allah taji batajin aman ta dago kanta ta zuba masa shanyayun idanunta tana murmushi tana shafar fuskarsa haka suka kure junansu da ido har jirgin ya nutsa sararin samaniya idanuta ta janye tana dariya ta dora kanta kafadarsa, ana raba abunci akazo kansu lemo kadai ya amsa adan cup yasha itako tace tea Mahabeer ya matsa ata amshi pizza ya bata abaki taci ta koshi ya bata magani saboda jikinta akwai zafi ya kwantar da ita jikinsa ya rufeta da mayafi ba jimawa tayi bacci dan dama ita wuni baccine tunda bata na dare bare yanzu safiyace shima baccin ya daikeshi ya jingina bayansa da kujera

🌟🌟🌟🌟🌟🌟🌟🌟🌟🌟🌟🌟🌟

karfe shabiyu da rabi na rana jirginsu ya diro garin Kano Mahabeer idanusa biyu jirgi ya sabka ya tashi zee idanu ta bude " munzu gida fah yanzu sai Katsina murmushi tayi ta shafi fuskarsa mikar da ita yai dan masu sabka har sun sabka yan Kano yan Abuja ne basu fitaba tashi yai ya d'aura mata Niqab dinta ya kama hannuta dayan hannusa, rike da jaka itama tana rike da jaka saida zasu fito wata latijuwa takira Mahabeer dan ita Abuja zata ya dawo " d'ana gaskiya ka iya rikon mace rayuwar auranku ta burgeni kai da yar balarabiyarka gatadai yarinya karama amma akwai nutsuwa Allah ya sabketa lafiya Allah ya karamuku dankon soyayya Allah yasa mutu ka raba kai da ita yaji dadin Addu'arta cikin farin cikin ya amsa yana godiya, suka sabko kallon gurin take ya burgeta sosai suna

Fitowa ta cire niqab ta tatare abayar ta dauré Mahabeer ya fara mata fada ta rufe jikinta surata duk awaje kar wasu yan iska su kalle masa ita shagwabe masa tayi yayi hakuri zafi takeji yanda ta shagwabe yasa yaji tausayinta maybe ko zafin takeji amma ransa bayason wani yaga kyawunta ya yaba ta lokacin su Daddy sun jima da isowa tarbarsu bayan sunje sun gama sa hannu anga posport dinsu sukaje gun kayansu Mahabeer ya jido ya zubaso cikin abun tura kayan bayan angama aunasu suka fito inda jama'arka ke tsayuwa domin tarbar baki Daddy ne ya fara hangosu ya kirasu Mahabeer yaga yan gidansu su shida ne sukazo sai Nawwara ita

karamace Dr Sardauna na hango cikin wani danyan boyal baki mai masifar tsada da kyau ya manna bakin gilashi kan fuskarsa wlh fadin kyawun da Sardauna ya zuba bata lokacine saide fuskarsa ba walwala harda mashakurah nagani taci uban kwalliya ta kece raini agaskiya tayi mutokar yin kyawu tana kusa da masoyinta sai wasu mace da namiji sukam ban sansuba sai ghiasha fuskarta dauke da farin ciki Mahabeer ya nunawa zee baby yan gidansu idanun da zata dago idanusu ya sark'e da juna amma ita bata ganin kwayar idanusa saboda gilashi ranta amutikar bace amma zahiri wani makirin murmushi dauke kan fuskarta ta kauda kanta tace" Auzubillahi minal Shaidanir Rajim Mahabeer ya kalleta yana nuna mata Daddy tana hangosa saboda ta sansa sosai ta pic ta yada Jakarta ta saki hannu Mahabeer ta ruga da gudu tana dariya shima dariya yakeyi Sardauna tsaki yaja ya kauda kansa aransa yace " Allah rabamu da jaraba gudu take amma gani take kamar an kara mata nisan gurin dariya suke ta mata yada ta zage tana gudu ko ina na jikinta motsi yakeyi masha Allah sai kallonta jama'a suke dan zee ba kyau Bade da sura tana dabda isa gurin Daddy sai kawai ta yanke jiki ta fadi da gudu sukayo kanta Mahabeer ya kira sunanta da karfin gaske "Zainab.... arikice yayi kanta da gudu kafin yazo Daddy har ya dagota amma abin mamaki bata mutsi babu alamar rai jikinta Mahabeer ya karasu ya amsheta yana kirkiza agigice amma bata motsa hankalin Daddy yayi mutikar tashi ya kalli Sardauna da yakema mashakurah masifa akanme zata to indai tana tare dashi karta kuskura taje kwalla tausayin zee ta goge ta sada kanta kasa Daddy haushine ya cikashi yace "dan ubanka zo maza dauki yarinyar muje asibiti mafi kusa ka dubamun lafiyarta idanu Dr Sardauna ya zaro bakinsa na rawa yace" Daddy ni kuma zan dauketa saboda Allah ga Wanda ya kawota nan Daddy bai sake maganaba yaje gun Mahabeer yace ya ajiye Zainab ya tashi baiyi musuba ya ajiyeta yace duk su tafi har mashakurah yace ta biyosu ya kalli Dr Sardauna yace" idan ka cika dan halak karka tabata kabarta ta mutum ka kaimun gawarta Katsina komin dare mu muntafi sai ka kawo mana gawarta yaja tawagarsa ghasha tazo ta dafa Sardauna cikin lallaba kome tacemasa oho kai ya kada yana kallon masoyiyarsa da aka hana tabishi saboda wannan banzar lips dinsa ya ciza da karfi yana kallonsu Mahabeer sai kukan zuci yakeyi kayansu yaje ya turo suka fice mashakurah harda kukanta an rabata da masoyinta bazata amotarsa ba sororo yayi yana gani har suka fice ransa yayi mugun baci ya nufi gunta yana yamutsa fuska ya kalli hannuwansa yaja tsaki sunkuyowa yai ya yaja mata rigarta ya ciccibeta ransa amutikar bace amma sai yaji sakwat kamar ya dauki yar karamar yarinya batada nauyi ko kadan miyau ya zubar ya kara hade face yayi waje da ita shikadai yasan yada yatsara cin uwarta da zai mata da zaran ta farfado....

🏃‍♀️Sai kunji next page insha Allah Wanda zamu shiga tarinhinsune kuma karashen Free Page ne Dan chakwayiyar da rikita rikitar gaba bata cikin Faree Page

*Karku manta kudin* *wannan book nera dari* *ukku ne kacal zakusha* *karatu maicike da* *abubuwa daban daban*
*na rayuwar duniya da wata irin rikitacciyar soyayya mai zafin gaske ga me bukata ya tuntubeni awannan number mu kashe magana Yanda* *zaki sambadi karatunki* *akan dari ukku kacal*🤸‍♀️
👇🏻
*+22796515805*

Rahma ce ummu Fareesa🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️

*💖💖👩🏻‍🦱ZEE BABY👩🏻‍🦱💖💖* *HATSABIBIYA* *RAMLAT RETURN*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

___

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

___

*Story & Written*
*By*
*Real Ladingo😉*

*Bismillahir Rahamanir* *Rahim*

*idan kina bukatar book dinan Akan nera dari ukku yake ki tuntubeni saman number nen zamu kashe magana😉 +22796515805*

*Free Page*

Page 5

*.....asalinsu* Alhaji Hasheem Almahadee magawata haifafan garin tahoua ne cikin Niger sun gaji sarauta GABA da baya mahaifinsa ne kan kujera mulki shidayane gun iyayansa rana tsaka aka riske gawar iyayansa lokacin yana kasar waje karatu labari na zuwar masa, ya dawo gida domin ahalin yanzu shine Wanda zai hau kan mulki anshirya komai aka hada yan mata biyu rana daya aka aura masa, amma sai me ana gobe nadin sarauta aka nemesa sama da kasa aka rasa, Abu kamar wasa, saida aka shafe shekaru biyu babu labarin Hasheem Almahadee Wanda suka kulla manakisar kuwa tuni sun hau kan sarautar suna zuba mulkinsu matan da aka
```

aura mishi kuwa tuni an kashe auran  shikuma baisan ya akayiba ya tsinci kansa a daura Nigeria yana yawo garari wani bawan Allah mai suna Alhaji Nuhu haifafan katsina ne amma mahaifiyarsa ce ta daura shi ya temakesa yana ganinsa yasan aikin jifane cikin ikon Allah ya dawo haiyacinsa yasha mamaki da ya gansa a Nigeria Katsina Nuhu ya tambayesa ko shi na wani garine dan ya ganshi jajur ga kyau tamkar balarabe bai boye komaiba ya labarta masa koshi waye Dan kasar niger ne buzune na Tahoua yagaji sarauta gaba da baya saboda itane aka fito dashi an kashe masa iyaye amma yace baya shawar komawa gida indai akan sarauta aka fito dashi yawon duniya ya hakura zai zauna ana Allah yasa haka yafi Alkhairi shikenan mafarin zaman sa tare suke hada hadar kasuwanci shida Nuhu tamkar uwa daya uba daya haka suke bayan shekaru kusan goma hasheem da nuhu sunyi aure sun zama wasu sunyi arziki shakaru na tafiya arzikinsu na bunkasa kuma har lokacin bai taba jin son komawa gidaba hasheem yanada yara hudu Abdulmutallab sai mai binsa Hauwa'u sai Faisal sai Salmanu daga kansu haihuwa ta

Tsaya sun taso cikin gata da kulawa Hasheem da zainab sunba 'ya'yansu tarbiya sun sami karatun boko da na Addina Allah ya kara bunkasa dukiyar Hasheem dan haka yace yaran sa kowa ya zabi kasar da yakeso ya tafi ya biyawa kowa yaje karatu lokacin Faisal yanada shekaru sha bakwai yace saudia nuhu ya tsaya masa kan komai saboda Hasheem yafi sonsa a yaran Nuhu akwai yayarsa acan madina Faisal ya tafi yake karatunsa cikin kwanciyar hankali da nasarori gidansu na Katsina abin kallone dan babu abinda babu aciki Hasheem na kula da yaransa shida zainab Abdulmutallab ne ya matsa masa saida ya gayamusu garunsu ya nemi izininsa ya tafi Tahoua gun dangin mahaifinsa cikin ikon Allah yasami tarba maikyau amma banda mai martaba ana Allah ya hadasu da Khadija suka kulla soyayya kafin ya dawo yana dawowa magana tayi karfi Dole hasheem ya tafi shi da Nuhu aka sanya ranar aure khadija yarinyace kyakyawa itama buzuwace GABA da baya farace tas kama Abdulmutallab sunyi aure cikin so da kaunar juna da mutum ta juna bayan bikinsu da shekara biyu ta haifi danta namiji yaci sunan Nuhu bayan shakaru hudu ta haifi Mahabeer shima sai bayan sharu hudun ta haifi mace mai sunan maijidda ko yayeta batayiba cikin ikon Allah tasake samun cikin ta haifo zankadeden danta namiji kyakyawa ajin karshe jajir dashi yaron

Akwai farin jini tamkar ba'a taba haihuwa ba shine yaci sunan  Almahadee wato Faisal tun yana karaminsa akwai son gaskia da son girma bayason raina ko kadan ga miskilanci da jiji da kai bai fiye fara'a ba idan ba yana tare da khadija ba wacce suke kira Ghaisha Kakansa hasheem ya saka masa Sardauna saboda yaron kana kallinsa kasan jinin sarautane ba karya sunan ya bishi tun yana karami yace karatun likita zaiyi ya temaki mutane to fah tun yana karami sukece masa Dr Sardauna kyawunsa ya fits daban agidan Dan sak kamar Hasheem ya fito yanada kanne hudu shima Najib ke bimasa sai Zainab sai hafeeza da auta Nawwara bangaran Mariya Amarya da Abdulmutallab ya aura saida ta kwashe shekaru biyar ta haifi yarta daya nana khadija sunan uwar gidansa sai mareniyar yarta da tazo da ita Khalisat idan ka ganta bazaka taba cewa ba yar gidan bace babu banbanci yarinyace kyakyawa amma ba canba batada laifi dai farace saidai batada hayaniya shiru shiruce suna zaune lafiya bazaka taba cewa ghaisha da Mariya kishiyoyineba sai Hauwa kanwar Abdulmutallab tana aure itama cikin Katsina da yaranta hudu sai salmanu shima yayi aure da yaransa biyu wannan zuri'ar Allah ya hada kansu suna

kaunar junansu yaransu sun taso cikin hadinkai da kaunar junansu Faisal ne kawai da baya kasar rashin auransu ya damesu sunata Addu'ar Allah ya janyo hankalinsa gid

*********

Faisal bayan ya kwashe shekaru tawas saudia yana, karatu bai taba zauwaba gidaba kuma bashida kiyuwa duk da ana aiko masa, kudi daga gida hakan baisaba yazauna ranar da ba karatu fita ya keyi neman na kansa dan yanaso shekarun biyu da suka rage ya koma kasarsa yabasu mamaki dan yanzu haka ya tara uban dukiya taban mamaki amma babu wanda ya sani ranar ya fito zai tafi daidai wani super market wani shahararan mai kudi sun fito da iyalinsa daga, siyaya zai shiga mota yada takarda ta fado aljihunsa da sauri ya nufi wajan daide ya dauka motar ta tafi dan taxi ya gani ya shiga yace yabi waccen motar bayansu sukebi har kofar gidan ya biya dan taxi ya nufi gun mutumin amma har sun shige gida yayi sallama yajima kafin ya fito yake tambayarsa, lafiya ya bashi takardar da ya yada bai saniba ya amsa ya duba saida ya tsorata dan takardun kadarorinsane da ya mallakawa yarsa kwaya daya Raiyan godiya yayi ta masa ya jasa suka shiga ciki yayi masa alheri sosai amma yaki amsa yace yayine don Allah sosai tarbiyar Faisal ta burge Fahad Abbu Rahaman to daganane suka saba ya sama masa aiki a kamfaninsa kullum yana gidan kamar dan gida sai abunda Fahad Abu Rahaman bai saniba Raiyan tun ranar da taga Faisal ta mutu akan sonsa tun tana daurewa har ta baiyana masa kiyawa yayi saboda tsoron balaraban saudia bayaba hausa dansa duk shima ba hausarba ne idan ma ba ance maba ba barabe baneba to bazaka ganeba saidai su suna banbance jansin su Abu kamar wasa Raiyan ta kwanta jinya ciwo hankalin iyayanta yayi kololuwar tashi har aman jini takeyi likita yace sumata abunda takeso zuciyarta takai matakin karshe dab take da bugawa nanne suka tambayeta ta fadamusu damuwar sunyi rantsuwa da Allah zazu mata dan basu taba zaton harakar soyayya ce jin sun mata alkawali yasa, tace Faisal ne takeso ranar anyi tashin hankali sunce saidai ta mutu taya zazu aurar da ita da Wanda basusan asalinsa ba kuma ba hausarsu dayaba, da sukaga fadan bayayi suka dawo lallashi suna rokonta tace ta janyen tunda sun mata alkawali har kuka suka mata amma fur takiya karshema da, numfashinta ya dauke saida, tayi sati bata farfadoba ganin zazu rasata yasa sukace sun yada ta zureshi saboda alkawali amma ba ruwansu da ita kuma yada yasasu bakin ciki taki musu biyayya itama sai ta zubar da hawaye haka akayi bikin Hasheem da Abdulmutallab su ne sukazo akayi komai amma Faisal yace shi yananan bazai komaba saidai ya rika zuwa ziyara. bayan aurene Ashe mahaifin Raiyan kodiri dayawa aransa sosai Raiyan da Faisal soke zuba soyayya kamar ba gobe Ashe shima yana sonta ganin kamar abin bazai yubane yasa da farko yace bayason ta bayan auransu da shekara biyu ya kammala karatunsa

cike da nasarori ya sami aiki a Jeddah Dole sukabar madina koda sukaje sallama gidansu Raiyan ba Wanda ya kulasu haka suka tarkata suka tafi lokacin tana fama da laulayin ciki yana bata wuya saida ya warware sosai ta samu sauki, ranar haihuwa ta zagayo taci uwar azaba amma kasa haihuwa tayi da kanta sai tiyata akamata aka ciro yara ukku maza biyu mace daya kyawawa, masha Allah ranar Faisal ya nuna tsantsar farin cikinsa amma babu Wanda yazo daga gidansu Raiyan sai wata Faisal ya samo take kula dasu, ranar suna ya sakawa mazan Hassan da hussaini macan sunan mahaifiyarsa, Zainab ranar anyi bidira a Nigeria yan uwa sai

jin dadi sukeyi suna jinjina al'amarin Ashe rabone tunda Fahad yaji labarin Raiyan maza ta haifa yaji dadi sosai yasan yanzu zai cika burinsa haka akayi ta tafiya rayuwa na gudu yaransu sun girma sosai saide sunfi shagwaba zee baby yarinyar akwai fitina sosai ga mugunta har uwayan bata bariba gashi muguntar ta tafi karfi suma mazan imusu takeyi makaranta mai tsada ubansu ya sakasu ko acan bata barin yaran mutane har malaman sun dukanta to ranar basu ba koyarwa idanu take likewa ta koma gefe tana dariya ahaka saida aka canza masu maranta ukku daide lokacine Faisal karami yazo karatunsa na likitanci Wanda zai dauki tsawon shekaru biyar amma yana madina sai karshan wata yake zauwa jeddah

sam jinunsu bai hadu da zainab idan tayi ba daidai ba dukanta yake ba da wasaba kuma hakan yanawa iyayanta dadi dan duk rashin tsoronta to tsoronsa takeyi ba da wasaba dan babu irin azabar da baya mata yan uwanta har kuka sukeyi tasha masa kunama amma duk yaji zafi zai dake sai bayan ya gusa yaje yayiwa kansa Allura ta rufe masa idanu yafi akirga amma dan taurin rai bai taba nunawa yaji zafin abun ba to wannan abubuwan yasa zee baby take tsananin tsoronsa tana tunanin to shi wani irin mutumne

dan taga yada mutane suke tsalle idan ta cutar dasu amma shi sam idanma tamasa guri yake nema ya zauna ko iyayanta sun roketa sai yacemusu kar ta kuskura ta bude masa idon yafi son zama dama baya gani kuma cizon kunama burgeshi yakeyi to ita ko ta tsani abunda yakeso shiyasa ta fasa masa saide duk ranar da muguntarta ta motsa sai tamasa, haka rayuwa tayi ta tafiya zainab ta gama primary school ta shiga secondary school loakacin kyawunta ya baiyyana kawayanta duk diyan hausawane jannat ce kadai balarabiya manal hausawane kuma dama tafi kulasu kaf cikin kawayanta jannat ta koya mata shaye shaye manal hausa dama kuma mahaifinta na koya mata, zee baby ta kware wanja shaye shaye da fitsara da rashin kunya gidan rawa ba inda bata zuwa gata da saka kananu kaya idan tayi shigar abaya ta fito to tana zuwa sai tacire ashiga, shaye shaye da raye raye idan kaga zee baby agida to Sardauna na garin to fah ko hauka take bazata fitaba saidai ta hanasu bacci dan kure kida take tana ihu da raye raye amma bata shan komai dan akwai lokacin da Faisal Sardauna ya yanka mata harshe kuma yace idan ta barsa ya kwana aduniya bata cika yar halak ba abun na damun Raiyan sai dai tayi ta Addu'a Faisal kuwa sai yace yarinta ce zata daina amma yanajin dadin yada Faisal karami yake hura masa ita haka sukaci GABA da rayuwa Hassan da hussaini iyanyansu sun kasa gane kansu duk sun canza musu ba kamar zee baby ba suma saida Sardauna yaci ubansu kafin su fara daidaituwa ana cikin haka Faisal wata Ranar. juma'a ya fito daga cikin gari yana waya yana driving kawai sai jiyayi babbar mota ta shigesa kafin yayi wani kokari mai afkuwa ta afku dan daket aka tataro na mominsa yayi raga raga abin babu dadin fadi ranar Raiyan ta shiga tashin hankali

Sardauna lokacin karatu ya tisasa gaba ya nemi ma alfarama yazo sun hanashi Dole ya hakura zee baby mutuwar mahaifinta ta girgizata mutika komai ajiyeshi tayi agefe ta nutsu ummi Raiyan haukane batayi ba yan Nigeria da sukazo saida akayi sadakar arba'in suka koma cike da jimamin mutuwar dan uwansu Wanda sukafi so saboda kirkinsa yana saudia ma babu abinda ya rage na zumunci bayan Arba'in Hassan da hussaini suka bijirewa ummi Raiyan fur basu ragamata ga wata irin tsana suka mata tun zee baby bata luraba har ta lura tako ci ubansu

mafarin da mahaifin Raiyan yazo ya dauke yaran babu yanda baiba yaja hankalin zee ta gujema Raiyan takiya shiko yace yayi alkawali sai yaga bayan duk mai kaunar Raiyan to daga shine zee ma ake farautar rayuwarta gashi rashin jinta yayi tsauri yanzu idan ta fita bata dawowa gida sai tayi kwana biyu ana haka watarana Sardauna yazo ummi Raiyan take fada masa yada zee ta kara lalacewa ransa yayi mutikar baci cikin sa'a kuwa tsakiyar dare ta dawo wlh ranar saida ya sumar da ita saboda launikan azabar da ya gana mata ya kuma yankarmata aharshe saboda tayi shaye shayen to tundaga lokacin Dole ta tsayar da yawon saidai ta tara kawayanta agida ana haka har Sardauna ya ka kanmala karatunsa shekara biyar yazama babban doctor wanda kafin yaje an gama Gina masa makekiyar asibiti mai zaman kansa wacce akasawa sunan *Almhadee Sardauna clinic hospital* asibitin da ta tsaru garin katsina iya tsaruwa nan unguwar malali cike da kewar juna suka rabu da ummi Raiyan tana kuka zee kuwa d'aki ta shiga ta rufo ta saki sauti tana mai farin ciki masifa da

jaraba tabar su har abadan yanaji bai dai biyataba idan kaga Sardauna bazaka taba cewa ba balarabe baneba saboda tsantsar kyawunsa kamarsu daya da zee dan ita Faisal ta fito sak sabanin mazan da suka fito Raiyan ya jadada, mata mutikar halinta da ta canza ya dawo ta kirasa shi zaizo ya kaita Nigeria ko dan kwasar shara su aura mata ummi harda dariyata haka ya tafi da haushin zee baby da yan uwanta da suka tsani ummi Raiyan bayan ya komane aka bude hospital din wada ake tururuwar zuwa dan Faisal Sardauna Allah yayi masa, baiwa kan aikinsa kaf katsina shine akeji dan ya karanci fanni ko wane ciwo a tsawon shekaru biyar da ya kwashe a saudia amma yafi aiki fannin zuciya da kwakwalowa da kuma binciken lafiyar mata amma duk da haka yana kula da, kowa shiyasa yayi suna a Nigeria ko wani gari kiransa akeyi indai ba mutum na matsa bane to bai fiye zuwaba yazo da wata dayane suka hadu da mashakurah an kawota batada lafiya Dan tana fama da ciwon ciki shine ya dubata lokaci daya sonta ya kamashi amma bai fada mata ya dai saka akabisu har gida aka ga gidan bayan kwana biyu yaje baisha wuyaba ta yarda amma tace tana karatune a London yanzu haka saura wata biyar ta gama tazo hutun karshan shekarane nan tabashi tarihinta tace subiyune gun iyayansu Alhaji Ma'aruf shine mahaifinta dan siyasa ne yanada kudi sosai duk da baikai su Sardauna ba sai yayarta Amina tana aure Abuja mashakurah kyakywace baka tanada jiki akwaita nutsuwa ga tarbiyya bata fiye surutuba haka suka kulla soyayyarsu har takoma taci GABA da karatunta kullum suna mnnne da waya sunajin lafiyar junansu,

Bangaran zee tunda Sardauna ya tafi ta maido iya shege so biyu tana samari kuma tana son su amma daga baya dai suce iyayansu sunce bazasu auretaba duk tana yarinya bawani girmaba tayi ba tunda secondary take amma tanajin ciwo ana hakan suka hadu da majeed shima haka ta faru to da zaran sun mata haka ta haramtasu dama ita tafison gwarzon namiji tsayaiye Wanda zai juyata mutikar ba hakaba to tasan mijinta zaici bakar wuya agunta gashi har yanzu bata samu ba shiyasa take soyayya sama sama ana cikin haka su biyu ana harin zee za'a kasheta Allah yake gyarawa ta sha amma hakan bai hanata

Yawoba to hankalin ummi Raiyan yayi mutikar tashi ga yaranta sun tu SATA GABA tabasu gadon ubansu Dole ta basu duk wata kadara abuye dan sunyi mata kashan kar zee baby ta sani bayan nan taji ta tsani zaman jeddah Dole ta tatara abinda yake hannuta ta siyar da gidan

da suke ciki suka koma cikin garin mekkah ta nemi unguwar hausawa khaleedia tasayi wani rantsatsan gida zee tayi ta rigima ita babu kawayanta su manal da jannat Ashe suma can sun tayarwa uwayansu hankali Dole sukace zazu kaisu mekkah su kammala karatunsu tunda duk suna da yan uwa acan hakan yamusu dadi dan makaranta daya suke kullum suna tare da juna amma iyayansu sun sa ansaka musu idanu dan duk shaye shayen da suke aboyé sukeyi su basa fito da iskancinsu kamar zee haka sukaci gaba da karatunsu har ranar gamawa tazo kuma mahaifin Raiyan har yau baisan ta kauro mekkah sunyi nema har sun gaji yanada kodirin kashe zee baby duk inda take ranar da suka gama secondary school da kwana ukku suka hada gagarumin party majeed tundaga shine bai koma jeddah ba yake zaune a mekkah gidan kawunsa ranar zee ta zuba hau maza da mata suncika gidan anci ansha ranar kwayoyin da tasha basu faduwa to daga shine ummi Raiyan ta yanke shawara Dole tabar saudia washe garine sukayi wannan raye rayen wanda majeed yace mahaifinsa yace ita yar macace shiyasa ta tsaneshi ta fasa saurar ansa da taso suyi aure da Maharaz amma yaso mata Fade shima shiyasa ta rufe babinsa dan ta tsani mazinaci arayuwarta ana hakane Mahabeer yazo kaita suka lula Nigeria wasu samarin basu ko sani ba  suma su jannat suna shirin komawa jeddah tunda karatu ya kare ga kawarsu batanan
Wannan shine asalinsu

*Mun dawo cikin labari*

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨
Taku yake cike da izza tamkar ba mutum ya rumgumo a hannusa ba fuskarnan tam ahade mutane cikin Airport din sai kallonsu suke cike da shawa parking spece ya nufa tun daga nesa naga ya danna rimote  wata wulwuleliyar motar  baka sudik  k'irar land range Rover évoque 2020 ta bude bayan motar ya cillata ya rufo ya shiga mazaunin direba yai mata key yaja da karfin gaske ya fice yana hawa kan titi ya kunna sigari yana busa baki da hanci hospital Nasarawa ya nufa ya dauki wayarsa ya danna wata number bugo biyu aka daga saita nutsuwarsa, yayi " Asallama Dr Yakub ykk" gud kana hospital ne ganinan saman hanya zan duba wata koran makkah ok bey sai nazo kitt ya tsinke Kiran ya maida hankalinsa kan driving har ya isa asibiti parking spèce ya shiga da motar fitowa yayi ya bude bayan motar ya ciccibeta ya rufe motarsa anutse yayi ciki da ita a respections ya hadu da Dr na jiransa ya taresa suka nufi emergancy Dr Sardauna yace" ai ba sai muje canba ba wani matsuwa tayi ba bani room inda ba kowa zan dan duba zata farfado? " ok Dr muje wani room suka nufa ba kowa tsaf dashi komai na gwaje gwaje akwai ya fita ya bashi guri wurgata yayi saman gadon ya cire gilashin fuskarsa ya shiga aikinsa yada ya dace saida yayi awa, daya cur akanta atsaye yana famar ceton ranta ya samu numfashinta ya dawo amma bacci take tsaki yaja" ai wlh dama kwayoyin sun kasheki shegiya mai ruwa da tsuntsuwa yarinya karama sai masifar shaye shaye toilet ya nufa bai jimaba ya fito ficewa yayi daga d'akin, yafi awa daya kafin ya dawo saida yayi sallah azuhur sosai Dr yakub ya karamashi yako ji dadi hakan tare suka dawo d'akin har yanzu bata tashi ba sun jima suna hira da yakub ya fita  zauna bakin gadon yai da niyar kiran mashakura yaji sun isa lafiya Dan yayi niyar yana gama wayar zai tasheta yaci ubanta Kafin su tafi wayarsa ta dau ruri ganin Mahabeer ne yasa ya dauka ya kara akunne" my brother saboda Allah kana

ganinta ta ci kwaya har tamata yawa ga yunwa kuma kazo ka banka mata kwayoyin zazzabi suka hadu sukayi mata yawa shegiya tantiriya wlh dama mutuwa tayi masifa Mahabeer ya fara masa karya kuma zaginta murmushin gefen baki yayi baice komai ba ya shiga ciza lips d'insa Mahabeer

Yayi magana cikin lallaba " Dr Sardauna namu Dan Allah gayamun zee babyna ta farka idan ta farka bani ita na kwantar mata da hankali Dan nasan rigimar nemana zata maka banaso tayi kuka kuma kayi tuki ahankali bata saba da wahalaba ran Dr Sardauna yayi mugun baci amma ya nutsu yana saurarон yada Mahabeer yake kafa masa sharuda a kan banzar yarinyar nan yar kwaya itako lokacin ta farka tana manta da ba Saudia take ba ganin bakaken kayan jikinsa da yanayin sa na Mahabeer duk da taga yau kamar ya Kara girma tunda Sardauna yafi mahabeer girma da cikar halitar Namiji mikewa tayi zaune ta rungumeshi ta baya ta sakalo hannuwanta ta wuyansa ta kwantar da kanta saman wuyansa ashagwabe ta kirashi tana shafa fuskarsa " ya Ahukhuya me yasameni ta fadi tana Kara rumgumarsa shiru taji kukan shagwaba ta saka masa " wlh Ahukhuya yunwa nakeji ta fadi tana goga fuskarta kagon bayansa tana kuka k'asa k'asa iya karshan Bacin rai yau Sardauna yaje idanusa sunyi bakikirin ya janyota ya birkitota ta dawo gabansa jikinsa har tsuma yakeyi ya yarfa mata maruka har hudu ajere ya bankare mata hannuwa ta baya saida sukayi Kara bashiri ta Saki ihu " Dan Allah Ahukhuya yi hakuri me namaka cilata yayi ta hadu da bango saida goshinta ya fashe tunda take bata taba jin azabar da takeji yanzuba ga yunwar da takeji ga cikinta na mata ciwo kafin ta Mike taji ya harbata " yar iska yar kwaya wlh sai kin gwammaci mutuwa da rayuwa take mata kafafu yayi sai yanzu tasan da wa take idanu ta dago ta kalleshi  ido hudu sukayi kauda kansa yayi duk da taji mugun tsoronsa ga wata irin walkiya da take fitowa daga idanusa da yanyin yada taganshin hadiye tsoronsa tayi ranta idan yayi dubu ya baci yinkurawa tayi ta Mike tsaye ta rike kuguntа tana girgiza cikin dauriya dan taji azaba ga cikinta na ciwo tace" kutumar babbar buro ubancan kai idan na yafema dukan da kamun ayau Wollah Ba Faisal Hasheem Almahadee bane ubana ta fadi tana tunkarosa shikuma tsaye yake yana wani miskilin murmushi ya tura hannusa cikin kwantacciyar sumar kansa yana shafawa yana ciza lips dinsa Dan ransa yakai kololuwar baci jiranta kawai yakeyi yaga mai zata iya dashi idan ta iso gareshi....

🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️Nagama Free Page duk mai bukatar cigaba da wanan labari mai bada kala da abubuwan mamaki da rikita rikita da wata irin mahaukaciyar soyayya ta fitar hankali da tsantsar love to anemeshi Akafta⛹🏻‍♀️⛹🏻‍♀️⛹🏻‍♀️

*Karku manta kudin* *wannan book nera dari* *ukku ne kacal zakusha* *karatu maicike da* *abubuwa daban daban*
*na rayuwar duniya da wata irin rikitacciyar soyayya mai zafin gaske ga me bukata ya tuntubeni awannan number mu kashe magana Yanda* *zaki sambadi karatunki* *akan dari ukku kacal*🤸🏻‍♀️

👇🏻
*+22796515805*

Rahma ce ummu  Fareesa🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️

*ZEE BABY*

*DAN ALLAH KARKU FITARMUN DA BOOK WAJE*

*👉🏻6*

.....wayarsa da take ajiye saman gadon ta dauki ringing gunta ya nufa yaga sunan Daddy jinin jikinsa yasha tabbas Mahabeer ne zai hadasu Dan tabbas yaji Marin da yamata Dan bai kashe wayarba lokacin saboda tsabar bacin ran dayake ciki hannu ya beka ya dauki wayar yai picking ya Kara akunne aikuwa fadane Daddy yake kirta masa " wlh Faisal idan ka kuskura kakuma bugunta ko kayarda tazo min da balshe ko sawun Mari Allah sai nayi mugun bata maka rai fiyeda yada baka tsammani kasan gabar nabaka Amana ka kawomun ita Katsina cikin koshin lafiya  gaban Dr Sardauna ya fadi ya kalleta tana dabda isowa gareshi ganin Marin da yayi mata fuskarta tayi jawur ga goshinta ya kumbura abunka da farar fata har ta  iso gunsa raina a bace na na isa gabansa bai mun magana yana sauraran fadan mahaifin nasa da sharudan da yake gindaya masa dukansa na shigayi  Dan na jigata kirjinsa nake bugo ina cizonsa da yagonsa tun karfina ko gezau baiba har Daddy ya tsinke kiran ya gyara tsayuwarsa nima Dan taurin kai naki daina dukansa Abu kamar wasa saida na shafe kusan Rabin awa ina yagonsa da cizonsa ko gezau baiba kuma ko kallona baiba nagaji sosai ga cikina na ciwo ga yunwa amma Dan taurin kai na Dage sai bugunsa nakeyi duk na cicijeshi amma bai nuna gazawa ba ganin na jigata yasa na tsayar da dukansa na zube k'asa

Ina ciza bakina Dan ciwon cikin nakeyi ga kaina na ciwo amma na daure na kiyin kuka birgima na fara ak'asa ina kiran "Ahukuhya kazo wannan mugun banzan zai kasheni wayyo cikina ciwo wayyo yunwa nakeji wayyo ummina kallonta yayi ya Saki kayataccen murmushin farin ciki saboda ko ba komai yanzu itace ak'asa bakin gado ya koma ya zauna yabarta tana ihunta tinkarfi har idanunta suka fara lumshewa Dan ciwon ciki takeyi ba da wasaba  wayarsa ya dauka ya kira yakub ya fada masa yanason akawo masa abunci baijimaba ya kawo masa daga kofa ya tsaya yayi knocking din kofar yazo ya bude " wai ko a saka mata drip ne? ah barta zata mikene wlh abuncinma Dan Daddy ya doramun yauni ne Dole yanzu tana cikin Amanata dariya yayi yamasa sallama shiko ya rufo kofar yazo ya ajiye abuncin yazo ya sunkuya ya dauketa cak Dan har ta suma shi abun dariya yake basa wai yunwa ce ta sumar da ita kan gadon ya kwantar da ita ya dauki robar ruwa ya bude ya kwarara mata ajiyar zuciya ta sabke ta bude idanu ta kalleshi harara ta zabga masa cikin karfin hali da harshan larabci tace masa " Allah ya isa mugun banza mugun hofi insha Allah sai kaga muguntarka ai kallon da yamatane yasa ta katse maganar tana zumburo baki ransa abace yake yakai kololuwar baci Dan de shi mutumne da

baya tsallake maganar mahaifa saboda fatan gamawa da duniya lafiya hakuri yasama ransa Dan yasan bakin yau dayane bashi ba ita babu abinda zai sake yada ya hadasu bare ta zageshi bakinsa da ita tayi badede yaci ubanta kamar yada yama mahaifiyarta Alkawali amma idan batayi ba shi baya fatan hanyama tarika hadasu Dan bata cikin tsarin rayuwarsa ajiyar zuciya ya sabke Dan soyake ya lallabata ya murza mata goshinta kartaje ahaka mahaifinsa yayi fushi dashi awaje ya furta "annaoba kawai zama yayi bakin gadon ya bude plate din abuncin ya ajiye mata saman cinyarta zata buge plate din abuncin ya zube yayi zafin nama ya rike hannuta ya boye bacin ransa ya zuba mata mayatattun idanunsa masu masifar dafi cikin wata irin murya yace" Oya ci abunci ya fada babu wasa duk da ya mata kwarjini ta basar ta buge hannusa tana murguda baki " anki baza'a ciba ko dolene meye hadinka dani ni zanci wannan kazamin abuncin ta fada tana yamutsa fuska lips dinsa ya ciza na k'asa baice mata komaiba ya Saki hannuta " OK tashi mutafi  kadai ya fada bai sake kallonta ba Dan bai fiye surutuba mik'ewa yayi

yana karkada makullan motarsa shikuma dama barazana yamata Dan bazai tsaya lallashiba ta kuma rainashi yanzu ma badan mahaifinsa ya daure saba yaushe ta isa tana dukansa da cizo ya kyaleta tayi kadan yarigai ya gano tanason abuncin Dan yaga yada take hadiye yawu kiransa akayi ya daga wayar yana amsawa ya nufi kofa cike da takon sa  na shidin namijine cikake mai lafiya da kuzari Wanda babu wargi cikin lamuransa ai tanaga ya fita tahau cin jalof din wacce taji kayan lambu da  ga gasasar kaza asama sai kamshi takeyi yawunta har tsinkewa yakeyi Dan yanayin girkin irin na larabawane sosai takeci da Sauri Sauri Dan bataso yazo ya iskota sosai taci iya cinta Dan ba wani cine da itaba amma yau yunwa tayi mata mugun kamu sai Dan kadan ta bari tayi Sauri takeyi ta sabko daga gadon ta sabko da plate din ta dauki dayan plate din ta rofe ruf kamar ba'a ciba ta ajiye ta gyara gadon taje ta wanko hannuta da bakinta ta cire rigar abayar ta shanya ta kunna fanka don yajiga mata ita da ruwa ta dauki gora ruwa Tasha ta koma ta zauna saman gadon daga ita sai dogon wandon da ya dameta sai yar ficiciyar Riga wacce ko cibinta bata rufeba yar tsakiyar da ta tilla cibinta ta saka sai gurin yayi tsaf tayi kyau sosai ga jeren tillar kunne Tasha kananun barima na zinare ga hancinta shima tasaka barima na zinare k'asan labbanta shima da tilla tasaka yar barima wlh tayi mugun kyau sai tazama tamkar haihuwar Ethiopia saboda kalar fatarta bata cika fariba

tas tunani ummi ya fado mun na fara matsar kwalla ga goshina da yake min zafi wayoyinsa har biyu da ya bari babba da Karama na kalla naji inason magana da ummina har na sa hannu zan dauka nama kaina fada na fasa Dan mai wayoyin ba mutumcine dashiba kofar ya tura ya shigo idanu muka hada naja tsaki na kauda kaina da Sauri ya kauda kansa daga kallonta" ke Dan ubanki tashi kisa Riga ya fada cikin tsawa naji tsoron yanayinsa mutika

yada naga ya dawo lokaci guda amma na boye tsoron ina kallonsa nace " baru ba gareta rigar kuma sanyi nakeji ai ganin ya nufoni gadan gadan yasa na Mike aguje naje na janyo rigar nasaka ina tsinemasa albarka Dan sanyi nakeji yanzu zazzabi na iya kamani bakin gadon na zauna wayoyinsa ya dauke yasa aljihu "Oya muje ya fada yana bude plate din abuncin yaga wayam idanu ya zaro ya kalleni baisan ta ina dariya ta zomasa saida yayi yai nadamar yinta Dan zata ita rainasa niko wata muguwar kunyace ta kamani nan take na fashe da kuka nayi

kansa ina dukansa akirji ina masa Allah ya isa me yagani ajikina na dariya saida nagaji da dukansa Dan kaina na fada saman kirjinsa na rumgumesa ina kuka tamkar ummi ta rasu Dan ina mamakin jarumtarsa ga kunya ta cikani kansa ya dafe yanajin ciwon Amanar da Daddy yace ya basa Mara tarbiyya nan tanason hadasa masa hawan jini janyeni yayi daga jikinsa ya kama hannuna muka zauna bakin gado baimun magana ba ya kama goshina yana murzawa gurin kumburin tin karfi " wayyo ummina zai kasheni wlh Dama banzo kasarnan ba mugu azalumi janyota yayi jikinsa ya matseta da kyau saida ya murje gun tas ya koma kafin ya saketa yana zubar da miyau ya Mike tsaye baimata magana ba ya bude kofar ya fice toilet

naje na wanko fuskata na biyo bayansa suna tsaye akofa suna magana da Dr Yakub nesa dasu na tsaya ina cika da batsewa yakub yace" kanwarmu sannu ykk? ayatsine nace "ni banajin Hausa dariya yayi Dr Sardauna yabashi hannu sukayi musabaha har gurin mota ya rakomu suka sallama baya na bude zan shiga tsawar da yamun tasa na dawo gaba na zauna tsaki yaja yama motar key suka fice daga asibitin yana hawa kan titi ya fara sharara gudu tunda ya fara driving ko kallona baiba wayarsa ya dauka ya kira wata lumber bugo daya aka daga cikin zazakar mursa ya fara magana cikin wani voice mai dadin gaske fuskarsa kamar bashi bane yake cicin magani " hello sweet babyna ykk? ko me tace ya Saki murmushi " lokacin bana kusa to ya gajiya Nima ganinan ahanya sosai yake hira suna zuba love tamkar bashiba ne mai tsamarnan niko sanyi nakeji sosai na fara jin zazzabi hakorana sun fara haduwa giri guda kallonsa nayi driving dinsa yake da hannu daya cikin nutsuwa yana wayarsa hankali kwance baki na ciza Dan wlh duk uwar wuyar da ya bani sai na Rama yauma Dan banida lafiyane sanyi ya adabeni gashi banida wani abun da zan rufa narasa ya zanyi ganin wayarsa yake kawai na matsa jikinsa na kwantar da kaina kirjinsa na zagaya hannuwana ta bayansa na rumgumesa gam na cusa kaina kirjinsa ina sabke ajiyar zuciya har tsawon minti uku sosai naji dadin hakan sanyi ya fara raguwa hannuna na dora saman wuyansa ina shafawa ashgwab'e na kirasa"Dr Sardauna ko gezau baiba yaci gaba da wayarsa yana driving d'insa duk da ta matseshi sosai ya bar tane saboda zafin da yaji ajikinta saida ya gama wayarsa ya ajiye wayar ya gangara yai parking can k'asa k'asa cikin daddar muryasa dan shi bai fiye taratsiba yace" wlh nidai an hadani da jaraba Dan ubanki ni sa'an kine meye zaki bani kike, kiran sunana bakin yaune kikeda damar hakan gobe ko ance ki nufi inda nake wlh bazaki zo dan ni bana yinki sam ya fadi yana janyeta jikinsa niko dama raguwace wajan zazzabi banida hakuri kuka na saka masa na Kara shigewa jikinsa" Dan Allah mai Suna Abbu kayi hakuri sanyi nakeji na fada ina karkarwa tsaki yaja ya tabe baki inda yake ajiye magani ya duba cikin sa'a ya samu ya dauka ya ballo biyu ya dago kanta ya bata ya bude gora ruwa ya kafa mata abaki Tasha kallon maganin takeyi kamar tace ya kara mata dan yau daya da bata taunaba batajin dadi rikeshi nayi gam ina goga fuskata saman wuyansa ina hucin zazzabi Dan nasaba alallabani kamar yada ummi takemun gashi ajirgi ma Ahukhuya ya lallabani k'asa nayi da murya, " mai sunan Abbu ka lallabani idan banida lfy lallabani akeyi na fada, ina had'e face d'inmu ina hawaye bakin cikin yama Dr Sardauna yawa bugemun baki yayi ya ingijeni " ke Dan ubankin tashi ki koma bayan mota ki kwanta yar iska jarababiya rashin tarbiyar zaki Nuna akasar Hausa jarababiya kawai zakici uwarki jikina ba na banzaye mata bane irinki naji zafin maganar sosai amma babu yada na iya saboda

ina bukatar gumi wlh har suma nakeyi idan haka ta faru banyi zuciyaba nasake dawowa jikinsa na rikesa gam ashagwab'e nace" Dr Sardauna kayi hakuri ceton raine zakayi wlh Nima idan ba doleba babu abin da zan da wannan lusarin jikin naka mai sufar mata niko na fadane Dan na bata masa azahirima bantaba ganin cikeken namiji mai cikar halita irinsaba wani Bacin raine yazo masa baisan lokacin da ya sharara mata mariba ya harbata ya matan da wata Amana janyeta ya wurgata baya " ni zan nunamiki ni Dr Sardauna bana cikin lusaran maza sai nasaki kinfadi haka da bakinki idan hakan bata faruba kice ni ba dan halak bane yau kinci darajar mahaifina amma kijirani wlh sai kinyi nadamar fadin hakan kuma daga yau bake bani idan kika sake shiga sabgata wlh zakiyi nadamar zuwanki duniya yar iska mashayiya ya fada yanama motar key ya fizgeta da karfi yana sharara gudu ransa abace yana kisama irin azabar da zai mata wacce itace ta karshe tabbas yasan daga ita bazata sake fatan shiga rayuwarsa ba Dan ya tsani yarinyar bata da tarbiya bata cikin irin mutanan da yake hulda dasu jiyake kamar ya tatara ya koma gidansa,Wanda bayada niyar hakan sai bayan yayi aure,

Naji ciwon maganganu da ya fadamun amma naji dadin yada yaji ciwon lusarin da nace masa murmushi nayi nima ina tsara yada zan Rama abun da yamun da karfi nace " Dr Sardauna na tsaneka bakada kirki yada ya karawa motar gudune yasa nayi mugun tsorata naja bakina nayi shiru Dan fah duk abinda nake masa wlh inajin tsoransa kwanciya nayi na rufe idanuna narasa mekemun dadi duniyar ma naji ta isheni amma da na tuna sati dayane zanyi sai naji farin ciki driving yake ransa abace sigari ya kunna yanasha cikin nutsuwa tunda na farajin kaurinta na kife kaina na toshe hancina ban yada yagane banason warin ba, haka dai har muka shigo garin Katsina abinda yasa ko na gane waya naji yanayi akofar wani makeken get muka tsaya yayi honr mai gadi ya bude masa ya danno hancin motar cikin gidan masha Allah duk suna tsatsaye harabar gidan parking space ya shigar da motar yai parking Mahabeer yanufo gunsu fitowa yayi gani iyayan NASA yasa ya bude mata motar ya bata hannu kin kamawa tayi ta murguda baki ta fito ai tana hango Mahabeer ta nufi gunsa tana dariya shima dariyar yakeyi ya ware mata hannayansa ta fada kirjinsa tana farin ciki Dr Sardauna ko kallo basu isheshiba ya wucesu Khalisat da ke tsaye kusan ghaisha ganin Sardauna ya nufo gun ta zuba masa idanu ta dan kallesa ta lumshe idanunta tana sabke ajiyar zuciya, gunsu Daddy ya nufa zee baby ko sai tabara takewa Mahabeer ashagwabe tace" Ahukhuya nayi missing dinka wancan mugun yayi ta dukana azaba iri iri ran Mahabeer yayi mugun baci ya kamo fuskarta yana shafawa idanunta masu mutikar haske ta zuba masa tana wani marerecewa " my zeena kiyi hakuri karki sake shiga sabgarsa kinji Rabin raina? " insha Allah my Ahukhuya na? dariya sukayi atare Daddy yace" Mahabeer kawota mana taga dangi mai ran karfe yace barni da ja'irin yaroAunty hauwa sai farin cikin takeyi jitake kamar Faisal dinne, gun jama'ar suka lso kowa kallonta yakeyi saboda tsabar kyawunta da kuma tsantsar kamar da sukeyi da Dr Sardauna kan Daddah tayi da gudu itako toni ta fara kuka ta tuno da danta Faisal rungume juna sukayi Najib dariya yake harda rike cikin Dr Sardauna ko tunda sukazo ya gaidasu dama shi ba sabgar mutane yafi shiga ba to wannan abunda zee baby tamasa yau yasa yaji yanason kara nesa da kowa shigewarsa, part d'insu yayi itako zee baby dariya takeyi tana buga bayan Daddah har tayi shiru ta saketa ta nufi gun Daddy ta rumgumeshi ta saki kuka tun karfi agigice yace momy waya tabaki cikin shashekar kuka tace" Ammin wlh ku kirasa ku tambayesa kuji azabar da yamun yau kasheni ne baiba wai ni annoba ce cikin dangi baya ko jin nauyin sunan da nake dashi gaba daya jama'ar

suka dauki salalami " aikuwa Dr bai kyautaba bakonka Annabinka ne gaskiya amasa magana ran Daddy amutikar bace ya rika waigawa inda zaiga Dr Sardauna babu alamarsa parlon suka nufa baki dayansu kafa yaran suka gudu gudun kar aturasu kiransa ya sabke akansu Mahabeer ya nufi part d'insu gun Sardauna ransa amutikar abace.....

🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️kuci GABA dabin yar mutan Niger domin kuji yada labarin zai tafi cikin wani yanayoyi da dama na rayuwar duniya Wanda Azahirima na faru

*ZEE BABY*

*DAN ALLAH KARKU FITARMUN DA BOOK WAJE*

*👉🏻7*

....kofar d'akin Dr Sardauna ya murda ya shiga da sallama ya fito daga wanka kenan daure da towel yana goge jikinsa ya amsa sallamar Mahabeer ya iso kusansa" Faisal meyasa baka tausayin Zainab yarinya cefa saida lallaba ba dukaba wlh bata da Ify tunda muka baro Saudia zazzabi take da amai amma kamata duka ko yaya take fah yar uwarka ce jinin kace bakada maraba da ita gata marainiya tunda Mahabeer ya fara magana Dr Sardauna bai kallesa ba murdaddan jikinsa ya shiga gogewa ya bude wardrobe ya ciro jallabiya fara sai kamshi take zubawa tamkar yanzu ya fesa mata turare ya saka jikinsa yaje gaban dressing mirror ya taje gashinsa Wanda yake kwance luf tamkar ka kitsa Dan Tara gashi yake tamkar yada indaiwa sukeyi ya dauki turaransa mai masifar kamshi da tsada ya fesa wlh zakace balarabene sak bai shafa mai ba" Faisal dakai fah nake magana? duk da yaji zafin abin da Mahabeer yamasa ga Wanda zee ta masa, ya juyo fuskarta dauke da murmushi " sorry my brother bazan karaba

ni nafita ma harakarta sai kayi kokarin hanata karta kuskura tashiga sabgata,nima ok? " insha Allah bata shiga ba amma ai kiné take tsoro ya zakace bazaka tsawatar mataba? baice komaiba ya dauki dadduma ya shimfida ya tayar da sallah la'asar har ya gama Mahabeer Na tsaye dan ya fahimci Sardauna yaji haushin abunda yamasa yana gamawa ya Mike wayarsa ta dauki ringing suna Daddy ya gani ya dauka yai picking ya kara akunnesa yana kallon Mahabeer ya daga masa gira " hello Daddy" dan uwaka zo yanzu ina parlo kitt ya kashe wayar " my brother karana takai muku ko? Hannusa Mahabeer ya kama suka fito suka nufi part d'insu Daddy da sallama suka shigo parlon zee baby na jikin Daddy tana matsar kwalla kusan Daddy ya zauna " Daddy gani? " meyasa da nace karka tabamun momy ka doketa momy wani irin duka ya miki? " Ammin wlh bankaremun hannuwa yayi ya daureni a karfan gadon hospital ya rika harbani wai sai yaga bayana wai ni annoba ce ya makoremun wuya saida na suma baci ba

sha haka ya barni har likintan abonkinsa saida yamun kuka saboda tausayi tunda ta fara magana Dr Sardauna bai dagoba ya kalleta har takai karshen maganar tana kuka kowa ya tausaya mata Daddy ya dagata " ke Hafeeza maza kuje tayi wanka ta canza kaya tayi sallah tazo tafadi abun da takeson ci ko wani irine yanzu za'a nemoshi momy kuje kiyi wanka nine zan rama miki karki damu dariya tayi cikin farin ciki tabi Hafeeza suka nufi bedroom d'insu cikin fada Daddy ya fara magana" Faisal nine zaka rainawa hankali ka daureta kana bugo saboda zalumci yarinyar da uwarta tabaka Amana k'asakantar da kansa yai "Daddy ayi hakuri bazan sakeba nafita harakarta insha Allah idan tayi ba daidaiba ga Mahabeer

zai tsawatar mata jikin Daddy yayi sanyi marin da yayi niyar masa ya fasa dan yasan Sardauna yanada ladabi " to naji ka kiyaye ba ruwanka da ita Mahabeer yace "Daddy tafi tsoransa ai Dole sai ana dan tsawatar mata mai ran karfe yace wannan haka yake Daddah tace" ko zata zauna part dinmu? Hauwa tace" da dai ta zauna gun yan matan ghaisha tace" hakan zaifi Aunty amarya tace" gaskiya abarmana kuma fah inaga Dole Faisal ne zai tsawatar mata Mahabeer naga bayason laifinta Daddah dariya sukayi Dr Sardauna tafiyarsa yayi dan maganarsu ko ajikinsa dan yayi Alkawalin baya shiga harakarta mutikar bata shiga tashiba Abu daya zaigani ya horata shaye shaye, suna shiga bedroom khalisat ce ta hada mata ruwan wanka taje tayi wanka tajima sosai kafin ta fito dauré da towel ta goge jikinta tas Hafeeza ta dauko mata Riga da siket na atamfa har taso tayi musu ganin karamin dinkine kuma tanada son kayan atamfa ta amsa, ta saka tayi masifar kyau atamfar ja ce anmata adon fari dinkin Riga da siket mai karmin hannu yayi mata kyau cuf ya mata da yake Hafeeza batada jiki itama amma saide kowa da irin dirinsa hafeeza ta kalleta" sister kinyi kyau sosai? " shukran bani dadduma nayi sallah shimfida mata tayi tasaka hijab ta tayar da sallah, suna zaune har ta gama ta kalli khalisat " meye sunanki? " khalisat yar uwata Hafeeza" ita na sani kece ban saniba ai ke babbace kin grimemu sosai mekike jira bakiyi aureba? kunya ta kama khalisat har hafeeza ma

mik'ewa hafeeza tayi " sister muje parlo fuska ta yamutsa " ni kwanciya zanyi ina shantocina ne ko suna gun Ahukhuya? " gasunan ajere waiwayawa tayi murna ta kamata taje ta bubude komai da ta dauko sunan har kwayoyinta da sirot dinta na kwalba gudun kar su gani yasa bata fidoba duk da tana matse karamar jakarta ce bata ganiba wayarta na ciki " my khalisat muje parlo muyi hira ko ta fadi tana kallon hafeeza tare suka fito parlon ba kowa duk sun kama gabansu sai ghaisha kade tana waya khalisat taje jikinta ta kwanta zee baby ta tureta" gani yarinya ke katuwa dake ai nima ummi tace dariya hafeeza tayi khalisat tayi murmushi " my zee zo ki kwanta to ta Mike ta matsa mata tako zauna ta dora kanta cinyar ghaisha tana waya gashin zee ta shiga shafawa zee tana murmushi ummina dawa kukeyin waya nima inaso akiramun ummina dariya su khalisat sukayi yada zee take shagwaba saida ta gama wayar ta kira lumber ummi Raiyan bugo daya ta daga da sallama suka gaisa da ghaisha taba zee baby " hello ummina wallahi nayi kewarki sosai? " Zainaba nima nayi kewarki dan Allah ki zauna lafiya da kowa kinji yarinyata? tafada tana goge kwalla" ummina insha Allah ai satine kadai zanyi na dawo gareki murmushi Raiyan tayi " ina Mahabeer dazu ya kirani mun gaisa har Dr ma baki na tabe " suna lafiya ummi sun jima sosai suna hira kafin suyi sallama taba gaisha wayar" ummi ina Ahukhuya? ya fita zai dawo kinji kai ta daga sukaci gaba da hirasu

Dr Sardauna bayan ya fita part d'insu ya koma ya canza shiri cikin kananun kaya wanda sukayi masifar kyau ya fito ya nufi gidansu Ahmed dan ya isheshi da kira yazo yamasa Allura zazzabi ke damunsa yana zuwa yayi parking akofar gida ya tura get ya shiga gidan har parlon su Ami ya shiga da sallama tana zaune" Dr ne ince mutumin ya takuraka ko? " ami babu komai dama da kullum sai nazo indai ba aiki yana ciki ko" yana part dinsa mik'ewa yayi ya mata sallama ya nufi bangaran Ahmed yana parlo sai nishi yakeyi " dallah can ragon namiji kawai tashi mutafi asibiti zama yayi kusansa ya dafa jikinsa zafi radau " Dr Wlh inajin jiki fah " tashi muje dai mik'ewa yai dama jallabiya ce jikinsa suka fito rikeshi yayi suka fita har kofar gida suka shiga mota sa hospital din Dr Sardauna suna zuwa yashiga masa gwaje gwaje ya saka masa drip da ya sha magani ganin magarib ta gabato ya shiga toilet ya dauro Alwalla ya fito " namijin duniya na tafi masallaci kai ya daga masa yana mamakin tsokanar da Sardauna yake masa yau ba shegen miskilancin sa, tunda ya tafi bai dawoba saida akayi sallahr isha'i ya dawo har lokacin drip din bata kareba ya zauna ya kira mashakurah suna hira su ta soyayya sai shagwaba take zuba masa yana lallabata" sweet baby wlh inaso na ganki amma agajiye nake yanzu ina komawa gida sai bacci " karka damu Dr nima inason ganinka amma nafi bukatar ka huta na ajiye shagwabar " ok thanks sweet bye ya tsinke Kiran Ahmed ya zuba masa idanu" ni fah Dr naga kamar son da kukewa juna yayi yawa ku ragema yan baya mana banza yamasa ya Mike ya karawa, drip d'in gudu minti biyar ta gama yacire masa, " malam ina magana fah? " banda lokacin ka " to naji wai naga da araga mana maguguna ya hada masa" Oya mutafi

tunda kaji sauki Dole ka rainamun wayo fitowa sukayi Dr Sardauna sai gaishesa ake yana amsawa sama sama Dan bacci yakeji ga baisha sigari ba tunda ya dawo daga kano,  ko amota iskacin Ahmed yayi tama Sardauna amma bai ko kallesaba bare yasamu arzikin magana har suka iso kofar gidansu Ahmed ya fito " Dr namu sai gobe idan na gama wartsakewa zanzo nama kanwarmu sanu da zuwa baimasa maganaba yaja motarsa ya tafi Dan lokaci yaja karfe kusan tara gudu yayi sosai yana zuwa yayi honr aka bude masa get ya shige parking space ya shiga ya faka yana fitowa part d'insu ghaisha ya shiga da sallama ya shigo parlon duk su hallara Ana hira zee baby na kusan Mahabeer zaune sai sangarta take zuba masa dannkwayoyin da taje yanzu taciyo aboe sun fara mata aiki shiko sa lallabata yakeyi su Daddy namusu dariya kusan Daddy ya zauna ya gaishesu " Dr Ashe baka gidan" wlh Daddy Ahmed ne ba lafiya muna hospital amma yanzu da sauki tunda taji shine danma karta kallesa ta boye kanta jikin Mahabeer dhiko baisan Allah yayi ruwantaba ghaisha tace" ayya Allah bashi lafiya Ashe shiyasa yau bai lekoba tashi kaci abunci tunda ya shigo khalisat ta zuba masa

Bayan sallah la'asar su Daddy suka tafi gidansu Nisha Daddy ya kira babban amininsa Alhaji shazali harda mai ran karfe aka tafi Alhji bashir ya tarbesu da hannu bibbiyu bayan sun gama gaisawa ne Daddy yayi gyaran murya yace"Bashir abinda ya kawomu Akan maganar Aisha ne da Faisal yace ita yakeso kaddara ta rabashi da wacce zai aura to da nace yasamo wata yace Aisha ya zaba wai harma yazo sunyi magana shine nace to bari muzo kar muyi k'asa agwiwa Abu na gidane mairan karfe yace "idan babu damuwa Bashir munaso atsayar da magana munzo neman aure Bashir k'asa yayi da Kansa cikin jin kunyar surikin NASA yace" to madallah ai duk Abu na gidane tunda har sun daideta banida ja bari na kira Alhaji yanzu mik'ewa yayi ya fito yana farin cikin abun dama shi yaron da Nisha take so bai bawani kwanta masaba parlon ya shigo da sallama umma Hauwa na zaune Nisha na jikinta akwance ta Mike hayatu na zaune yana waya zama Bashir yayi yana kiran waya Babban Wansa ya kira yake sheda masa komai cikin farin cikin yace gashinan zai zo ya bada auran Aisha cikin jin dadi ya kashe wayar Hauwa ta kallesa" Alhaji bangane ba fah ta kalli Nisha wace tayi tsuru tsuru da idanu sai kif kif take da idanu Bashir yayi dariya ya kalli Nisha"Aisha kinason Dan uwanki zaki aureshi ko? kunya taji ta rumgume Hauwa ta boye kanta tana daga kai Hauwa tace"ikon Allah Bashir ya warware mata duk yanda akayi har zauwar Sardauna gun Nisha zauwar Dan uwansane yasa ya Mike ya koma gunsu Daddy suka nemi auren Aisha Mamuda ya basu har sadaki Saminu ya bayar nera dubu dari nan take mamuda ya amsa aka tsayar da ranar aure daide da na mahbeer kwana ashirin da bakwai yau daide yayi saura kowa agurin farin cikin yake da wanan Abu mahbeer ana gamawa ya Mike ya shigo ya gaishe da hauwa wacce itama tayi farin cikin sosai sai waya take da kawaye da abokan zama suna tayata murna irin wannan Abun Alheri kai tsaye da Allah ya kawo hayatune yasa nisha gaba yana zagi "Dan ubanki kika yarda aka hadaki da wannan mugun Dr Mara imani zakici ubanki shegiya karaf akunne mahbeer hayatu na zagin Dr Sardauna kuma yasan dalilin zagin da sallama ya shigo Nisha na ganinsa ta Mike ta taresa ta rike hannusa "Oyoyo bro dariya yayi "Amaryar mu aban goro sakin hannusa tayi cikin kunya ta ruga daki da gudu ta boye kai ya girgiza ya zauna kusan umma dariya umma tayi " mahbeer kasa kanwarka jin kunya kaga masifafan da ya takurata tun dazu mik'ewa hayatu yayi yabar parlon ko kallo bai ishi mahbeer ba Dan yaji zafin zagin da yama Sardauna dama yanada

haushinsa murmushi mahbeer ya saki" umma ina yini " lafiya lau ina momy kai ya Sosa na barota tana bacci yau rigima takeji dariya umma tayi zatayi magana wasu mata uku suka shigo da sallama mahabeer ya Mike "umma suna jirana na tafi "to zanzo gidan zuwa dare dariya yayi ya fice a bakin get ya samu su Daddy sun fito suna shiga motar Nuhu da sauri ya karasa mairan karfe zai shiga mota ya rikeshi yana tsokanarsa sandar hannusa ya kwada masa dariya mahabeer yayi ya sakeshi ya gewaya mazaunin direba ya tashi motar ya mata key yabi banyan motar su Nuhu get aka bude musu suka fice.................. ✍🏻

*💖💖👩🏻‍🦱ZEE BABY👩🏻‍🦱💖💖*

*DAN ALLAH KARKU FITARMUN DA BOOK WAJE*

*👉🏻29*

....saman titi Mahbeer ya harba motar cikin nutsuwa yake tukinsa hankalinsa kwance yake sharara gudu yana tunanin zee dinsa ko ta tasho tayi sallah kawu saminu na masa hira dariya kawai yake hankalinsa kwance yake driving dinsa ya dauki hanyar kofar Marusa lowcos, Nisha ko tunda ta shige bedroom ta fada saman bed ta lumshe idanunta tanajin wani irin dadi tamkar dama tanaso haka ta tsinci kanta afarin ciki sai juyi take tana sakin murmushi ko me ta tuna ta zabura ta bude idanunta ta dafe kirjinta"wayyo nashiga uku Yaya Sardauna tsama fah gareshi gashi inajin tsoronsa ya zanyi zama dashi mahafus zaice naci amanarsa murmushi tasaki "to ai Dr yacemun nasaki jikina dashi nabar tsoronsa bazai dokeni ba Sorry mahafus ni Dan uwana zan aura ta fada tana kwanciya rigingine ta shiga duniyar tunani batasan lokaci yajaba saida taji hassan na kiranta"Aunty kizo Abba na kira mik'ewa tayi tana turo baki"wlh idan karyace zaka sani tare suka fito Bashir yace"Aisha zo mana kusansa ta zauna cike da kunya tana sunne kai "Abba gani? " yauwa Aishatul humairah ga kudin sadakinki nakine halak malak kiyi yanda kikeso ya kamo hannuta ya Dora mata "kai Abba Allah ni ba ruwana ku rike na Baku kai da umma bari na dauki dubu biyar nasha ice cream ta zagi dubu biyar ta ajiye sauran cinyar Abba ta Mike da gudu tayi d'aki dariya abin ya basu shida Hauwa da kallo suka bita har ta shige hayatu ko sai zabga Mata harara yake

bangaran su mashakurah bayan sun koma gida iyayan babu Wanda ya shiga sabgarta bedroom ta shiga ta fada saman bed ta fashe da kuka tana nadama da danasani ga son Dr Sardauna kamar ya kasheta jitayi ta tsani bandar arayuwarta da bai shigo rayuwartaba da hakan bata faruba da babu mai rabata da Sardauna Miji na kerema sa'a yayarta takira tana fadamata duk abinda ya fara tsabar rikita da takaici da mamakin abinda mashakurah ta aikata yasa ta tsinke kiran kukan mashakurah ya karu rana zafi inuwa k'una lalai ta kira tazo su yanke shawara mai fitar dasu amma tana zuwa iyayan mashakurah suka hanata shiga gunta shiyasa yau ta wuni cikin kunci da ta kura sai kuka take tana nadamar

aikata zina arayuwarta,

✨✨✨✨✨✨✨✨

khalisat ce zaune ta rabka uban tagumi ta rame tayi baki sai abkin kuka tana kiran Sardauna Aunty amarya na hango itama tayi baki ta rame sai wasu kuraje da suka fara fito mata ta nufo gun khalisat "wai keba zakiyi tawakali ba kiyi hakuri ki amshi kaddara ki cireshi aranki tunda duk inda mukaje sai ace babu aure tsakaninku amma ai nace miki kiyi hakuri har wa'adin da boka kafi madubi ya daukarmun idan yacika mukoma mugani zai sake mana sabon shiri kallon uwar tayi ta fashe da kuka"wlh momy duk kece kika jawo mana muna zaman zamanmu da mutane masu mutumci son zuciya yasa kika aikata abundan muka aikata gashi munyi biyu babu ke babu ni babu Aunty amarya kanta da tasani takeyi Mara anfani. kukan itama ta fara ta rumgume yar tata tana bata baki akan zasu koma insha Allah tayi hakuri ita inna kallansu take ta rabka ta gumi Dan tasan duk laifintane itace bata Dora mariya atarbiya ba ta koya mata son abin duniya da da mugunta da makirci har itama ta Dora yarta a turba Mara kyau Allah ya kyauta yasa mufi karfin zuciyarmu Amin ya Allah

Mahbeer suna zuwa gida su kawu saminu suka shiga motcinsu suka nufi gidajamsu mahbeer ko part d'in Daddah ya nufa yana tsokaransu, Sardauna bayan ya dawo daga sallah ya cire jallabiyar jikinsa ya kwashi wayoyinsa ya dauki kwalin sigari da lemo gudu biyu ya fito ya nufi swimming pool can nesa da ruwan ya zauna gun wash gugayan kujeru ya zauna yana shan sigarinsa yana kallon ruwa zee suna zaune a parlor tana jikin umminta ghaisha na tambayarta"momy fushin me kikene? baki ta turo "ummina yo ba ummi bace tace wai na tafi Swimming pool da abaya dariya ghaisha tayi "yi hakuri kinsan fah akwai ma'aikata yan aiki da masu gadi zasu ganki kibari da kun karya kwanar sai kicire murmushi ummi Raiyan tayi tana shafa kan zee da take turo baki hafeeza ce ta fito da katon hijab cikin ko yar mitsitsiyar rigace ta wanka ta Iso "sister tashi mutafi mik'ewa zee baby tayi tana kallon hafeeza "sister ahaka zaki? murmushi tayi ta janye hijabin dariya zee tayi ta ce"ummina yanzu na gano dariya suka musu hafeeza ta kama hannu zee zasu tafi ummi tace"baby kawo wayarki karki sakata ruwa "ummina pic zamu dauka ta fada suna ficewa daga parlon anutse suke tafiya aikuwa inda sukabi suka hadu hashim me wanki da isah mai ba shifkoki ruwa suna karya kwana zee ta cire Abayarta da gudu ta nufi gun ta ajiye abayarta saman kujera hafeeza ta iso ta cire hijabinta ta ajiye zee ta zauna hafeeza tace" tashi muyi nutso tare kafada zee ta makale "jeki ba yanzu ba zanyi jeki zanyi pic ne da gudu hafeeza ta nufi gun ruwan ta tsunduma tana nutso zee tayi tsaye tana daukar hoto iri iri wani

tayi murmushi wani ta turo baki wani tayi dariya duk abinda take Sardauna na kwance saman kujera na kallonta kai ya girgiza ya lumshe idanunsa yanajin wani irin feelings yada surah jikinta ta baiyana tsaki yaja ya bude idanunsa ahankali kamar bayason magana yace "zee baby karaf akunneta idanu ta fara rarabawa tana neman Sardauna Dan taji muryasa shagwabewa tayi tana turo baki"Yayana naji muryarka kana ina please ka fito wlh tun d'azu nakejin kamshinka Yaya Sardauna dabas ta zauna tana kallon hafeeza wacce take wankanta cikin kwanciyar hankali

lallausan murmushi ya Saki Dan yasan bata ganshiba sake kiranta yayi ta shiga waige waige mik'ewa tayi ta nufi gun kujerun da Sardauna yake kwance Dan tabbas taji ajikinta yana gurin yana ganin ta nufo gun ya lumshe idanunsa "Yayana kana inane ta fada tana isuwa gun ta gansa akwance "Yayana shiru ya mata ahankali ta karasu gunsa ta duka gabansa gwiwowinta ak'asa ta riko hannusa "Yayana gani bude idanunka Ify kuwa shiru taji kuma taga kamar baya motsi girgizashi tana kiran sunsa "Yayana ka tashi mana meyasa meka ko bakada Ify yaufa kai angone Daddy ya kira ummi ghaisha yace anyi Sadakinka da Nisha ansa ranar aure daidai da namu da ya mahbeer kwanaki kadan suka rage Yaya tashi kabani gorona namaka zaben mata wlh kun dace najini ina farin ciki duk da bamu shiri dakai amma na zabama ka mata kayarda zaka aureta Yaya Sardauna naji nabaka daraja mai girma nagode kuma insha Allah ni dakai bazamu sake fadaba ai kaima bazaka dokeniba ko angon Yayata Nisha ta fadi tana dariya tana leken fuskarshi shiru bai bude idanuba sai taga kamar yana kokowa da numfashinsa da karfi karfi arikice take zizigashi tana kiransa "Yayana Sardauna menene bude idanunka kaji tashi tayi ta lallaba ta kwanta saman kujera ta rumgumeshi ta fashe da kuka ta had'e face dinsu"Yayana menene don Allah kabude idanunka ko mutuwa dai kayi sauran Dan kuzarinsa da ya rage ya tataro jarumtarsa ya bude idanunsa ya zuba mata idanu hawayenta na zuba saman bakinsa yana lashewa ahankali naji ankira sunana Wanda na rasa nutsuwa nan take na rude fuskata

na janye na kallesa ina shashekar kuka "Yayana wai meye yasamaeka ina baka labarin matarka kayi banza dani zaune ya Mike yajanyoni jikinsa ya kamo fuskata ya zubamun tsumammun idanunsa masu fitar dani haiyaci"my Kanwas mutikar kinaso mushirya dake maza ki hadiye kukanki kimun shiru idan ba so kike ciwon zuciya ya kamaniba da Sauri na dora hannuna saman bakinsa ina girgiza kaina"Yayana wlh na daina kuka daga yau karkayi ciwon zuciya please angon Nisha kaina ya tallabo ya Dora harshensa yana shanye hawayena saida ya shanye tas ya sakeni jikina yayi sanyi jikinsa na koma na tura kaina kirjinshi ina sabke ajiyar zuciya shima rumgumeni yayi gam yana sabke ajiyar zuciya munjima ahaka mun makale juna can naji yace"My Kanwas kin tabbatar Nisha zata soni ni mutumne Mai son asoni sosai abani kulawa anunamun love zata iya wani irin k'ululun bakin ciki naji ya turnukeni amma na daure tunda banida dalilina na hakan

jikina na janye na matsa nesa dashi na kamo hannusa na rike "Yayana wlh zata soka sosai ma kaima kabata kulawa please Nisha ba ruwanta kaji yayana na fada ina langwabe kai ina sakin murmushi "gud My Kanwas nagode ya fada yana kamo yatsata yasa bakinsa yana tsotsa wani irin feelings ya tasomun ashagwabe nace"Yayana bakajin tsantsanin hannun hagumne fah na fada ina dariya zan zare ya ki Saki ya sake salon tsotsar idanu na zuba masa"Yayana please kabari mana zanyi kuka gira ya dagamun ya turamun yatsarsa abakina na kallesa gira ya dagamun alamar na tsontsa cizo na gantsara masa da karfi amma yaki cirewa na Kara masa wani cizon na cire yarsar bakina ina dariya cizona shima yayi da karfi na Saki ihu na fashe masa da kuka ina yarfa hannuna face ya hade" wlh idan kika bari hawayenki ya zubo k'asa sai kin raina kanki ni da kika cijeni fa wa nama kuka shiru nayi na hadiye kukan hannu ya rike yaga san hakoransa sun fito iskar bakinsa ya shiga huramun ya saki hannun"ina wayarki? " gatacan " jeki dauko mik'ewa nayi na nufi inda kayana suke idanu ya zuba mata da sauri ya rumtse idanunsa ya dafe kansa saboda tafiyarta kadai zata tadama namiji hankali bare kayan jikinta da

yanayi zubinta da Allah yamata gata de yar siririya ce doguwa amma akwaita hips d boobs masu daukar hankali hafeeza ta gaji da wankan tana zaune tana ta daukar pic na iskota ina murmushi "sister ina kika buya ko kece na hango can? "eh gun Yayana nake bari na kai masa waya nazo nayi wanka hafeeza hanata tayi taci GABA da daukar pic daide lokacin,

Mahbeer ne ya shigo parlonsu yana neman Sardauna ya masa albishir bai gansaba ya nufi d'akinsa yaji arufe fitowa yayi yana nemansa yasan irin wanna lokacin yana Swimming pool can ya nufa lokacin zee ta gaji da iskancin hafeeza kokowa suka fara tayi nasara warce wayar ta ruga da gudu ta nufi gun Sardauna tana dariya mahabeer ya hango zee babynsa da wanna Riga mai masifar kyau yar guntuwa zai bita yaga hafeeza tana saka hijabi ya nufo gunta "ke dan ubakin haka tsirara kuke yawo dan kin ganni zakisaka hijabi ina ne zee ta nufa ahaka idanu hafeeza ta fara cicirawa "bro ai cemun tayi gun Yayanta zata nazata kaine to ko gun yaya Sardauna ne idanu ya zaro "kina nufin ahaka tazo?? "A,A ga rigarta nan dauka rigar yayi ya nufin gunsu zee ko tana zuwa ta zauna kusan Sardauna tana dariya"Yayana ga wayar shakota yayi ransa abace"wai dan ubanki haka kika fito daga part d'inku ya fada idanunsa sunyi jajur tsoronsa ya kamani kai na girgiza"Yayana wlh da abaya na fito tana can a ajiye Yayana ka shakeni sosai fa sakina yayi idanu na zuba masa yada babban kirjinsa ke sama da kasa hannuna na dora kan kirjinsa "Yayana kafiye girma masha Allah Yayana babban yarone mai tsada na fada ina sakar masa kiss saman faffadan kirjinshi mai yalwar gashi wani farin cikine ya mamaye Sardauna duk da bai taba mata murmushi gaba da gaba ba sai da ya subce masa itama murmushi tayi ta cire hannuta saman kirjinsa kamo fuskata yayi ya had'e face d'inmu muna shakar numfashin junanmu cikin wata iriyan murya yacemun" my Sweet zee wlh kinfini haduwa kedin babbar yarinyace danya sharaf mai tsadar gaske ya fada yana lasar idanuna ashagwabe nace"wayyo my Sardauna kabari mana kiss ya sakarmun saman idanu yana sakin murmushi ya dago ya tallabo kaina ya daga bakina yana huramun iskar bakinsa wani kamshi nake Shaka muna kallon juna sai ji nayi ya zubamun yawu ya rufemun bakina yana murmushi "Oya My Kanwas hadiye fuska na kwakwabe " OK bani abuna tunda bazaki Shaba hadiyewa na ina lasar baki "to yayana na hadiye na fada ina riko fuskarsa "Yayana tsaya meye saman idanunka mugani cikin dubara na bude bakinsa Nima ina hura masa iskar bakina na kakalo yawuna na zuba masa abaki na rude masa bakinsa ina dariya sai naga ya hadiye yana murmushi gira na daga masa "wayyo Yayana namaka wayo kasha yawuna kafada ya dagamu "My Kanwas bani wayar mana "to Yayana ga wayar"gud My Kanwas bani number Humaira da sauri na kallesa "yayana wacece haka kuma ni banida na fada cikin tsiwa zan Mike ya rikoni ya mannani da jikinsa ya kai bakinsa kunnene cikin tatausan lafazi yace"My Kanwas Nisha nake nufi ya fada yana shafa gashin kaina cikin sanyin jiki na janye jikina ina murmushi karfin hali na bashi wayar "gashi yayana zaka ga nasaka My dear amasa yayi ya duba babu security ya shiga ma'adanar lambobi yaga number nisha wayarsa ya dauka ya kwashe number Nisha yayi dailing number tana ringing ba'a dauka ba har ta katse ya sake kira zee baby idanu ta zuba masa zuciyarta na mata zafi amma ta boye damuwarta "Yayana bata dagaba ne bari na kirata nace kaine Kiran har ya kuma katsewa bata dagaba zee ta kirata bugo daya ta daga"my dear amaryarmu Yayane fa yake kiranki baki dagaba daga can Nisha ta zaro idanu"wayyo my dear wlh ban saniba ai to kibani shi idan kuna tare zee saida ta rumtse idanunta "OK my dear ido ta bude ta kalli Sardauna yana fama latsa waya tace"Yaya Sardauna amshi Aunty Nisha nason

magana da mijinta kallona yayi na sakar masa murmushi amsa yayi ya Kara akunne"hello Amarya ya kike daide lokacin mahbeer ya iso gun ransa duk abace ina ganinsa farin ciki ya kamani daman neman yada zanbar gun nake cikin farin ciki nace"my heart zo ka kamani mutafi jiri nakeji wanka zanje nayi Yaya Sardauna na kawoma waya suna...ban idasaba ya fisgoni na Mike tsaye saida nasaki Kara"wayyo my heart wlh hannuna naji zafi da Sauri Sardauna ya dago kai ransa amutikar bace saboda fizgar da mahbeer ya mata yajita har ransa amma ya kauda kai yaci gaba da amsa wayarsa jikinsa ya matseni yana sakamun abayar hannusa Wanda niko hanklina gabaki daya yana gun wayar da Sardauna yake da Nisha muryar mahbeer ta dawo dani yana mun magana afada fada ya matseni gam "wlh my zee babyna Idan............... ✍🏻

*Gidan kudi yauwa ina bara comments don Allah saboda naga sarautar taku ta motsa sai yan kalilan sukeyi 🤣to yau na roka comments da sharhi Nasaka mukarama labari sugar amma idanu munji shiru sai na dauka ko bakujin dadin labarine🙄🙄🙄*

*💖💖👩🏻‍🦱ZEE BABY👩🏻‍🦱💖💖*

MALLAKAR  UMMU FAREESA NE

*DAN ALLAH KARKU FITARMUN DA BOOK WAJE*

*👉🏻30*

...."kika sake fitowa ahaka sai na bata miki rai gida cike da maza zaki rika fita ahaka "yo my heart  ai babu Wanda ya ganni fah sai Yaya Sardauna kuma ni yaya mahbeer kabarmun fada Allah ni banason fada sai Karina min fada jifa hannuna kajimu wayyo Yaya Sardauna kagani my heart yajimun ciwo ko? "yi hakuri my zeena zo mugani janyeta yayi ya kamo hannuta suka zauna kusan Sardauna ya kwantar da kanta kafadarsa ya rike hannuta "Dr ango kaji zainab tana kullamun Sheri wai na jimata ciwo ya fada yana murmushi yana murzawa zee baby hannuta Sardauna dagowa yayi Wanda ransa yayi mugun baci ya danne yama Nisha sallama yace Zai kirata da dare ya kalli mahbeer yace"my bro kaima naga irin fisgar da kamata ai kashinta bai kwarin da zaka fizgeta hakaba sai kajimata ciwo zee najin haka Sardauna ya daure mata gindi ta b'are baki ta fashe da kuka tana bekama Sardauna hannunta ya riketa ransa wani irin mugun baci yayi kwashe wayoyinsa yayi ya Mike yabar gun mahbeer yace"Dr Namu ka tsaya kaji labari mai dadi bai juyoba yace" toilet zan shiga zamuyi maganar anjima ya tafiyarsa dukansa zee ta fara tana kuka"to ni sakeni na tafiyata wlh ba ruwana dakai tunda ka kori

Yayana gashinan kajimun ciwo daket ya riketa  ya shiga lallashinta  yasamu tayi shiru tana zumburo

baki saida ya lallabata har ta sabko ta Saki ranta ya jata suka nufi gun ruwan abayar ta cire taba mahbeer ya rike mata tana dariya "my heart naje nayi wanka ta nufi ruwan da gudu ta tsumduma mahbeer na zaune sai murmushi yakeyi yana lumshe idanu yana jinsa a farin ciki zee nutso kawai take ruwan saboda ta iya ruwa sosai idan tayi nutso ta gaji sai ta leko a kirayi mahbeer tana dariya shima dariya yake mata sai takoma yay yay da ita ta fito sutafi taki saida taji Ana kiran sallah ta fito gashinta har gadon baya na tsagar da ruwa mik'ewa yai ya taro ta ya rikota yana goge mata gashinta da mayafin abyar tana dariya ta shafi fuskarsa"my heart ina sonka murmushi ya Saki ya saka mata rigarta ya yane mata kanta da gyale ya mata kiss agoshi "nima ina Sonki ina kaunarki wlh bazan iya rayuwa babu keba rumgumesa tayi tana dariya" nima wlh Yayana ina Sonka ina alfahari da kai janyeta yayi ya kamo hannuta suka nufo cikin gida daide part d'insu ya Saki hannunta "my zeena alwalla zanyi na tafi masallaci dariya tayi ta wuce part d'insu shima ya shiga part d'insu akofar get sukayi Karo da Sardauna ta dago da Sauri face ya had'e ta tare hanyar ta marerece fuska"Yayana ina wayata hannusa yasa ya matsar da ita bai kalleta ba yace"tana gun ummi zatayi magana ya buga mata wata uwar tsawa jikinta na rawa ta shiga ciki da gudu tsaki yaja ya tafiyarsa tana shiga ta wuce bedroom ta cire kayanta ta daura towel ta shiga bathroom saida tayi wankan tsarki saboda rumgumar da Sardauna ya mata ta zuba sosai tana fitowa

ta saka Riga da siket yan kanti rigar mai dogon hannuce ta fesa turare ta fesar da gaahinta ta shafa mai ta daureshi da ribbon ta saka hijab ta hau darduma ta tayar da sallah hafeeza ce ta shigo itama ta dauro alwalla ta tayar da sallah zee ko da ta gama bata tashiba zaune take tana hailalah da salatin Annabi hafeeza ma zaune take tana karatun Alqura'n mai girma har aka kira sallahr isha suka Mike sukayi atare suna idarwa zee ta tashi ta cire hijabin ta nufi D'akin ummi tana zaune kan darduma tana Addu'a hawaye na zuba saman fuskarta jin motsin zee yasa tayi saurin gogewa ta shafa fatiha ta Mike ta kalli zee tana zaune bakin gado wayarta ta dauko"ga wayarki inji Sardauna amsa zee tayi tana jujuya wayar ahannuta tanajin kamshin Sardauna jikin wayar ummi ta zauna ta rumgumo zee "zainaba kinada damuwane? dariya zee tayi"kai ummina wlh babu abinda yake damuna ummina murmushin farin ciki tayi zee ta budewa umminta kai" wow ummi kizo nayi miki kitso mana ko Dan bazai kitsu ba ta fada tana warware gashin Wanda tsayinsa ya wuce mazauninta dariya ummin tayi tana ma zee dukan wasa "sakarmun gashi hirasu suke cikin so da kauna hafeeza tashigo da sallama "ummi ghaisha na kiranki murmushi tayi "to ganina zee tashi muje kici abunci rumgume ummi tayi"to ki goyani janyeta tayi ta Mike tsaye ta daure kanta ta kama hannu zee suka fito tana mata rigima sai ta goyeta dariya su Daddy suka musu kan dining suka nufa Sardauna na zaune yanacin hadin salak da akwai Daddy yace kaga Dan gatan ghaisha kallonsa zee tayi ganin fuskarsa ahade ta kauda kanta ghaisha tayi serving d'insu mahbeer ne ya Iso yana dariya ya nufi gun Sardauna ya zauna yasa hannunsa cikin plate din "ango baka bani gorona ba fah? " murmushi Sardauna yayi "bro zan baka karka damu Daddy yace "yauwa idan mun gama

cin abuncin zamuyi magana kunga Abu ya gabato suka amsa da to zee ta kalli mahbeer "my

heart ba ko magana ko? " zo muci salak akwai dadi" Allah Ya mahbeer to bari nazo naci ta Mike tana kallon Sardauna ido suka hada wani irin abu ya sokeso atare wani mugun kallo Sardauna ya watsama zee da nunin karta kuskura tazo dabbas ta koma ta zauna Dan ta gano kashedinsa baki ta murguda ta hararesa taja tsaki ta kauda kanta tanajin wani irin yanayi na baibayeta Mahbeer yace ya kika fasa zauwa? cikin sanyin murya tace "Ya mahbeer banaci ne Sardauna spoon d'in ya ajiye cikin plate ya mike ya dawo parlo sude iyayansu abuncinsu sukeci mahbeer yayi yay da zee tazo taci salak taki dam Sam ya fice mata arai abuncin kadan taci Dan bata fiye cin abunci sosaiba da dare surutu tayi ta zuba musu har suka gama suka dawo parlo Sardauna na zaune yana waya da wani Dr da yake Abuja Akan yazo Abuja gobe zee tana jikin umminta kwance Sardauna na gama wayar Daddy yayi gyaran murya yace"yauwa dama abinda nakeso daku shine maganar lefene

Kai Faisal nasan aiki aiyuka sunma yawa Mahbeer kaine zaka jagoranci tafiyar kaida ummi Raiyan da khadija zaku tafi Dubai ku hado kayan lefe da da kayan daki da gadaje har na Aisha nine zan mata komai ya kasance kun musu iri daya kamar yada gida janku yake iri daya to hata kayan da za'a zuba agidan ma ya kasance iri daya akwatina ma iri daya komai yazama iri daya dama na gama shirya koma jibi idan Allah ya kaimu zaku tafi momy sai muyi zaman mu ni dake da hafeeza har su dawo ko? " wayyo Daddy atafi dani please sai nazabo komai Dan Allah Daddy na fada ina son yin kuka ummi tace"nafa San halinki idan munje bazaki barni nasake ba nayi abunda ya kaini ba kukan shagwaba na saka mata na Mike na nufi bedroom Sardauna da kallo ya bita yana lumshe idanunsa zuciyarsa na bugawa Daddy yace"ko atafi da ita sai tazabi irin abubuwan da take so ummi tace"abarta wlh bazata barni na sakeba yanzu zan shiga na lallasheta zata hakura murmushi Daddy yayi
Sardauna gun ghaisha ya dawo ya zauna ya kwantar da kansa cinyarta kansa ta shafa masa "Autana ya dai Mamana gobe zan tafi Abuja insha Allah amma kwana biyu zanyi ko uku "Allah ya kaimu ya.kaika lafiya ya bada sa'ar aikin da akaje yi Daddy yace"ni bazaka fada munba tashi yayi ya koma gun Daddy ya rumgumesa "sorry my Daddy dariya sukayi mahbeer yace"Dr Sardauna namu wai bazaka bani gorona ba murmushi yay ya kallesa "Allah bro kafiye takura yo ni goro gareni kuda kukaje kuka kai kudin auren kukasa ranar aure ai Kane zaka bani goro ko Daddyna ya fada yana rumgumesa Nawwara da nanah dariya sukayi suna kallon Sardauna harara ya zabga musu ghaisha tace ka firgitamun yara mahbeer yace"au haka kace ko gira Sardauna ya daga masa yana dariya ya kalli ummi "ummi kije zainab fah na kuka ita daya ki lallasheta dariya mahbeer yayi "eh lallai tama zaben mata ummi mik'ewa tayi tamusu sallama ta nufi bedroom d'insu zee hira suka taba kadan Sardauna ya Mike ya musu sallama Dan da Asubah yakeso ya kama hanyar Abuja mahbeer ko yana nan suna tattauna yada komai zai tafi atsari sai karfe kusan shadaya ya tafi part d'insu ummi da ta shiga

zee na kwance har tasaka kayan bacci taci kwayoyi kwallaba daya ta shanye ta sirot dama ita daya ta rage mata hafeeza ta tambyeta meye Tasha tayi banza da ita Dan yan isakan sunzo kanta akwance ummi Raiyan ta iskosu murmushi tayi isowa bakin gadon tayi ta dauketa cak kuka ta saka mata "ummina wlh ni saukeni nayi fushi ta kalli hafeeza"diyata kiyi hakuri natafi nayi lallashi tare zamu kwana shiru zee tayi tayi lamo jikin ummi dakinta ta nufa da ita ta kwantar da ita cire abayar jikinta ta shiga bathroom tayi wanka ta fito ta saka kayan bacci ta

hayo gadon ta rumgume yarta da take kukan sangarta ba hawaye Dan kwayoyin sun fara aiki"zainaba yi shiru yar autata bari namiki waka mai dadi waka ta fara mata akunnanta ta larabci kunsandai balaraba da zakin murya tana shafa gashin kanta tun tana turjewa, har ta tsaya tayi shiru tana sauraro tayi lamo jikin ummi bata jimaba bacci ya dauketa abinka da tayi shaye shayenta ummi bata bariba saida taga baccinta yayi nisa Addu'a ta tofa mata taja blanket ta rufesu Dan itama so take tayi baci ko ta farka cikin dare tayi sallah tana rumgume da yarta har bacci ya dauketa hafeeza tana dakinsu ita daya itama tayi bacci rashin zee baby dama itace ke hanata bacci da wuri sucika dare suna hira can dare ta gudu gun umminta ta kwana,

Sardauna yana zuwa wanka yay yayi shirin kwanciya yayi sallahr nafila raka'a biyu ya jima zaune yana Addu'a ya Mike ya cire jallabiya ya ballo maganinsa yasha ya fada saman bed yaja blanket ya rufa jikinsa yana juyi har bacci ya daukesa koda mahbeer yazo lokacinma Sardauna yayi bacci shima wanka yayi yay shirin bacci ya kwanta amma yay cikin wuya yayi bacci sha'awar zee dinsa ta adabeshi ga tunanin zai barta yayi tafi wacce yasan zasu kusa sati haka yayi ta juyi har yayi bacci bangaran Nisha tunda Sukayi magana da Dr Sardauna muryasa ta dimautata ta gigitata don bata taba wata magana ta arziki dashiba sai yau kwance take saman gado sai juyi takeyi motsi kadan ta kalli wayarta Dan yace zai kirata zuwa dare sai lumshe idanu take Dan bacci takeji gashi ya Mata kashedi baya kira aki daukan kiransa haka dai har bacci ya kwasheta cike da begen Sardauna Asubah ta gari,

**************************************

*agurguje bayan sati uku*

Bayan wannan lokacin abubuwa daya sun faru harda zuwansu ghaisha da ummi Raiyan da mahbeer Dubai Wanda suka dauki tsawon sati guda sun hado kaya na kece reni gadajema iri daya aka sayoma zee baby da Nisha haka akwatuna ma iri daya da kayayakin sawa hata kayan kitchen d'insu iri daya saida suka kwashe kwana bakwai cur suka dawo zee ton washe garin tafiyarsu ta koma gidan Nuhu can Nisha take iskota suna hira Sardauna shima baya gari saida ya dauki kwana biyar a Abuja rashin zee baby ya adabi rayuwarsa kamar yada itama rashinsa ya dameta har zazzabi tayi amma tasama zuciyarta hakuri bangaran Sardauna da Nisha ba laifi yana kiranta suna Dan hira amma ba sosai ahaka dai har suka Dan shaku tun bayan dawowar su mahbeer daga Dubai su ghaisha da ummi suka shiga ma zee gyaran jiki na uban mamaki cikinta da waje gyarata suke dan sun b sayo kayan gyaran amare iri iri magani kala kala nasha sai banka mata suke da murjeta da turaruka iri iri yanzu ko parlo sun hanata zama Dan ko mahbeer ghaisha ta hanashi ganinta Dan so take zee ranar auranta ta fito matakar tauraruwa cikinta da bai dinta Dan jinta take tamkar ita ta haifeta ba surukaba zee amugun takure suke daga ita har Sardauna cikin dubara Sardauna da yaje gun Nisha ya amshi wayarta ya dauki number zee baby ya kirata ta gane shine amma saboda yan iskan suna kanta ta fitsareshi tace idan yasake kiranta sai ta hadashi da mahbeer haushi yasa ya tsinke kiran bai sake kiranta ba tayi kukanta har tagaji sai Akan dining suke haduwa idanunta kade ake gani cikin katon hijab take fitowa harda niqab aikin ghaisha ne wanan canma bangaran Nisha umma ba karamun gyara take mataba ciki da bai bayan zauwasu da satine aka kai kayan Nisha akwatina 12 shake

da kaya iri iri masu tsada nagani na fada Wanda ya burge kowa Nisha ji take tafi kowa, sa'a aduniya yan makarantarsu Nisha ma sun zuzuta kanyanta sosai da mijinta na tserema sa'a haka zee baby duk iri dayane aka musu ita da Nisha zee sosai komai na kayanta ya burgeta yada taga mahbeer ya mata taji dadi sosai dangi kowa ya yana yabo ummi Raiyan har kukan farin ciki tayi aboye bangaran Aunty amarya Abu ya lalace mata Dan ajiyane taje gidan boka kafi maduba ta iske babban bala'i kafi madubi ya kumbura ya tsage gida biyu  wani irin ruwa baki da manya tsotsotsi na fitowa jikinsa ai wani irin ihune ta Saki ta fita aguje tana so she so she kurajen jikinta sunyi budur budur duk inda ta Sosa sai ruwa wani baki ya bultso mai wari haka tabi titi tana gudu tsautsayi wata mota saman titi ta bugeta take ta samu karaya uku direban ya gudu bai tsayaba saida takusa wuni gefen titi ayashe ta suma daket aka samu wasu maga Allah suka dauketa sukayi hospital da ita rayuwa kenan Asiya ma kawarta aranar mijinta ya mata Saki uku da Dan banza duka saida ya karya mata kafa da hannu ya janyota kofar gida ya rufo kofar haka yara suke taruwa akanta suna mata ihu daket tasamu wani Dan shaye shaye ya kirawo mata adedeta ya cicibeta sukayi gidansu dagacan sukayi hospital,

✨✨✨✨✨✨

yau ya rage saura kwana uku daurin aure An shiraya ma Nisha dakinta tsafa a Narkeken agidan Dr Sardauna  Wanda ya hadu tamkar gidan turawa Wanda yake unguwar, barhim estate kitchen dinta kadai abun kallone, ginda ya hadu iya haduwa haka dakin Dr Sardauna da Nisha, ya hadu Dan shima, komai sabo ya zuba abangaran sama da, kasa, Dan kayansa sunfi na Nisha tsada shi komai NASA kirar Italia ne yazuba sama da k'asa duk inda yayi sha'awa zai kwanta sab'anin Nisha kasa take wlh idan kashiga gidan kace bazaka fitaba yada, zee baby taji Family su na yabon irin yada gidan Nisha ya tsaru har kuka tayi abarta taje ghaisha ta hana itama nata gidan akayo video aka kawo mata saboda kusan komai iri dayane sai ban bance ban bance saboda gidajan ajere suke iri daya ne saide kowa da yanayin gininsa amma gaskiya gidan Sardauna yafi haduwa nesa ba kusaba shi harda Swimming pool tafkeke da rumfar shakatawa gashi gidan makeken na akwai fili rumfar ajiye motocima kadai ba karamabace wata ga ko ina shifkokine franni gwanin shawa zee ganin yada gidansu ya tsaru da mahbeer sai taji aranta na su Nisha baikai nasuba ni ko nace zee da kinga gidan Nisha bazaki hadashi da nakiba wlh idan kaga yada zee baby ta dawo sai tabaka sha'awa tayi mugun kyau taji gyara cikin da waje ko inanta sheki yakeyi saide maganin da suke bata ya adabeta koda yaushe zuba takeyi har wani kaikayi gabanta yake da nonota shiyasa kwana biyu take azumi ga tunanin rashin jinta jikin Sardauna ya dameta sama da kwana ashirin basu rumgumi junaba basusha yawu ba duk acikin mugun hali suke Sardauna yafita damuwa danma kwana biyu suna waya Dan ya kasa daurewa bayan ta masa rashin kunya da ya huce ya kirata to wannan Karon bata masaba sosai suke shan hira sai sukai kusan Asubah tayi ta zuba masa shagwaba amatsayin yayanta shikuwa ya biye mata to shima abinda yasa kenan tunaninta ya Dan rage masa suna chatt da juna gamuwace basuyi ko sun hadu a parlo idanuta kadai ake gani Nisha ma ta hadu ba karya Sardauna ma saida ya yaba mata tayi ta jin dadi Dan ba laifi yana kula da ita tunda yasan kaddarasa, ce auranta ba mashakurah ba mahbeer ji yake kamar ya, maido yau auransu Dan ya kasance da, zee Dan yau yakai sati yana azumi shakuwarsu kuwa tana nan ghaisha ta Dan barshi suna hira amma zee ba'a, ganin kominta sai idanunta ummi abin. Namata dadi sosai

shirye shirye ya kankama saura kwana uku daurin aure anko masu tsada wajan kala hudu akayi su zee anyi dinkuna na kece raini abin sai Wanda ya gani abokin mijin Salma kanwar Nisha ne ya tsatsara musu dinkuna masu uban tsada haka bangaran mahbeer da Sardauna ma sunyi dinkuna na kece reni tare da su Ahmed da bandar da Hadeem kai wannan aure saide muce Allah kaimu lafiya gaskiya akwai shagali babba, Dan baki har sun fara zowa daga niger

Da misalin karfe biyar na yamma zee baby ce kwance a bedroom tana waya" wlh my dear Allah nayi miki fushi kinki zuwa kiga kayana ko waike kunya Hamm nagode"ayya my dear wlh nima umma ce ta hanani fita amma bari yanzu zanzo dan Allah karkiyi fushi ko har ankai kayan can gidanki? " ba'akaisu ba kizo wlh nayi missing d'inki "ok zanzo yanzu wai angama dinka miki anko kuwa ni nasamu dinkuna na fah salma tace naki sunyi mugun kyau na dinner dariya zee tayi Dan Sam batason zancen tace"kibari zamuyi maganar idan kinzo?" OK bye ta tsinke Kiran dariya ta saki ta mike ta saka doguwar Riga ta saka hijab da niqab ta fesa turare ta fito tana jin jiri dan azumin bugata yakeyi gashi yau tin safe takejin ciwon kai ita daya zata rika zabura saboda mafarkin da tayi jiya wai kar tayi aure tanada auran sarkin Aljanan k'udis bushewa tayi da dariya "Allah mafarkin shirme baiyiba parlon babu kowa su ghaisha da ummi suna part d'in Daddah har hafeeza zaune tayi a parlo tana kollon TV Nisha ta shigo da sallama na Mike da gudu na nufi gunta muka rumgume juna najata muka nufi gun kujerun parlon muka zauna Niqab ta cire mun "wow haka kika zama dariya nayi na maids niqab din nace "kema kinyi kyau wlh tsaf dake amarya yayana dariya tayi" ina ghaisha ne? " suna gun Daddah muje kiga kayan kafin suzo zaki kwana ne? " A,A Yayamu idan yazo zai maidani wani iri zee taji ta kalli Nisha "wlh kibar bari kuna kebewa dashi kibari zansa my heart ya kaiki ba aso amarya da ango suna haduwa "Allah my dear "wlh my dear Karki sake yarda Sardauna ya ganki sai an daura muku aure shigowa yayi da sallama karaf akunnesa abinda zee take fadama Nisha idanu ya zaro Nisha ta sada kanta kusa da ita ya zauna fuskarsa babu wasa ya kamo hannuta yace" Humairah waye ya baki izinin fitowa kin fadamun ne? kika fito ya fada yana murza hannuta cikin wani Dan iskan salo Nisha ta rikice ta dago ta kalleshi wani irin kallo ya watsa mata Wanda taji kibiyar sonsa ta soketa kanta ta sada "Kayi hakuri yaya my dear ce tayi kewata shine nazo mu gaisa zee, baby Allah kadai yasan halin da tashiga ganin abinda Sardauna yakema Nisha kokowa ta shiga da numfashinta har ta daure ta dake ranta ta Mike dan so take ta janye Nisha daga gunsa ta kamo hannu Nisha" My dear tashi muje muyi abinda ya kawoki zata tashi Sardauna yace"babu inda zata tashi mutafi na maidaki gida amaryata Nisha jikinta ya Saki bazata iya masa musuba ya Mike ya kama hannun Nisha yana gyara mata mayafinta  zee baby jirine ya debeta amma haka ta daure ta danne haushin Sardauna ta Kalli Nisha "my dear Ngd yau kin nunamun matsayina kin zabi mijinki Akan yar uwarki fuskarta ta bude tana murmushi tana kallonsu nagode Nisha kije bakomai wlh banji haushinki ba ta fada tana murmushi ta nufi hanyar bedroom dafe da kanta da yake Sara mata Nisha fashewa tayi da kuka "Yayamu Dan Allah kabari naganta kartayi fushi dani wani shegen murmushi ya sakar mata yaja hannuta suka nufi kofa wani. irin gigitaccen ihu zee baby ta Saki sai da parlon ya amsa sai gata timmm ta zube ak'asa tana karkarwa kumfa na zuba bakinta ai baisan lokaci da yasaki hannun Nisha ba yayi kanta da gudu yana kiranta" Zainab.... menene ya sameki dai de lokacin su ghaisha suka shigo da ummi hankalinsu atashe sukabi bayan Sardauna da gudu Nisha Ma kuka ta Saki me ciwo ta bisu da gudu..........✍🏻

*idan na samu dama zaku jini zuwa, yamma*

*💖💖🙍🏻‍♀️ZEE BABY🙍🏻‍♀️💖💖*

MALLAKAR UMMU FAREESA NE

*DAN ALLAH KARKU FITARMUN DA BOOK WAJE*

*👉🏻31*

....Sardauna na isa ya kamata ya rumgumeta yana girgizata "please zainab tashi nine na batamiki rai ko yi hakuri kanwata kinji ya fada ya rumgumeta gam jikinsa jikinta sai karkarwa yake wata irin gigitacciyar dariya tayi saida duk girman parlon ya amsa jikinta na kirrrma murya babu dadin ji sai lokacin ya tuna Ashe aljanai gareta, da Sauri ya dago kansa ya rike kanta da karfi ya fara mata karatu kokowa suka fara suna kwarara ihu "dan Allah ubangidanmu katsaya kaji Karka cucemu wlh bazamu yafeba katsaya munemi masalaha abarmana matarmu sai ku zauna lafiya kai munaji dakai bazamu cucekaba da garaje bakin ya matse ya riketa gam ya Dora bakinsa kunneta da karfin gaske yake mata karatun su ghaisha ne suka iso gabansu suka zube ummi Raiyan na hawaye ta rike mata kafa itama tana tofa mata addu'a ghaisha ma haka Nisha hannuta ta rike tana kuka "saida nace kabari nazo kar tayi fushi gashi nan Aljanuta sun tashi my dear ki yafemun don Allah Sardauna da karfin gaske yake kuga karatun cikin kunne zee sai hadashi suke da Allah yace" to ku fadamun dalilin shiga jikinta" saboda matarmuce kaima muna raga makane amma ka fara kaimu bango kodan kaga

muna tsoronka shine zaka takura mana bakin ya huge"zakuci ubanku wlh koneku zanyi ya maida bakinsa kunne zee ya matse bakinta yada bazaiji duk abinda za suceba yana Mata karatu sai harbe harbe take tana zaro idanu atishwa tayi sau uku tayi hamma hayaki ke fita bakinta da hancinta da yawu mai shegen yauki tayi lamo jikin Sardauna sai bacci har lokacin baibar karatun ba ghaisha tace"Dr sunfa gudu bacci take tashi ka kaita daki sai lokacin ya zare bakinsa akunneta Nisha ya kalla da take famar Rusa kuka"dallah imana shiru ai kamar anyi ruwa an dauke ta hadiye kukan ummi ta kamata ta Mike"Aisha yi hakuri Al'amarin baby sai Addu'a ghaisha tace"Faisal tashi mana mik'ewa yayi da zee jikinsa ya nufi bedroom da ita kwantar da ita yayi saman gado ya goge mata fuskarta ya zauna yana kallonta yanda ta Kara mugun kyau da kwarjina bacci take cikin nutsuwa hannuta ya rike yaji wani irin laushi gaba

dayanta wani ni'imataccen kamshi take karamar yatsarta yasa bakinsa yana tsotsa motsi ta fara tana motsa bakinta"Yayana sakin hannunta yayi ya rankwafo ya tallabo kanta ya k'ura mata idanu "Na'am my zeener sannu ya jikinki kanwata ni wasane nake miki gani yayi bacci take yanaso ya cire mata hijabi ya shaki kamshinta yaga hakan bai dace ba face d'insu ya had'e yana lasar fuskarta habarta ya kamo yana tsotsa ya kamo tafin hannuta yana murzawa ya maida bakinsa saman

karan hancinta yana tsotsa ya Saki ya kamo lips d'inta yana tsotsa idanu ya lumshe yanajin wani mugun dadi na ratsashi ahankali yake kissing dinta cikin nutsuwa da kwarewa harshenta ya lalubo yana tsotsa cikin bacci takejin kamshi Sardauna na baibaye hancinta da irin zakin yawun bakinsa ahankali ta kamo harshansa ta fara tsotsa tasa hannu ta fisgoshi jikinta ta rumgumeshi gam sona tsotsar bakin juna kamar zazu cinye bakin junansu wata irin tsotsa sukewa juna dukansu hawaye ke kwaranya saman fuskarsu sun rumgume juna gam ahankali ya fara zuba mata yawunsa tana hadiya yana tallabe da kanta ya kura mata idanu jiyake kamar yacinyeta sai makaleta yake zuciyarsa na wani irin bugawa bakinsa ya zare anata baki ta b'are zatayi kuka "Sorry my sweeya zeener amshi kisha maybe na ban kwanane ya fada idanunsa na zubar da hawaye fashe masa, tayi da kuka "sorry babyna amshi da sauri ya had'e bakinsu tako cafke tana tsotsa cikin nutsuwa kallonta kawai yakeyi yada take tsotsarsa bakinsa wata irin tsotsa ya fara mata sai shasheka take tana mimmik'ewa sun makale junansu suna shan bakinsu kakaf suka Kari miyau din bakinsu sai nishi suke zare bakinsa yayi ya kirata cikin fizgo Numfashi "My Sweet zeener tashi zamuyi magana ta gaskiya wlh zuciyata takusa bugawa tashi musamu mafita ya fadi yana rumgumeta gam yana tsotsar wuyanta cikin wani mugun shauki idanu ta bude ta kallesa Dan har ga Allah ta dauka mafarki takeyi tanaga zahirina ta fara dukansa "sakeni wlh natsaneka babuni babukai matseta yayi gam"kanwata tsaya muyi magana tambayarki zanyi ki fadamun gaskiya tsakaninki da Allah wlh inada mafita ta kwarara ihu tana rusar kuka Dole ya saketa ransa abace" OK shikenan tunda haka kika zaba Nisha ce da ghaisha suka shigo da gudu face ya hade yace da Nisha "zo muje na kaiki gida ya fice daga dakin ghaisha namasa magana bai tsayaba ya fice gun zee Nisha ta nufa ta rumgumeta tana kuka" Dan Allah kiyafemun wlh

Bazan sake bata miki raiba ghaisha tazo ta zauna bakin gadon ta rumgumosu tana lallashi Dan zee wani irin kukane take mai daci sai daket ghaisha ta lallabata tayi shiru ghaisha ta kalli nisha"maza tashi kije ya maidake gida cikin sanyin jiki ta Mike zee takin ko kallonta abin ya daga mata hankali Dole ta fice ghaisha saida tasa zee tayi wanka da kanta ta shiyarta tsaf cikin abaya tasa hijab ta kamo hannuta suka fito parlo lokacin bakin sun dawo daga part din Daddah gun ummi zee ta nufa rumgumeta tayi Aisata tace"amaryamu bayan auranki tare zamu niger murmushi tayi batace komaiba dariya sauran sukayi suna yaba kyawun zee baby duk da suma ba baya bane buzayene jajur dasu gashi har baya a mota Nisha ta isko Sardauna fuskarsa, murtik tsoronsa ya cika mata zuciya tana shiga ya tashi motar cikin sanyin murya tace"yayamu kayi hakuri idan na batama rai kallonta yayi yaga itafa batada laifi har gidansu akazo akace Ana sonta murmushi ya sakar mata "no Nisha baki batamun ba zainab ma Dan batada Ify ne ba fushi take dakeba kisaki ranki amaryata kinji? ajiyar zuciya ta sabke taji dadi sosai sama sama suke hira har yakawota gida akofar gida ya ajiyeta ta fito ta shiga gida yaja motarsa gudu yake

shararawa sosai saboda an fara kiran sallah yana zauya alwalla yayi ya nufi masallaci, bai fitiba saida akayi sallah isha tare suka fito da mahbeer part d'insu ghaisha suka nufa da sallama suka shigo parlon Daddah tace"wlh Sardauna bakada kirki gida cike da baki dangi amma baka zuwa part Dina sai kaga dama ko dariya yayi ya Saki hannu mahbeer yaje ya rumgumeta"tuba nake uwar gidana dariya suke tuwusai tace"gaskiya muma fushi Muke ismaghi ne suka shigo da Daddy yace"Faisal ja'irin yarone bai taba zuwa niger ba tare zamu kuyi amarci acan sakin Daddah yayi ya nufin gunsu ya rumgume ismaghil"to uncle zanje mahbeer yayi dariya yaje kusan zee ya zauna wacce take jikin ghaisha manne tanabin kowa da idanu Dan ita jima takeyi auran ya fice mata arai fuskarta mahbeer ya kalla cikin tausayawa yace"zeena sannu ya jiki fuska ta yamutsa daket tace da sauki duk abin dake faruwa kan idanun Sardauna tsaki yaja ya nufi kan dining zee mik'ewa tayi daga jikin ghaisha "momy ina zaki "ummi kwanci zanyi "ah sai kinci abunci mahbeer maza jeka bata abunci da Sauri ya Mike ya kama hannuta suka nufi kan dining ya zaunar da ita suna zuwa Sardauna ya Mike ya fasa cin farfesun ya bar gun daket yasamu taci farfesun kazar kadan sai yaga duk ta canza masa to sanin halin mutum mai

jinnu sai hakuri har bedroom ya rakata ta kwanta ya fito ummi sai murmushi takeyi sosai ta yaba da samun sirikin kwarai gabaki dayansu suka nufi kan dining akaci akasha Daddy yau farin ciki yake gasu tare da family Almahadee magawata hira akace cikin farin cikin da anushuwa mahbeer sai yage baki yakeyi  bangaran zee da Sardauna kuwa sunacan kowa zuciyarsa babu dadi ahaka har zee tayi bacci Dan ko ina na jikinta ciwo yake mata mahbeer sai shabiyu ya koma. part d'insu yayi wanka yayi shirin kwanciya amma saida yayi sallah yama zee Addu'ar samun Ify ya kwanta yana Addu'a yaji Ana kecewa da wata irin dariya akowane bangon daki anacewa "wlh gwara ko kayi Addu'a Dan kana bukatarta ko ajikinsa yaja blanket ya shige yana Addu'arsa har bacci ya daukesa bangaran Sardauna sallah yayi  saida ya dauki dogon lokaci sai karfe biyu ya gama yayi Addu'a ya shafa ya Mike ya cire jallabiya yasaka kayan bacci ya Haye saman bed yaja blanket yana juyi alokacin babu abinda yakeso sama da yaji zee baby cikin jikinsa, ya rumgumeta gam yayi bacci wayarsa, ya dauka ya kirata, amma wayar akashe tsaki yaja yayi wurgi da wayar"oh my god haba my kanwata meye na miki da zafi haka, wlh nasan da karna kiraki ne kika kashe wayarki to me yasa, kika zabarmun Nisha idan kinsa bakison hakan wlh babu digon sonta na soyayya sai na yan uwantaka da darajarki taci da kuma yaba hankalinta da nayi tsaki yaja, yana dafe da goshinsa yana juyi har barawon bacci ya kwashesa da mafarkin zee baby,  asuba ta gari

************************************

*Bayan kwana uku*

Yau take juma'a To fah yau take sallah ga angwaye da amare yau take ranar daurin aure Wanda za'a daurasa bayan sallahr juma'a wlh fadar irin taron da yake cikin wannan gida to bata lokacine bikine fa yau ake na kece reni wlh idan kama zee kallo daya bazakaso ka dauke idanunka akantaba  ghaisha da ummi sun yi mata uban gyara da shiri kanwar mijin maijidda yaya Sardauna ce ta cancada mata kunshi da kitson wlh fadin irin kyawun zee bazai faduba gashi ta saki jikinta tabar tunanin Sardauna tun washe garin ranar tayi watsi dashi ta kashe

wayarta, ta maida hankali kan abunda yake gabanta kowa yaga kunshin zee da kitsonta sai ya yaba mata mahabeer da yagani saida ya rike hannuta yayi ta lasar kunshin tana masa dariya bangaran nisha ma ta hadu ba karya itako kanwarta Salma ta mata saboda itama gwanace wajan kitos da kunshi yau bakin Nisha baya rufuwa sai washe shi takeyi dan wani ubansu Dinner ne aka shirya karfe biyar za'a tafi gidansu Nisha fah shima cike yake suna sai kidan kwaryar akeyi Nisha daga cikin sai rawa take ita da kawayanta suna ihu sai zuga nisha suke saboda tayi mutikar yin kyau material din ya amsheta gidan Abdulmutallab yau babu masayar haki shagali fah ake sosai harda masu kidan kwaraya sai casu akeyi ciki na kutsa domin samo labari ghaisha na hango cikin wata uwar shadda gizna blue color sai kai komo takeyi bedroom naga ta nufa tundaga kofa nake jiyo ihu zee na hango tsakiyar su hafeeza dan tayi gayar kawayansu na makaranta ga, zainab itama da kawayanta amma sunada aure zee ce cikin wani dankareren material ruwan toka kanta ba dankwali an mata meke-up ta zuba sinare ajikinta kamar bad a kudiba aka saya wuya da hannu da yatsotsinta tilar hancinta da kasan lebanta duk ta sauya musu zinare wlh idan kaganta zaka zaji babu ta biyunta akyau kidane ke tashi sai cashewa suke maryama matar Nuhu ce tsaya tana koya musu irin rawar da za'ayi gun dinner zee sai dariya takeyi haka ghaisha ta shigo ai maryama kamar ta nutse a k'asa zee dariya take harda rike ciki "Aunty wlh kinban dariya ghaisha ta girgiza kai "maryama zo dama ke nake nema idan kin gama koya musu rawar maijidda tayi dariya "ai aunty muna hanaki kikaki sum sum ta fice zee tace"ummina ina ummi dariya ghaisha tayi " gatacan gun yan kidan kwarya tana dauka awaya dariya zee tayi ghaisha ta fice zainab tace"wow matar yaya wlh ina tsoron daga gun dinner ya wuce dake Brahim estate dariya sukayi ta hararesu ta Mike tana rawa cikin wani shegen Salo da iya taku dan tana mugun son wakar gwanja mata ku taka rawar ganin ido mata kununa farin ciki dariya suke mata itako ko ajikinta dan tanada damuwa dannewa ne takeyi ta wayance dan batasan takamemen damuwarta ba bangaran nisha ma abun ba'a cewa komai itama sunacan suna cashewa ko gajiya rawa batayi da kawayenta abin ya rabu abiyu wasu gidan Umma hauwa wasu gidan ghaisha haka dangi aka rabu ana hidima ko wane gida raguna da saniya aka yanka sai girke girke ake zee Ana hanata saida ta saci jiki ta fito gun yan kidan kwarya ghaisha ce da gudu tazo ta janyeta su hafeeza da intisar 'ya'yan kawu Saminu da su haulat sai casu suke zainab ma da tsohon cikinta sai takawa take ummi Raiyan na musu barin kudi tana dariya

Da misalin karfe daya na hango Sardauna da tawagar abokaninsa Wata d'anyar Shadda gizna ce yasaka milk color wacce tsayawa fadan kudinta bata lokacine wani irin mugun kyaune yayi saide fuskarsa ba walwala Mahabeer ko sai washe baki yake Shaddarsu iri dayace da Sardauna su Ahmed anci uwar kwalliya kace shine angon bandar ma haka Hadeem ma haka yakub ma haka da Najib kanen anguna kai da sauransu wlh kana ganinsu kasan nera tayi kuka bikin kuma na manyan yarane ba karya Sardauna ya zama tamakar tauraro cikinsu sai surutu sukeyi sigarinsa ya kunna ya sha iya shansa Ahmed na masa tsiya wani shegen kallo Sardauna ya watsa masa ya daga masa gira nuhu ne ya ISO yana dariya "to ku tashi muje masallaci angwaye bayan sallah juma'a acan masallacin za'a d'aura auran murmushi Sardauna yayi ya Mike ya rumgume nuhu "Dr kako ji jikinka zafi rau yawa wuta fa amma dan dauriya kake zaune "wlh Babban yaya kaban dariya saikace mace dagajin zazzabi sai na nemi magani mahabeer ya Mike ya rumgume Sardauna yaji zafin "babban yaya wlh kusan kwana nawa na lura bajin

Fadamun meye kike so? " My Sardauna nah ba kaibane kaki bani yawunka nasha ta fada tana Kara sautin kukan"OK to yi shiru bari kukan ji jikinki akwai zafi karkiyi Nisha ta jimu kukan ta saka masa cikin shashekar kuka tace"yo taji mana ni ina ruwana yo haka ake mutum da Dan uwansa ahanashi ya wataya My Sardauna ni banason Nisha haushinta nakeji tanason rabani da Rabin jikina tarine ya sarketa kyakyawa rumguma ya mata"Ya Salam My Babyna yi hakuri kin fiye zafin kishi kalli kinason kashe kanki da kinsan halin da yake ciki akanki yafi naki hakurine yakeyi amsha maza kisha tarin ya tsaya wlh bazan taba bari ki kamu da ciwon zuciya ba ya fada yana fito da harshensa ya tura mata cikin bakinta taji murya Nisha na kiranta makale Sardauna tayi tayi lamo jikinsa tana tsotsar harshensa ko ajikinta shine yayi kokari ya zare harshensa ta makaleshi" Yayana yanzu tafiya zakayi ka barni ta fada cikin kuka mikar da ita yayi tsaye ya jinginata da bango ya mata rumfa da faffadan kirjinshi ya zuba Mata mayatattun idanunsa ya tallabo kanta ya. bude bakinta ya Dora nashi sama yana gogawa ya zuba Mata yawunsa yana wasa dashi da Sauri ta fara lasewa tana hadiyewa maganar Nisha yaji ya zare bakinsa anata ya gyara mata gashinta bakinsa yakai kunnenta cikin tattausan lafazi ya narkar da murya"my Kanwas idan kinason farin cikin Sardauna karki kuskura kiyi kuka ko ki kwana da

damuwa ki Saki ranki bazan taba yardaba ciwo ya kamaki irin na Almahadee ki jure kizama jaruma maza hadiye kukanki kimun dariya ki Saki ranki za'a maida muku auranku kuma idan kinason farin cikina karki sake saka kananun kaya kirika saka manyan kaya kinji my baby yar kanwata ya fada yana sakar mata kiss zee baby tunda ya Dora bakinsa kunnenta ta lumshe idanuwanta tayi lamo saman faffadan kirjinshi ta rikeshi gam tana sauraron amon muryarsa mai dadin gaske har bacci ya kwasheta Dan batasan sauran bayanin da yakeba jin yana lasar kunneta batayi dariya ko ta motsa yasa ya zare bakinsa ya d'ago ya leka fuskarta manyan idanunsa ya zaro ganin baccinta take cikin nutsuwa fuskarta ya shafa"oh my God my zeener bacci kikamun ajikina yanzu ya zan miki gashi banason kiyi kuka ko damuwa tamiki yawa sona ya adabi zuciyarki nasan kina mugun son Sardaunanki wlh Nima ina miki so da kaunar da suka linlinka naki saide abin bakin cikin bazamu malaki junaba ko da akwai auren tsakanimu ni bana noma gonar da wanina ya noma  zan binne sonki cikin zuciyata kema zan miki Addu'a Allah ya cire miki kaunata azuciyarki ya fada yana daukarta cak kamar yar baby ya rumgumeta ya fito da ita direct part d'insu ghaisha ya nufa da ita da sallama ya shigo parlon. duk suna tsaitsaye Ana neman zee Nisha ganin Sardauna rumgume da dear dinta gabanta yayi

mugun faduwa ganin yada ya rumgumota tana manne jikinsa Addu'a ta fara karantawa ganin ya nufi hanyar bedroom Daddy da ghaisha suka nufosa da Sauri"Sardauna meye ya sameta" Daddy lokacin da na fitane na shiga part. din Daddah narika jiyo ihu da kuka ina zuwa naganta ak'asa tana birgima Aljanunta sun tashi wlh daket na sabkesu Nisha ce ta iso hawaye ya wanke mata fuska ta Dora hannuta saman fuskarta ta shafa" my dear Allah baki lafiya muna hira tace bari tazo ta daukomun wayarta naga sabon pic dinta da tayi Ashe tana fita suka bigeta ghaisha tace" momy saida nace ta yafa mayafi takiya Sardauna kaita d'akin ummi Raiyan Daddy yace"wlh ciwon momy ya fara damuna jinnu sun matsa mata jeka ka shinfideta tafiya yayi ghaisha ta rumgume Nisha tana lallashinta"Aisha kiyi hakuri yar uwarki zata warke insha Allah Sardauna bedroom d'in ummi Raiyan ya shiga da ita ya kwantar da ita saman gadon ya zauna yana tofa mata Addu'a duk jikinta ya shafe mata fuskarta motsi ta fara" Yayana Sardauna murmushi ya saki ya matsa baya Dan karta kamoshi har ya gama Addu'ar ya rumguma mata katon pillow tako rumgumeshi gam lullubeta yayi da blanket " I love you my zeener Allah ya ciremana son junanmu tunda basamun junaba zamuyi ba kin haramta gareni rankwafowa yayi ya sakar mata kiss saman lips d'inta da idanunta da hancinta ya Mike ya fice ransa duk abace idanunsa sunyi Ja ummi tace"Dr sannu Allah yama Albarka"kai ummi ai babu komai kanwatace fah Aisha tashi mutafi Daddy sai da safe"Dr namu sannu Allah yayi maka Albarka yabaka abinda kakeso duniya da lahira ghaisha tace"Ameen Abban Sardauna murmushi yayi yaje ya sake musu kiss suka musu sallama suka fice su Daddy ma tashi sukayi kowa ya nemin gun kwanciya dare yayi karfe, goma shadaya na dare, suna fitowa suka shige mota Sardauna

yamata key bakin get ya tsaya yana horn sai ga mai gadi ya fito ya bude musu get Sardauna ya fizgi motar da karfi yaja driving yake acikin nutsuwa ya kalli Nisha da tayi shiru kanta a sade janyota yayi jikinsa"my Neesher yanaji kinyi shiru? rumgumeshi tayi gam tana sabke ajiyar zuciya" sweetheart wlh nadamu da rashin lafiyar my dear tabani tausayi Allah yabata lafiya"Ameen my Neesher karki damu zata warke kinsan fah mai ciki ba'aso tana saka damuwa aranta ki Saki ranki ya fada yana tura hannusa cikin rigarta yana shafo marata shiru tayi ta d'ago tana kallonsa" my Dr kabari" naki na bari wasa nake da babyna shiru tayi ahaka har suka isa gida tana manne jikinsa yana shafa marata horn yai mai gadi ya bude masa get ya shige ciki da motar rumfar motocin ya shiga ya faka ya kashe motar Nisha ta bude ta fito shima ya fito ya rufe motar ya kama hannuta suka nufi sashensu Sardauna ya saka key ya bude suka shiga da sallama ya maida kofar ya murzawa key suna zuwa tsakiyar parlon Nisha ta amshe hannuta ta nufi bedroom dinta"ina jiranki dariyar karfin hali tayi "OK tace ta shige bedroom dinta kayan jikinta ta cire ta shiga wanka agagauce ta shirya cikin kayan bacci Riga da wando gabanta sai faduwa yakeyi Dan tasan bazai mata ta saukiba kofar ta tura ta shigo da sallama har ya gama shirin kwanciya ya had'e cikin kayan bacci ruwan toka masu sulbi yana kwance ta karaso bakin makekan royal bed d'insa hannu ya ware mata"Oyoyo mamar baby Oya zo gun mijinki gabanta na fadu ta isa gunsa ta fada jikinsa ya rumgumeta yana sunsunata ya beka hannu ya kashe wutar d'akin yaja musu blanket

"My Neesher ya naji zuciyarki na bugawa da karfi?"kai my sweetheart babu komai ta fada tana shafar fuskarsa" my Dr inason sajan fuskarka bai bariba ta karasaba ya kame bakinta amma

yana fara tsotsa ya Saki yanajan tsaki itako babu abinda take so sama da bakinsa wani salon ya fara mata tun tana tsoro har ta saki jiki har tafiya tayi tafiya ya shigeta cikin nutsuwa yake kashe arna Nisha yau wani mugun dadi takeji sai sambatu take tana kamkameshi shima kansa yaji ta canza yana Dan jin dadi ba kamar farkon auransu ba shiyasa yake mata yan kananun maganganu yana tambayarta tanajin dadi kai tsaye tace"wlh inaji Ya Faisal shiyasa ya Kara fawa"yana cewa my Nisha kirikamun zantutuka masu dadi amma saboda ya rudata ta kasa, sai nishi take tana ririkeshi Abu kamar wasa har wucin awa daya nisha taji shiru bashida niyar sauka akanta aikuwa ta fara kuka Dan ta gaji tayi release so biyu kuka take wiwi" Ya Faisal nagaji wlh nagaji ka dagani zafi nakeji amma bai sauraretaba Kara fawa ma yayi cacakarta yake bada wasaba saida ya kwashe awa biyu cuf  asamanta yayi release ya  kamkameta dakyau yajima sosai kafin ya mirgina gefe yana sabke numfashi zufa na keto masa ta ko ina Nisha ta

jigata sosai ko motsin kirki batayi sabkowa yayi daga saman gadon yaje ya hada ruwan zafi ya dawo ya dauketa" Nisha raguwa shiru tamasa Dan haushinsa takeji cikin ruwan ya nasata yayi wanka tsarki ya dauro alwalla ya fito tsaki taja tana hawaye ta Mike"jarababbe kawai ina dalili ayita garzar mutu ba dare ba rana haka tayi wanka ta fito lokacin da ta fito yana sallah sai uban kamshi yake jikinta ta goge ta maida kayanta da cire mata ta haye gado tayi kwanciyarta gabanta sai zafi yake mata ga jikinta sai ciwo yake batajima ba baccin walaha ya dauketa Sardauna kuwa sallah yayi bai idarba sai karfe uku na dare yayi Addu'a Allah ya cirewa zee sonsa shi kam yasan sonta ajininsa yake amma yana Rokon Allah ya cire masa sonta sai da yagaji Dan kansa ya Mike ya cire jallabiyar yasa kayan bacci ya hauro saman gadon ya rumgumota yaja musu blanket yana Addu'ar bacci Kara shiga jikinsa tayi ahaka shima bacci ya daukesa da tunanin zee baby azuciyarsa Asubah ta gari,  bangaran mahbeer ya kasa sukuni ko abunci bai ciba magugun da malam ya bashi yayi daki daki bayan ya kammla ya kira Khalisat kuka tayi ta masa yaki tiro ayi maganar auransu daket yasamu tayi shiru ya lallabata har ta hakura suka fara hira soyayya sai tsakiyar dare sukayi sallama ya kwanta bacci Adubah ta gari mahbeer

**********************************

*Bayan kwana biyar*
yau kwana biyar da malam kabiru yaba mahbeer magugunan Alhmdllh mahbeer ya dawo haiyacinsa yanzu dayaga zee hajiyarsa take harbawa khalisar kuwa Tasha cin mutumcin zagi uwa da uba yace mezaiyi da ita ya tsaneta tasa ya saki matarsa da yafi so fiye da komai ai nan khalisat ta fadi ta suma tun shekaran jiya ya dagawa yan gidansu hankali shi wlh bai Saki matarsa ba idanma yaketa to ya mayar da ita Daddy yace bazata komaba sukayi ta zaginsa akan me ya mayar da ita bayanin komai ya musa ya warke ras bashida wata matsala kuma ya tsani khalisat Daddy yace bazata komaba sai sunga dama hardasu kuka yayi zee ma ta daga musu hankali abarta ta koma gidan mijinta Dan abukace take tun ranar da Sardauna yayi kissing dinta ta rasa nutsuwarta namiji take bukata gashi tin ranar bata sake ganin Sardauna ba ko ta kirasa bata samunsa har zazzabi tayi mai zafi ko a hospital yaki yarda ya dubata Nabeel ne ya dubata Yakuma ce ayi taka tsantsa zuciyarta ta fara tabu shiyasa Daddy ya yarda yace abarta ta koma gidanta tunda tanaso bangaran Nisha da Sardauna babu laifi yana bata kulawa

sosai yana nuna mata soyayya saide jarabarsa ta takura mata babu yada ta iya Dole take biye masa idan ta fara jin zafi tayi ta kuka shiko ko ajikinsa saide idan ya gama Tasha tatali ankawo mata mai aiki koda yaushe cikin cin kaza take Sardauna yayi ta mata dariya yana cewa"babyna yasa mamarsa kaudai sai ta fara kuka sai ya lallasheta sa'arta guda bata laulayi,  bangaran mashakurah wlh sai ta baka tausayi ta rame ta jeme cikinta ya fito gashi abukace take da namiji Dole ta hakurata rike bandar Dan yana bata kulawa sosai jiran haihuwa akeyi amusu aure Ahmed da hafeeza wata irin soyayya suke zubawa mai tsayawa azukatu Sardauna ya ganosu burus ne yayi dasu yaga iya gudunsu

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

da misalin karfe 8:00pm na dare Nisha Zaune take a parlo tana tsotsar lemun tsami tana kallon makekiyar TV dake manne abango Sardauna ya fito daga bedroom d'insa yana waya kusanta ya zauna jikinsa ta kwanto" eh wlh Daddy kaina yakemun ciwo tun yamma gashi gabana yafiye faduwa sai Addu'a nakeyi amma bari yanzu zan fito na dubasa insha Allah OK bye sai nazo ya tsinke kiran ya kalli Nisha ya daga mata gira ya Kara matseta" yanzu daga mutum ya fara murzaki zaki fara kuka My Nisha ki daina shan lemon tsami dariya tayi ta rukumkumeshi tana kissing dinsa murmushi yai ya tura hannusa cikin rigarta yana lalubarta yana shafa cikinta lafewa tayi jikinsa"my sweetheart kaidin na dabanne mintsineta yayi dariya tayi"kitsaya naji ya babyna yake" my Dr ina zaka ina zuwa? " no ki zauna yanzu zan dawo mairan karfe ne bayajin dadi zan dubasa kirawo Rabia mai aiki kuyi fira kiss ya mata ya Mike hawaye ya wanke mata fuska ta fara shashekar kuka" Ya Salam tashi dauko hijabi mu tafi mik'ewa tayi da gudu tsawa ya buga mata" Nisha bana hanaki gudu ba kina jijigamun yara cak ta tsaya ta fara tafiya ahankali taje ta dauko hijabin ta fito har ya fice amota ta iskeshi ta bude ta shiga ta rufe yaja tunkafin ya iso mai gadi ya bude masa get yafice ya harbata motar kan titi yana gudu Nisha ta kallesa"my Dr kayi hakuri bazan karaba kai ya daga mata jikinsa ta kwanto ta boye kanta kirjinsa tanajin mugu mugun sonsa da kaunarsa na ratsa zuciyarta matseta yayi gam jikinsa yana tuki sai ni'imataccen kamshinsa take Shaka tana shafar wuyansa har suka iso kofar gidansu yaga motar mahbeer ta fito zee zaune agaba suna magana suna dariya suka fice shiko ya shige,  ciki parking yayi nisha ta janye jikinta ta bude ta fita shima ya fito hannuta ya kama suka nufi part din ghaisha akofar parlo suka hadu da Daddy" yauwa Dr Ka iso muje ka hadu da iyayan rigima mun bashi matarsa harda kuka yamana itama ta damemu da kuka ita mijinta ta keso murmushi Sardauna yayi" nagansu Daddy Allah ya basu zaman lafiya Nisha shiga gunsa momy Daddy yace "muje da ita suma sunacan Nisha cikin kunya ta gaishe da daddy

"Aisha sannu ya karfin jiki muje to gidan daddah suka nufa,  mahbeer ko sai murna yakeyi yau zai angwance tuki yake cikin nutsuwa zee na zuba masa surutu tana kwance jikinsa" my heart ka rage gudu mana ta fada ta rumgumeshi tana dariya juyowa yayi ya mata kiss yana murmushi "wlh my zeena da na rasaki mutuwa zanyi bakinsa ta rufe masa tana kwakwab'e fuska zata masa kuka gangarawa yayi bakin titi yai parking ya janyota jikinsa"yi hakuri wasane nake miki bazan mutuba ya fada yana tura hannusa cikin rigarta yana murza manyan breast dinta narke masa tayi"wayyo my heart inajin dadi jin ta fadi haka ya janye rigar tata yasa hannusa duka biyu yana murzamata sai nishi take tana bangaro masa, kansa ta tallabo tahade bakinsu tana masa

wata irin tsotsa mahbeer ya zauce duk ta rikitashi bakinsa ya zaro ya maida kan breast dinta yana tsotsa bankarewa tayi ta fashe masa da kuka shima kukan ya fara yana tsotsa duk sun haukacewa junansu suna romance bakin titi motace ta kwace tayi kansu  mai babbar motar sai horn yake musu jama'a suna kiran sunan Allah amma Sam basa haiyacinsu Dan har sun cire rigunansu kawai sai ji kake garam motar ta bugi motarso zee tashigi motar Sosai Wanda atake zee numfashin ya dauke
jini bulbulowa daga sharan kanta mahbeer yana cikin jigata saboda karfen da yasokesa aciki ganin zee ahaka ya kwalla Kara yana jijigata"zeena don Allah karki barni bazan rayuba idan babu ke samanta ya fada nan take ya sume jama'a sunyi caa gun Dan motar ta game sai anyi dubara za'a cirosu mai motar hannnu ya Dora akai ya fashe da kuka Dan idan kaga yada motar tayi wlh sai kayi kuka Dan tausayi haka jama'a suka taru Ana kokarin ciro abinda aka samu nadaga jikinsu Dan mutane basa zaton sunyi rai..................✍🏻

*💖💖🙍🏻‍♀️ZEE BABY🙍🏻‍♀️💖💖*

MALLAKAR UMMU FAREESA NE

*DAN ALLAH KARKU FITARMUN DA BOOK WAJE*

*👉🏻41*

....daket jama'a sukafito dasu babu mai motsi acikinsu jini ya bata musu jiki mahbeer harda wani karfe gefen cikinsa da ya cakesa cikin hukuncin Allah sai ga Ahmed yazo wucewa yaga taro jama'a sunacewa akaisu hospital parking yayi ya fito ya nufi wajan ganin su zee ne abun ya tashi hankalin Ahmed arikice yace" don Allah ku kamamun musasu mota motar Ahmed aka sasu harda mai motar ya shiga yana kuka Ahmed yaja da sauri yabar gun gudun kar akirawo yan sanda wayar Sardauna ya kira, lokacin suna hanyar dawowa gidansu ganin Ahmed ya, daga ko magana baiba yace" Dr kaiyi sauri kazo hospital ya kashe Kiran,  yaci GABA da tuki hankalinsa atashe suna zuwa hospital aka taresu aka kawo gadon marasa lafiya aka fito dasu aka kwantar dasu kai tsaye emergency akayi dasu

Ahmed hankalinsa atashe yake Sardauna ya shigo da mota ko parking d'in kirki baiba ya fito Nisha na biye dashi Ahmed ya taresa "Dr kayi sauri kaceto rayuwarsu rike Ahmed Sardauna yayi" suwa ye? " zainab da Mahbeer ai bai tsayaba ya sakeshi yayi ciki da gudu Nisha ta fara kuka" meye ya samesu? " hatsari sukayi kiyi hakuri bari kukan muje ki zauna Sardauna kai tsaye emergency ya shiga jikinsa na tsuma sunaga Dr ya shigo suka dakatar gun mahbeer ya

nufa kallo daya yamasa, idanunsa ya ciko da ruwa ya kalli Dr Nabeel " kuje ku ceto ran matarsa bari ni na dubasa, da kaina bai sauraresu ba ya fara ceto ran mahbeer saida ya kwashe awanin biyu ya dinki masa gefen cikinsa da cinyarsa da

sharan fuskarsa da goshinsa da ya tsage wlh ba mahbeer ba Sardauna ma yau abin tausayine ya hada duk maganin da yasan zaiyi Saurin dawo dashi haiyacinsa da kashe masa zafin ciwanka ya saka masa drip ko ina akumbure yake jikin mahbeer lokacin da ya fito yaga yan gidansu cike akofar dakin hankalinsu atashe ghaisha ta nufoshi" Dr ya zainab take da mahbeer don Allah ka fada mana? cikin dakiya yace" ghaisha da sauki zasu warke basu wani jimuba Nisha tana kuka tace" wlh Daddy sun jimu kallo daya idan mutum ya musu bazai sakeba wani mugun kallo ya watsa mata ta sada kanta Daddy da nuhu da kawu saminu suka hada baki"Dr dan Allah ya suke ciki? " Daddy kuyi hakuri da sauki zasu farfado barima na duba zainab din wajan ummi Raiyan ya nufa tayi tagumi tana zaune" ummi kuyi hakuri

zata farka insha? " Dr babu komai Allah shine mai iko da kowa da kuma komai a lokacin da yaso Allah ya tashi kafadinsu gurin ya bari da sauri dan da sunsan halin da yake ciki sai sun tausaya masa dauriya ce kawai yakeyi gurin zee ya tafi kanta anade yake an dinki mata gefen da kanta ya bugu saboda bata jimuba sosai saide buguwar kanta bakin gadon ya zauna zuciyarsa na bugawa gatanan bata motsi duk na'urorine jikinta saboda buguwar kanta tashi yayi ya kara, duba lafiyarta da kyau cikin dakiya da jarumta yake komai amma ko alamun motsi batayi ba jikinta ya fada yana kuka saida yayi yagaji dan kansa ya fito ya nufi wani room yashiga ya rufe kansa, yayi alwalla ya shimfida darduma ya tayar da sallahr nafila yana nema musu sauki awajan Allah har baisan adadin awanin da ya daukaba saida ya duba agogon hannusa yaga karfe, daya na dare ya Mike ya fito har yanzu yan gidansu ba Wanda ya tafi tausayi suka bashi

yace "Daddy dan Allah kutafi gida insha Allah zasu farka cikin haiyacinsu mamana kuje gida babban yaya kai sai ka tsaya Kawu Saminu yace" wlh babu inda zamu yanzu muka gama musu Addu'a zasu farka nan kusa gun Nisha ya nufa ya kamo hannuta ya nufi Office d'insa da ita"ya saka key ya bude suka shiga saman doguwar kujera ya kwantar da ita" Nisha ki kwanta ki huta kibar kukan yar uwarki zata farka inshn Allah kinji? kai ta daga kiss ya mata agoshi yaje ya dauko wata jibgegiyar rigarsa. ta sanyi ya lulubeta ya zauna kusanta k'ugunsa ta kamo tana kuka kasa-kasa bayanta yake bugawa har tayi shiru tana sabke ajiyar zuciya saida yaji tayi shiru ya Mike ya fice har yanzu

Yan gidansu ko mutum daya bai motsaba kai ya girgiza dan sasun halin da yake ciki wlh sai sun tausaya masa dakiya kawai yakeyi sai lokacin Sardauna yaga Ahmed da mai motar gurunsu ya nufa Ahmed yace"Dr kabi asannu kaima ba lafiyar zuciyace da kaiba karfa kasa, damuwa aranka don Allah kayi tawakali? murmushi Sardauna yayi ya rumgume Ahmed yana buga bayansa" Abokina karka damu nabarwa Allah ikonsa kaikuma ina godiya da samunka aboki nagari nagode nagode" dan Allah kabarmun godiya kaga bawan Allah nan hankalinsa atashe su Daddy sunce ya tafi sun yafe masa, amma yace sai yaga tashin bayin Allah nan sakin Ahmed Sardauna yayi ya isa gun mutumin " kaje kawai babu komai Allah ya kaddara bawa baya wuce

kaddarasa kaje munyafe maka ni ganinka ya fi batamun rai don girman Allah kaje mun yafema ganin yada jikin Sardauna yake tsumane yasa mutumin tsorata wuff ya fice da niyar gobe sai ya dawo zaune sukayi zuciyarsu da alhini har karfe kusan uku da, rabi na dare wlh idan ka kalli bayin Allah nan sai ka tausaya musu na'uran datake jone ce jikin mahbeer ta fara kuka da gudu wata nurse ta fito Kiran Sardauna arikice yayi ciki mahbeer ya farka sai tari yake jini na fita yana Kiran sunan zeena don Allah karki mutu gwara ni Na mutu ke kirayu da gudu Sardauna yayi kansa yana bashi temakon gagawa, su Daddy ana hanasu amma saida suka shigo daket Sardauna ya samu ya daina aman jinin rumgumeshi yayi yana kuka abinda yan gidansu taba ganin Sardauna yayi ba shine ya karyar da zuciyoyin yan gidansu ghaisha k'asa ta zauna

tana kuka, mahbeer yace"Kenan zeena mutuwa tayi shine kukamun Alluran bacci har aka binneta Daddy ne yazo ya rikeshi Sardauna yace"wlh bata mutuba zako rayu tare itama nemanka take tarin ya sarkeshi ya ruko hannu Daddy" Dadyna don Allah kuyafemun nine nayi sanadiyar mutuwar zee da na nace sai an maida mana auranmu da yanzu tana rayuwarta wlh ina sonta banga anfanin zamana aduniya babu zainaba ba don Allah duk Wanda nabatawa ya yafemun gabaki daya kowa yayo kansa, ghaisha, ta ISO ta rumgumeshi tana kuka"mahbeer mun yafema amma wlh zainaba tana raye bata mutuba Sardauna aje ayi dubara akawota da "to ya amsa dan yasan na'ururin da suke jikinta ayanzu bazai yuba aciresu mutikar fata farka tabbas komai zai

iya faruwa da zee rike hannu Sardauna yayi muryashi tayi k'asa" karku takura kanku ni nasan zee ta mutu saboda naga yada kanta yayi zan tardata muci gaba da rayuwarmu nide kuyafemu ya fada yana shakuwa jini na fita daga bakinsa ahankali yake kalmar shahada Daddy yayi saurin rumgumeshi yana fadin" lailaha illallah Muhammadun rasulullah sallalahu alaihi'wa sallam haka mahbeer ya maimaita har sau uku numfashinsa ya tsaya cak idanu Sardauna ya zuba masa mahbeer na damke da hannunsa jikin Sardauna babu inda baya rawa ghaisha ganin mahbeer ya mutu ta tsayar da kukan cak daddy kansa kasa shafema mahbeer idanu yayi Kawu Saminu ne da Nuhu sukayi jarumta kawu ya shafema mahbeer idanu Sardauna wani irin kukane ya kufce masa ya fada jikin mahbeer ya rumgumeshi yana kuka Nuhu ya janye Sardauna ya rumgumeshi Daddy ya kwantar da gawar mahbeer ya Mike tsaye

ummi zubewa tayi asume gabaki daya Sardauna jikinsa kerrrma yake yana wani irin kuka na fitar hankali gabaki daya ghaisha tama kasa motswa daga inda take tana karkarwa azaune ta tsare gawar mahbeer da idanu Daddy ne yayi kan ummi Ahmad akidime yayi waje ya kirawo likita Dan yasan Sardauna babu abinda zai iya ayanzu tare suka shigo da nurse da Dr Nabeel aka fitar da ita domin ceto ranta daddy ya koma gun gawar mahbeer ya tsugunna ya rike hannunsa"mahbeer yanzu ka mutu kenen Allah nagode maka da ka jarabeni ka daukemin yarona mai son yan uwa mai hakuri mabucin dariya mai son nak'asa dashi Allah na amshi jarabawarka da hannu biyu mahbeer Nayafema duniya da lahira khadijah kizo kiyafema d'anki zai tafi tafiya ta har abadan Saminu ya rike Daddy ya Mike tsaye "haba Abdu muyi tawakali da Allah mu karawa nak'asa damu kwarin gwiwa mana Nuhu ya Saki Sardauna yaja hannusa suka zauna "Faisal kayi hakuri kaga ba lafiyar zuciyaba gareka ba kuma kukanka shine yake Kara tada hankalinsu daddy kalli ghaisha halin da take ciki jeka ka bata baki babu Wanda ya isa ya

hana Allah ikonsa duk lokacin da yaso fuskarsa ya goge masa ya ja hannusa suka tafi gun ghaisha Sardauna ya rumgumeta"momy kiyi hakuri kinji rumgume Sardauna tayi ta fashe da kuka "Faisal kaga yayanka yatafi ya barmu ko? Ahmed ne ya amso farin yadin ya kawo daddy tashi yayi ya lulube mahbeer ya dauki waya ya fara kiran yan uwa suna zaune agun sun tisa gawar mahbeer gaba ummi kuwa ba'a samu ta farfadoba sai karfe biyar na asubah tana kuka tana kiran mahbeer da zainaba sun mutu saida aka mata allura barci bayan sallah asubah gabaki dayansu suka dunguma gida har gawar mahbeer zuwa karfe takwas na safe gidansu mahbeer babu masayar tsinke Al'ummmah musulumai sun cika gidan sai koke koke akeyi zainab kanwarsa nan take naguda ta kamata sai hospital batajima ba ta haihu da namiji hadeema ana take yace asa sunan mahbeer yana kuka tamkar ransa zai fita dan bashida abokin da ya wuce mahbeer gashi mijin kanwarsa tana haihuwa ya koma gidansu mahbeer duk inda kake neman tashin hankali to wannan Family wlh sun shiga ga zee bata farkaba Daddy dubi suke itama ta mutu Sardauna boye musu yayi misalin karfe Tara na safe an gama shirya mahbeer za'a kaishi makwancinsa yan uwa gewaye dashi sai Addu'a suke masa ghaisha ta rumgume gawar amma bata kuka"mahbeer halinka nagari yabika na yafema duniya da lahira hafeeza ma rumgume take da gawar tana kuka Nisha ma Najib salma intisar ma tace"Ashe bazan rayu da kaiba nasoka kamar na mutu yaya mahbeer Allah ya jikinka da rahma Sardauna yace" kubamu guru mu daukeshi Ana jiranmu Dan kokarine kawai yakeyi maryama da anty hauwa suka janyen su amma maijidda taki sakin gawar mahbeer tana kuka mai cin rai daket Sardauna ya dauketa cak ya kaita gabansu Daddah suka ririketa su nuhu suka dauke gawar suka fice Sardauna ya rumgume ghaisha" momy idan bakyaso nima ki rasani to kiyi shiru don Allah? " nayi Sardauna nayi shiru kuje ku kaishi gidansa na gaskiya sakinta yayi ya nufi gun ummi Raiyan ya tsugunna gabanta"ummi kiyi gakuri don Allah wlh nima zaku rasani idan Baku bar kukanba" mun bari Faisal tashi katafi mik'ewa yayi ya fice Ana shirin sallahtar gawar

ya bi sahu aka sallahci Dan uwansa hawaye na zuba a idanunsa Ana gamawa akayi masa Addu' aka daukesa sai gidansa na gaskiya wlh fadin irin jama'ar da mahbeer ya samu bazai faduba saide nace Allah yayi masa gafara kawai haka suka kaishi gidansa na gaskiya suka binneshi jama'a kowa yabon halinsa yakeyi yan gun aikinsu ma dayawa sunyi kuka rufe kamfanin akayi akace sai bayan sadakar ukku direban da bikesu tamkar zaiyi hauka kuka yake yana cewa yakashe mutum wuni jama'a sukayi ana shiga ana fita har bayan la'asar har yanzu Sardauna bai sama cikinsa koda ruwaba Nuhu ne ya fahimci hakan daket ya lallabashi ya kawo masa tea ya kurba ciki gun mata ma hakane babu Wanda ya iya sama cikinsa wani Abu har dare bayan sallah isha'i Daddy yace Sardauna ya daure yaje ya dubo zainaba ko da sauran ranta Dole yasa Najib ya tukasa suka tafi yayi mata, dube dube babu wani alamun motsi jikinta haka suka dawo Sardauna sai zubar da hawaye yake Allah kadai yasan halin da yake ciki, Nisha ma bata sukuni abun ya mata yawa tafe kawai take hauwa tana dan kula da ita tsakiyar dare kowa ya nemi guri ya kwanta Sardauna yana saman darduma yana sallah yana kuka saida yaji kafafunsa basu daukansa ya hakura, ya zauna yana ma dan uwansa da zee Addu'a yana kuka, da yagaji nan ya bingire ya kwanta har barawon bacci ya daukesa saboda jiya babu Wanda ya rumtsa Asubah ta gari

**********************************

*Bayan sati guda*

Yau mahbeer yacika sati guda da mutuwa wlh har yanzu idan ka kalli yan gidansu sai ka tausaya musu saboda sunsa mutuwar aransu saide Dole suka fara hakura tunda sunsan bazai dawoba yan niger motoci biyu sukazo bayan sadakar uku suka koma amma minata da tuwasai sunce bazasu ba sai bayan arba'in Sardauna saida akayi sadakar ukku daket ghaisha ta matsa masa, suka koma gidansu saide kullum idan sunzo sai dare suke komawa, yarame sai fari da ya kara ya tara k'asumba Nisha ma tarame dan mutuwar ta shigeta dadinta daya har yau Sardauna bai kusancetaba bangaran zee baby har yau bata farkaba tsawon sati daya hankalinsu ba karamun tashi yayi ba ummi har tagaji da kuka tanaso tace abata ita sutafi saudiya amma ta kasa ganin yada suke nuna damuwarsu akan zainab gashi suna tatalin ummin da kwantar mata hankali duk da suna cikin tashin hankalin mutuwa akullum Sardauna so uku yake zuwa dubo zee tanada rai lokacin farkowarta ne baiba

da misalin karfe biyar na yamma Sardauna na zaune cikin parlon yana kallon tashar Sunnah TV zauwarsu Kenan daga gidansu"Nisha ki kawo mun mana" gani fah yi hakuri Rabia ce take aiki agurin na nuna mata wani abune zama tayi kusansa ta kafa masa cup glass d'in abaki ya kurba yana yamutsa fuska jikinsa ta kwanto" my Dr yi hakuri kasha please kaifa kace na hadoma coffee mai dadi muyi hakuri babu yada zamuyi da hukuncin Allah amsa ya rikayi tana bashi abaki yanasha idanunta sun ciko da hawaye Sardauna ko tunda ta rumgumeshi yaji yana bukatar kusantarta dan satin da yayi tashin hankaline ya kauda masa sha'awarsa amma yanzuma sam bazai wani iya tabuka komaiba bashida kwanciyar hankali mutikar baiga zee baby ta farka ba bayan ya shanye coffeen ya rumgumeta gam yana sabke ajiyar zuciya"Nisha kibar kukan mu amshi kaddara da hannu biyu kara shigewa jikinsa tayi tana buga bayansa itama

alamar lallashi wayar Sardauna ta dauki ringing idanunsa ya bude ya kalli screen d'in wayar yaga Dr Nabeel da sauri cikin rawar jiki ya dauki wayar gabansa na faduwa yayi picking ya kara, akunnensa" hello Dr meya faru? " Dr Sardauna kayi kokari kazo yanzu na'urorin jikin zainaba Faisal Hashim Almahadee sun dauki ruri alamar ta farka ai bai tsaya, saurаren karshen zancanba ya janye Nisha ya zaunar da ita"Nisha natafi hospital sai nadawo key din mota ya dauka, aguje ya fice Nisha hankalinta atashe tana Addu'ar Allah yasa dear dinta ce ta tashi Sardauna yana shiga mota ya figeta da karfin gaske kafin ya ISO mai gadi ya bude masa get ya fice aguje wani irin gudu yakeyi Allah ne ya kawoshi hospital lafiya ko parking bai gama yiba ya bude ya fice aguje ya yashige direct d'akin da zee take mai cike da na'urori ya nufa har likitoci sunyi tsaye kanta, yana zuwa suka matsa gefe kowa ya fice dubata ya fara ko minti uku baiba ta fara motsi tana fizge fizge cikin farin ciki Sardauna ya riketa gam yana kuka "Zainab ina mutikar farin ciki da farkawarki kanwata yau tsawon sati gudu banaci bana sha saboda rashin Abu biyu masu mahimmanci arayuwa sosai yake kukan farin ciki ya matseta jikinsa har ta daina fizge fizgen amma idanunta arufe hawaye yana kwaranya saman fuskarsa ya zuba mata manyan idanunsa cike da tausayinta ya zauna ya cire mata na'ururin ya rumgumeta gam ya kirata"zainab tashi bude idanunki kinji ahankali ta bude idanunta ta sabkesu akan Sardauna tayi masa kuri da idanu murmushi ya sakar mata hawaye fuskarsa suna zuba saman fuskarta "

zainab sannu ya jikinki da idanu ta kafesa ko giftawa batayi "my kanwas bazaki mun maganaba ya fada yana langwabe kai yana sakar mata murmushi ga hawaye na kwaranya daga idanunsa duk dan ya saka mata kwarin gwiwa murmushi ta sakar masa ta dora hannuta saman fuskarsa ta shafo hawayen ta langwabar da kai ahankali kamar mai koyon magana tace" my kanwas bazaki mun maganaba ta fada tana sakin murmushi kara rumgumeta yayi hancinta yaja" banson raini ni sa'an kine murmushi ta saki ta beka hannuta saman dogon hancinsa ta ja tace" banson raini ni sa'ankine idanu ya zaro" my kanwas ni ko itama tazaro manyan idanunta ta tsaresa da kallo tace "my kanwas niko gaban Sardauna ne yayi wani irin faduwa da Sauri ya janyeta daga jikinsa ya Mike tsaye ya kwantar da ita ya jona mata wata na'ura akanta ya nufi gun wata na'ura da gudu dan ya kunnata ya binciki zee tashi tayi ta fashe da kuka tana kokarin cire na'urorin jikinta da ya jona mata dan tabishi arikice ya nufo gunta "zainab tsaya ganinan.............. ✍🏻

💃Ladingo Yar ilu

*💖💖👩🏻‍🦱ZEE BABY👩🏻‍🦱💖💖*

MALLAKAR UMMU FAREESA NE

*DAN ALLAH KARKU FITARMUN DA BOOK WAJE*

*Allah Nagode maka da yan uwa musulmai da suka sanya bakunasu masu Albarka wajan yin Addu'a har Allah ya fitomun da fareesa lokacin da bamuda tsammani hakika Allah abin godiya yan grp dinan ina godiya sosai da gudun muwar da kuka bada wajan yin Addu'a*

*👉🏻42*

....cikin sassarfa ya karaso gareta ya riketa ya mannata jikinsa yana buga bayanta" zainab ki tsaya mana kukan me kike babu inda zani shiru tayi ta kwanta kirjinshi ta d'ago da kanta tana kallonsa murmushi ya sakar mata" my kanwas murmushi ta sakar masa hawaye nabin kumcinta cikin sanyin murya tace"my kanwas lumsassun idanunsa ya zuba mata zuciyarsa na wata irin

bugawa ya tallabo kanta hawaye yacika masa idanu ya lakuto. hawayen fuskarta ya lasa" my zainab meyasa zakimun haka me haka yake nufi menene ya faru dake please idan wasane kike ki dainamun kinji murmushi ta Saki ta zuba masa manyan idanunta ta beka hannuta ta shafo hawayen fuskarsa ta lashe ta rike fuskarsa ta maimaita abunda ya fada mata da sauri ya Mike ya cire mata na'uran da ya jona mata ya zaunar da ita ya juya ya nufi gun wata na'ura aikuwa ta fashe da kuka da Sauri ya dawo ya ware mata hannunwasa tazo gareshi Sam batasan

hakanba Dole yazo ya Sanya hawansa ya dauketa kamar baby ya rungumeta " to yi shiru kallonsa take tana shashekar kuka tace"my Kanwas" Na'am my Kanwas please kimun rai kibar kukan ahaka tana jikinsa ya nufi gun Na'uran ya kunna ya dawo bakin gadon ya kwantar da ita harzata fara kuka taga ya zauna tayi shiru jona mata Na'urorin wayarsa ya dauka ya kira Daddy bugo daya ya daga da sallama "assalamu alaikum Dr Allah yasa muji alkhairi"Daddy" please kuzo yanzu hospital harda momyna da ummi duk kuzo kuga hukuncin Allah ya sake sabka akanmu Allah yasake Dora mana wata jarabtar arikice daddy yace" Sardauna meke faruwane? " Daddy sai kunzo kitt ya tsinke kiran ya kwantar da zee da ta tsareshi da idanu ya shiga duba lafiyarta, su Daddy sunzo suna waje saida ya kwashe awa daya cur ko ina na jikinsa rawa yakeyi sai sunayen Allah yake kira ya cire abun da ya jona akunnesa dabas ya zauna ya cire mata na'uran ya zuba mata idanu kukanma ya kasa Nabeel ne ya kirasa awaya su Daddy sun matsu suga zainab yace ya kawosu, kofar aka turo da sallama ya amsa ghaisha da ummi da gudu sukayi gun zee ai tana daga kwance taga mutane na nufota akidime ta Mike zaune ta fashe da kuka ta fada jikin Sardauna tana karkarwa ta boye kanta acikin kirjinshi

tana kiransa" my kanwas rungumeta yayi yana buga bayanta ya Kara boyeta jikinsa sosai tamkar cinyeta zasuyi hankalinsa atashe yace" baby yi shiru bari kukan lafewa tayi jikinsa ta rikeshi gam tayi shiru ta lumshe idanunta ya kalli su daddy " wlh Daddy akwai babbar Matsala batasan kowa ba fah ayanzu sai ni sabode tayi losing memory ta mance kowa da komai nata na baya sai Wanda za'a koya mata yanzu da ita da Wanda aka Haifa yau basuda banbanci Nima abinda yasa ta yarda dani saboda tana bude idanunta nita fara gani ita atunaninta babu kowa cikin duniya sai mu biyu daddy yace "innahlillahi wa'innailaihi Raji'un Allah mun gode maka kuma mun amshi jarabawar da kake bamu ummi Raiyan fashewa tayi da kuka ghaisha ta rungumeta"kiyi hakuri Raiyan zata samu sauki da yarda Allah kinsan bawa baya wuce kaddarasa Daddy yace"Raiyan don Allah kiyi hakuri zata warke insha Allah daddy yazo bakin gadon ya zauna "Dr yanzu yaya za'ayi fitar da ita za'ayi k'asar waje ko yayane?" Daddy zata warke insha Allah akwai maganin da zan dorata akai da yarda Allah lokacin da yaso zata dawo haiyacinta koda yaushene babu yau babu gobe ghaisha taja hannun ummi Raiyan ta zaunar da ita saman kujera ta nufi gun Sardauna ta dafa kafadunsa"Dr Sardauna yanzu ya zamuyi momy ta saba damu ta yarda murika koya mata abubuwa? Daddy yace tashin hankalin kenan, ai

Sardauna ya furzar da iskar bakinsa ya kalli zainab da tayi luf ajikinsa idanunta arufe ta rikeshi gam kamar zai gudu murmushin karfin hali yayi"Daddy muje gida yanzu sai nasamu nayi Mata yan dabaru ta yarda da ummi saboda ta Rika koya Mata abubuwa idan yaso zan kasance ina bata abunci da magani mu dage dayi mata Addu'a zata warke Dr Nabeel yace" Dr ayanzu yarinyarnan bazata iya rayuwa da kowaba sai dakai saboda kaika dai take gani mutum Dan

uwanta Sardauna ya kalli Dr Nabeel "Dr kaje ka dubo mun irin magugunan da ya dace mu dorata akai ka kawomun kai Nabeel ya d'aga ya fice ghaisha kukan tausayin zeey ne ya kufce mata Sardauna yace"momy kiyi hakuri Adfu'a zaku mata ba kuka ba janyeta Sardauna yayi daga jikinsa ta bude idanunta ta saka masa kuka"baby tare zamu yi hakuri sabkota yayi daga saman gadon ya shidota k'asa ya rike hannuta boyewa tayi abayansa tana rike da rigarsa daddy yace"Allahu Akbar

Allah ya baki lafiya Sardauna yace"Amin ya kwashe wayoyinsa ya kalli iyayan nasa" Daddy mutafi gida asamu tayi wanka taci abunci mik'ewa sukayi Sardauna yana rike da hannuta ya rigasu fita waje zainab na rike da rigarsa har suka fito yana jiran Nabeel kafarta ya kalla ba takalmi ya cire na kafarsa " baby bari nasamiki nawa sakarmun Riga idanu ta zuba masa dan bata gane me yake fadiba ahankali ya cire hannunta daga rigarsa ya sunkuya gabanta ya kamo hannuta ya dora akafadarsa ta rike tana dariya ya kamo santaleliyar kafarta fara tas tamkar ta jarirai dan taushi ya saka mata takalminsa sun mata yawa sosai murmushi yayi ya Mike tsaye ya dagota dariya tayi ta fada saman faffadan kirjinshi tace"my kanwas? rungumeta yayi"Na'am my kanwas kallonsa take tana murmushi shima kallonta yake baima San iyayansu sun fito ba da kallo suka bisu daddy ya jinjina kansa yanajin dadin yada Sardauna yake kula da zeey Dr Nabeel ne ya ISO

da leda ya hado Wanda suka samu dafa kafadar Sardauna yai "Dr gasu kallon Nabeel yayi ya beka hannu ya amshi maganin"OK zan duba idan mun isa gida thanks Dr murmushi Nabeel yayi" ai munatare uban gidanmu kai Sardauna ya girgiza ya kalli daddy" my dady mu tafi ya janye zainab ya kama hannunta ummi Raiyan hawaye ya cika mata idanu yau gata ga zainaba amma batasan taba Sardauna yace" dady kuje gamunan zansa takalmi a Office "to sai kunzo Dr hannuta yaja suka nufi Office d'insa ya ciro makullai ya

bude yana rike da hannunta suka shiga idanu take zarowa tana kallon ko ina na Office d'in sakin hannuta yayi yaje yasa takalmi da gudu ta biyoshi ta rungumeshi ta baya tace "my kanwas" Ya Salam ya fada yana juyo da ita gabansa ya rike kafadunta ya zuba mata tsumammun idanunsa"baby babu inda zani takalmi zansa kai ta langwabe tana turo baki sakinta yayi ya kama hannunta sukaje yasa, takalmin ya riko hannuta suka fito ya rufe Office d'in suka fito tana rike dashi gam har gurin mota ya bude ya zaunar da ita agaba ya rufe da ya zagaya ya shiga idanunta har sun tara kwalla yana zama ta kifa kanta saman cinyarsa ta fashe da kuka tana kiransa"my kanwas"Ya

Allah gani gareka baby ya zanyi Dole fah zamu rabu tunda ba guri dayaba zamu rinka kwana dake ba please ki daure kisaba da rashina ah irin wannan lokacin jikinsa ya janyota yana bubbuga bayanta yakai bakinsa kunnenta" yi shiru baby nine nataba Habibty shiru bazan sake barinki ba ina tare dake baccine zai rika rabamu lafewa tayi jikinsa tanajin dadin maganar da yake mata akunnenta ta lumshe idanunta ta kamo hannunsa ta rike cikin nata gam jin tayi shiru yayi murmushi ya janye bakinsa ya gyara mata kwanciya jikinsa ya tashi motar ya nufo bakin get horn yai aka bude masa get ya fice ana ta daga masa hannu driving yake cikin nutsuwa zuciyarsa babu dadi damuwa tayi masa yawa ga zainab cikin halin da take ayanzu tana bukatar

kulawarsa hannusa da ta rike janye  ya dora saman kanta ya shafi gashinta" my baby kanwas kara shigewa jikinsa ta d'ago da kanta tana lumshe masa idanu muryata can k'asa tace"my baby kanwas kallota yayi ya daga mata
gira ya maida hankalinsa kan driving ta maida kanta kirjinshi ta lumshe idanunta Nisha ta kirasa,har sau biyu bai dagaba ahaka har suka ISO gida horn yayi aka bude masa get ya shige da motar nan tskiyar harabar gidan yai parking ya kashe motar,

ya dagota"My Baby Kanwas Oya mushiga ciki murmushi tayi ta dora hannunta saman dogon karan hancinsa tanaja kai ya girgiza ya janyeta jikinsa ya bude motar ya fito da ita shima ya fito ya zagayo ya kama hannuta da ido takebin gidan har suka shiga parlon da sallama hafeeza ta taresu da gudu zata riko zee tayi tsale ta makale Sardauna  tana ihu. janyeta yayi ya nufi gun ummi ya zauna zee na daga gefe tana makale dashi sai wani irin kallo takema su Najib da su minata da Tuwusai Sardauna yace" ummi kuje ki gwada mata wanka da sallah da sauran abubuwa agyara mata gashinta kufito ina jiranku na bata abunci da magani sai natafi mik'ewa ummi tayi Sardauna ya mikar da zeey tsaye"baby kuje agyaraki tsaresa tayi da idanu tsaye ya Mike ya kama hannunta yajata har kofar d'aki yaba ummi ita fur taki tafiya ta fara kuka daurewa yayi ya had'e fuska ya daka mata tsawa wuce maza ku tafi nace cikin rawar jiki ta labe bayan ummi tana kiransa"my baby kanwas kai ya kauda"ummi kuje ki nuna mata ya fada yana juyawa ya

 dawo kan kujera ya zauna kusan ghaisha ya kwantar da kansa kafadarta ya lumshe idanunsa zee ko Dole tabi ummi suka shiga da ta rike mata hannu fizgewa tayi suna shiga ta shiga bathroom ta hada ruwan zafi tazo tajata tana tirjewa harda kuka tana Kiran my kanwas haka tajata ummin kanta hawaye take daket ta cire mata kayan jikinta ta nasata cikin ruwan gumin tana zuba mata ruwan har kanta da kanta tayi mata wanka har dukanta take amma saida ta wanke tas har gashinta bayan ta gama mata ummi ta tube ta kunna shower ta dauki soso da sabulu tana wanka zee ta fito itama ta tsaya gaban shower ta amshi soson tayi duk yada ummi tayi tana murmushi towel ummi ta d'aura itama ta d'aura ummi tayi Alwalla zee ma tayi suka fito tana karda gashinta tana dariya gaban dressing mirror ta janyota ta tsane mata gashinta ta shafa mata man gashi ta dauré mata da Ribbon yada ummin tayi abaya mai kyau ummi ta dauko mata ta bata ummi ta dauko tasaka itama ta saka tayane mata kanta da mayafin abayar

Darduma ta shimfida itama zee tazo ta tsaya gaban ummin tana kallon tana turo baki tace"my kanwas ta fada tana nuna kofar daki janyota tayi suka kalli alkiblah ummin ta tayar da kabarar sallah duk abinda ummin tayi cikin hukuncin Allah shi zee takeyi sukayi sallah isha'i bangaran Sardauna ghaisha ta shafi kansa"Auta kayi hakuri kafara cin abunci ansan mutuwa da ciwo amma babu yada muka iya daddy yace"Faisal ka dauré muyi ta wakali mu amshi kaddara kaga yada Allah ya sake jarabamu ta fannin zainab minata ta share hawaye tace"wlh ina tausayinta sosai baiwar Allah sai abinda aka koya mata Sardauna jinsu kawai yake dan basu fishi shiga damuwaba dauriya yake ga rashin d'an uwansa na ragargazar zuciyarsa ghaisha ya kalla"momyna kanshi ta kuma shafawa"Na'am Autana me kakeso? " babu komai ya fada yana murmushin karfin hali" zakasha coffee?  su ummi ne suka fito zee tasha abaya mai kyau da mayafi da gudu tayi kan Sardauna fuska ya had'e ganin yada yayi yasa ta karasa anutse ta

zauna kusansa tana kallonsa ta matsa ta kwantar da kanta kafadarsa"my baby kanwas daddy kallonsu kawai yakeyi janyeta yayi ya Mike ya kama hannuta ya dauki ledar maganin

ya nufi kan dining.kujera yaja ya zaunar da ita ya dauki plate ya zuba mata abunci jalof d'in shinkaface taji busashen kifi shi ba ciba yake amma Dole ya zuba ya zauna ya dauki spoon ya ya tsakuro yakai bakinsa murmushi tayi ta dauki spoon d'in ta tsakuri abuncin takai bakinta tana kallonsa kai ya daga mata" Oya baby ci sake daukowa tayi tanaci ganin tanaci ya ajiye spoon din hannusa itama ta ajiyewa tai" baby kici mana kafada ta makale tana kallonsa dauka yayi ya tsakuro yana bata da kansa tako amsa tanaci ta matsa ta kwanta jikinsa ahaka ya bata abuncin har ta koshi ya bude robar ruwa ya dago kanta ya kafa mata robar ta rika sha saida yaga ta dan sha mai yawa ya barta ledar maganin ya bude ya duduba ya b'aballosu ya tallabo kanta ya zuba mata cikin baki ya dauki robar ruwan ya kafa mata abaki tasha saida ya tabbatar ta shanye ya ajiye ya rungumeta yana shafa kanta sanin maganin yanzu zai fara aiki don bayaso tayi kuka idan zai tafi d'ago da kanta tayi tana kallonsa hannuta saman dogon hancinsa tana Ja tana murmushi gira ya daga mata yana hura mata iskar bakinsa yana shafa lallausan gashinta suna kallon junansu idanu ta lumshe yada yake hura mata iskar bakinsa ta kara rikeshi gam. ganin alamun bacci sun fara baiyana ya mikar da ita ya dauki ledar maganin ya riko hannuta sai lumshewa take ya ratso ta parlon suka shige dakin ummi ya kwantar da ita ya zauna yana shafa kanta kin kwanciya tayi ta tashi ta kwanta cinyarsa barinta yayi yana buga bayanta ko 5 minute batayi ba tayi bacci ya kwantar da ita ya rankwafa ya sakar mata kiss saman lips d'inta da

goshinta ya shafi fuskarta"my zeener da sonki zan mutu wlh ina mugu mugun sonki da kaunarki amma babu damar zama dake tabbas nasan sai sonki ya kasheni zuwa GABA zuciyata inada yakinin zata buga akanki nayi miki alkawalin tsayawa na kula da rayuwarki har Allah ya baki Ify ki warke na zaba miki miji nagari ki aura rungumeta yayi yana wani irin sabke ajiyar zuciya"my zainba i love you kece bugun numfashina ina sonki sonki kasheni zaiyi nan GABA kadan sosai ya rungumeta da karfi yana sabke Numfashi da karfi saida ta motsa tana kiran "my kanwas tana rungumeshi "Na'am bugun numfashina janye jikinsa yayi ya tofa mata Addu'a yaja blanket ya lulubeta
Ya Mike ya fice daga d'akin ya fito parlo Daddy yace "Allah ya biyaka Sardauna yace"Ameen daddy yayima iyayansa sallama ya tafi hafeeza ta Mike ta nufi dakin tana hawaye tuwusai tace"bawan Allah wlh dauriya yake yaron yanada damuwa ghaisha ta share hawaye tace"ai Dole rabuwa da dan uwa rabuwa ta har abadan ga el uwasa cikin mawuyacin hali ummi tace "khadijah hakuri zamuyi mu amshi kaddara daddy yace" mutumin da Allah baya jarabarsa ai ba mutum bane yayi kuka da kansa minata tace" niko Abdulmutallab inada magana amma bari naga Daddah tukun da mai ran karfe? kai ya jinjina" to Allah ya kaimu goben saboda dare yayi kowa ya Mike ya nemi makwancinsa ummi tana shiga tayi shirin kwanciya kafin karfe biyu ta tashi sallah ta kalli hafeeza da ta rungume zainab hawaye ya bushe kan fuskarta har bacci ya dauketa saman gadon ta hauro ta kwanta gefen guda ta rungume zee tana shafa kanta tana tofa mata Addu'a" hafeeza yau jikin el uwa akayi bacci Allah sarki ta fada tana goge hawaye tana tunanin yaranta da iyayanta kullum burinta mahaifinta da mahaifiyarta su dawo gareta da 'ya'yanta ahaka har bacci ya dauketa Asubah ta gari,

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Sardauna lokacin da ya isa gida Nisha tana parlo tana jiransa hankalinta atashe sai sunturi take ta kasa, zaune takasa tsaye ta hada cikin kayan bacci farare tas Riga da wando knocking taji anyi da gudu nufi kofar ta murza key ta bude yana sayo kafa ta fada jikinsa ta fashe da kuka ta rungumeshi"my heartbeat ina kashiga ina kiranka baka dauka rungumeta yai yana buga bayanta yakai bakinsa kunnenta"My Neesher Sorry ki yafemun naga kiranki banida nutsuwane yi shiru bari kuka my Neesher ina cikin koshin Ify kinji matata shiru tayi ta kara shiga jikinsa tana sabke ajiyar zuciya daukarta yayi cak" muje ki kwanta ya babyna? fuskarsa ta shafa ta sakar masa kiss " my Dr inajin sonka kamar zai kasheni ta fada tana lasar fuskarsa "no maman babyna muna tare insha Allah inason zama dake ya fada yana shiga bedroom d'insa da ita saman makeken royal bed d'insa ya zaunar da ita ya lakaci hancinta"Nessher Dr kinci kaza ko naje na kawo miki? " naci sai da safe "gud ya fada yana cire kayansa bathroom ya shiga ya santalo wanka ya fito daure da towel yana goge jikinsa ya murza maiyuka masu kamshi Nisha ta dauko masa kayan bacci masu kyau ta saka masa yana kallonta bayan ta saka masa ta dauko turarensa mai masifar kamshi ta fesa masa" thanks my Neesher murmushi tayi kwanciya sukayi ya kashe wutar dakin ya janyota jikinsa ya lulubesu ya dora hannusa saman cikinta yana shafawa" my Dr? " my Neesher Oya muyi bacci ya fada yana kara shigar da ita jikinsa dan sam bashida nutsuwar da zai iya Saduwa da ita lamo tayi jikinsa hannunta saman fuskara tana shafawa" Dr ina sonka sosai kanta ya tallabo ya sakar mata kiss ya lalubo bakinta yana tsotsa yana shashafata jikinta ta sakar masa tana lumlumshewa har ya rikitata bacci ya dauketa bakinsa ya zare anata ya rumgumeta yana tofesu da Addu'a bai jimaba bacci shima ya daukesa ransa babu dadi sam baya cikin kwanciyar hankali jarumata kawai yake saboda shi Mutumne mai dakiya da tawakali Asubah ta gari Sardauna and Nisha............✍🏻

*Bazan gaji da Mika muku godiyata ba bisa irin gudumuwar da kuka bada wajan yin Addu'a akan batan Fareesa har Allah yaji kanmu ya fito da ita lokacin da muka cire rai da samunta kwana da yini har yanzu kukan farin ciki da tausayin yarinyata nakeyi Allah nagode maka suko Allah ya Toni asirinsu😭😭😭😭😭😭*

*💖💖🙍🏻‍♀️ZEE BABY🙍🏻‍♀️💖💖*

MALLAKAR UMMU FAREESA NE

*DAN ALLAH KARKU FITARMUN DA BOOK WAJE*

*👉🏻43*

....karfe hudu daidai na Asubah Sardauna ya farka idanu ya bude ahankali bakinsa dauke da Addu'a ya kalli Nisha da suke manne da juna tana sharara barci hannunsa ya Dora saman cikinta yana shafawa zuwa k'asan marata yana murza mata ahankali yana lumshe idanu motsi ta fara da Sauri ya janye hannunsa dan kar ya tasheta ya janyeta daga jikinsa ya lulubeta ya sabko daga gadon ya shiga bathroom shower ya sakarma Kansa ya dauro Alwalla ya fito daure da towel yana goge jikinsa ya bude wardrobe ya ciro jallabiya ya saka ya fesa turare ya shimfida Darduma ya kalli Alkibla ya tayar da sallah Raka'atanin Fajri bayan ya gama ya shiga kwararowa Dan uawansa Addu'a yana kuka dan mutuwar Mahbeer ta tsaya masa arai yajima yana masa Addu'a kafin ya shiga yima Zeey Allah yabata Ify cikin gagawa bayan ya gama mata Addu'a ya shiga karatun Alqura'ani mai girma bai bariba saida yaji masallaci Ana shirin tayar da sallah ya rufe Qura'an din ya Mike gun Nisha ya nufa ya janye blanket din ya shafi fuskarta"maman baby tashi kiyi sallah idanu ta bude gira ya daga mata

ya fice da kallo ta bishi har ya fice sabkowa tayi ta shiga bathroom ta dauro Alwalla ta fito ta duba cikin wardrobe d'in Sardauna ta samu Abayarta guda aciki ta cire kayan baccin ta saka Abayar ta yane kanta da mayafi ta hau darduma ta tayar da sallah, bayan ta gama tama Dan uwanta Addu'a Allah ya jikinsa ya masa rahma da zee Allah ya bata lafiya yasa ta farfado cikin koshin lafiya ta shafa fatiha ta Mike ta cire Abayar ta maida kayan baccin ta fesa turaren Sardauna ta haye saman makeken royal bed d'insa tayi kwance sai lumshe idanu takeyi Dan tana bukatar mijinta kusan kwana Tara basu kwantaba duk da tanacin wuya ahannunsa yau bukace take tana cikin tunaninsa ya shigo ya murwa kofar key ya cire jalabiyar ya ciro wasu kayan baccin ya saka dan kyankyami garesa bazai iya maida Wanda ya kwana dasuba saman bed d'in ya hauro ya kwanta ganin Nisha idanunta rufe zatonsa bacci takeyi jikinta ya matsa yaja musu blanket dan baccin Sam bai isheshiba yanaso ya tashi karfe takwas yaje ya dubo zee baby Nisha

